[10/02, 9:34 am] Abue Saleh: BOOK 3

2

........Yanda duk suka zuba masa idanu zai tabbatar maka da ƙagararsu na son jin yace wani abu. Shima ya fahimci zalamar tasu, dan haka kai tsaye ya furta, “Imran bama Dabo yay tracking number ɗin nan?”.

Cikin bin umarni ya amsa da. “Okay”.

Babu ɓata lokaci Dabo ya fidda laptop ɗinsa a jakarta, dan da abinsa yazo. Faro ya miƙa masa wayar. Karo na farko Dada ya miƙe yana kai-kawo a falon hannayensa duk goye a bayansa. Jikin window ya ƙarasa ya tsaya. Yanda ya zubama compound ɗin gidan idanu ya saka Yusuf miƙewa shima ya nufi inda yake hango coffee maker. Sai da ya duba duk coffee powder ɗin dake wajen sannan ya haɗa wanda yasan boss na sha a da, duk da bai sani ba ko ya canja a yanzu. Amma dai ya haɗa ya jira har coffee maker ɗin ta gama matso masa shi sannan ya ɗauka. Koda ya miƙa masa cike da girmamawa sai Dada ya murmusa. A hankali ya furta, “You’re the best”.

Yusuf yay murmushi shima har haƙoransa na bayyana. Cikin ƙara sirinar da kai ya ce, “Yace thanks you Boss”. Daga haka yabar wajen, shi kuma ya fara shan coffee ɗin yana maida hankalinsa ga wajen dai hannunsa ɗaya a aljihu.

“An sauke layin akan waya gaba ɗaya fa. Sannan an goge duk wani information a kansa, tare da hanashi aiki na har abada.”

Gaba ɗaya fuskokinsu ya canja daga sauraren Dabo mai maganar. Amma shi Dada a mamakinsu murmurshi ma yake yi. Dan a hankali ya tako ya dawo inda suke, ya zauna a inda ya tashi yana ɗora ƙafa ɗaya kan ɗaya. Kamar bazai ce komai ba tsahon minti guda yana ta shan coffee ɗinsa. Ganin yanda a yanzu ma suka zuba masa idanun ya sashi sake murmusawa, sannan ya furta, “Wannan ba aikin jahilai bane. Idan lissafi na yayi dai-dai sun ɗauke ta ne dan karkata hankalinmu a kanta kawai su sami yin abinda suke so, Imran, Faro ku janye sojojin ku na ƙofar da sukace su sakar min matata”.

Imran ya zaro idanu saboda kalmar (Matata) ɗin yana gimtse dariya, hakama Faro. Su Dabo kam sun girgiza ne kawai ta ɓangaren aiki duk da sun san Nimrah tun tana ficiciyarta, sai dai batun aure basu san da shi ba, ba kuma su fahimci furucin boss ɗin nasu ba a yanzu. Cikin kasa haƙuri Imran ya ce, “Lissafin ka dai-dai ne. Amma yanke wannan hukuncin duka akwai ruɗani.”

Caraf Faro ya karɓe da, “Tabbas akwai ruɗani Imran, dan kuwa hakan na nufin zasu aikata abinda suka shirya a wannan yankin, sannan ba lallai idan sun sami biyan buƙata su saketa ba, ko kuma su cutar da ita kafin su saketa. Mutanen nan fa sun wuce duk yanda muke zato da tsammani Boss, ni nafi gane kawai mu farmake su, mu amso ta wlhy”.

Dada da kamar baima jin abinda suke faɗa ya wani lumshe idanunsa ya sake buɗewa. Sai kuma ya taɓe baki kaɗan. Hankalinsa kwance ya furta, “Daga lokacin da lissafi ya zama RUƊANI ko mabiyan addini kan kasance a rikice ne. Dan zasu gagara gane waya kamata su bautamawa? Sai dai abu ɗaya tak da zasu nutsu da shi, mafitar mai sauƙi ce. Bayan ANNABIN ƙarshe UBANGIJI bai sake turo wani MANZO ba, kenan duk wanda zai faɗa maka wanene UBANGIJINKA zai koyar dakai bin ALLAH ne da koyarwar MANZON ALLAH ANNABI MUHAMMAD (S.A.W). UBANGIJI ya halicci abubuwa guda biyu dake bama duniya hasken da har idanun mu ke banbance wanne muke ciki. Hasken RANA, dA hasken FARIN WATA. RANA duhun hadari, ko shigowar dare, ko shigowar hazo na sanyi ne kawai ke iya risinar da ita a garemu, amma hakan baya hana muga hasken DUNIYA. FARIN WATA, canjawar farkon wata zuwa tsakiya da ƙarshe ke canja mana ganin cikakken kaifin haskensa, sai kaga a ƴan awannin nan daya rissina dole muke amfani da fitilu. Shin hakan na nufin mun makanta ne? ko

wannan hasken shine dama sandar jagorar idanun mu bisa hukuncin mai hukuntawa?”.

Imran ya ɗan furzar da iska yana mai sakin murmushi. Dan shi ya fahimci komai, saboda yasan Zak-Shadow sanin da ko alfahari yayi da duk duniya babu wanda yay masa irin wannan sanin dole a yarda. Faro dai ba komai ya samu warwara a kansa ba. Amma da yake shima ALLAH ya bashi kaifin basira na tunani, sannan ya yarda da Dada yarda ta haƙiƙa sai ya jinjina kai kawai.

[10/02, 9:35 am] Abue Saleh: Dabo, Yusuf dama masu koyi ne daga ƙyawawan hali irin na boss ɗin su. Sannan masu biyayya ne akan ayyukansa musu ƙyau dan sunyi imanin in sha ALLAHU bazai taɓa karkatar da su zuwa mummunar hanyar bijirema UBANGIJI ba.

Shima dai gogan bai sake cewa komai ba. Dan daga haka ma ya miƙe abinsa ya nufi ɗakin nan na sirri ya barsu a falon suna cigaba da tattaunawa. Saboda yanzu dai aiki ya rage garesu.....

<••••><•••><•••><••••>

A gidan Mammah cikin tashin hankalin Ruƙayya suke bayan wanda suke ciki. Dan ta rikice musu ga jikinta ya ɗauki mugun zazzaɓi sai amai take. An kira doctor ya dubata ya tabbatar musu damuwa ce sannan gudun zuciyarta ya canja sosai. Dole ya buƙaci su wuce da ita asibiti. Hakan dole akayi, Ammar ya ɗauketa gaba ɗaya zuwa mota. Yaya Bilal yaja. Ma'aruff da Ja'afar da Mammah suna wata motar. Dan tace bazata iya zama a gidan ba. Suna isa aka fara bata taimakon gaggawa.. Abinda ya sake tada hankalinsu har bayan awanni biyu allurar da sukai mata ta barci taƙi ɗaukar jikinta. Kuma babu abinda sukafi buƙata tayi irin barcin a yanzu. Sunan Ninah kawai take kira. Da ƙyar, da addu'oin da Mammah keta faman tofa mata aka samu nasarar barcin ya ɗauketa. A lokacin kusan 2:30 na dare.

Su Ja'afar sun gagara barin asibitin. Dan cikin ikon ALLAH ma a kusan lokacin sai ga kiran Dada ya shigo wayar Bilal. Ya kira ne dan son jin yaya Mammah ta kwanta dai ko? Sai kuma ya ji akasin lissafi. Yay ɗan jimm na sakanni, kafin ya furta.

“Wane asibiti ne?”.

Sunan asibitin Bilal ya sanar masa. Dada bai ce komai ba ya yanke wayar. Fitowa yay daga ɗakin sirrin daya shiga. Su Imran dake ta faman aiki duk suka ɗago suna kallonsa.

“Faro cikin jami'an daka haɗa ɓangaren masu farin kaya mutum goma suje kk hospital ka tura musu number ɗin su Ma'aruff”.

“Wani abu ne ya faru?”.

Cewar Imran yana tsaresa da idanu. A taƙaice ya ce, “Ruƙayya ce ba lafiya”. Daga haka ya sake juyawa ya koma.

Imran ma aikinsa ya cigaba da yi, sai Faro ne daya ɗauka waya ya fara ƙoƙarin neman ɗaya daga cikin jam'an sirri daya haɗa batare da kowa yasan ɗan uwansa ba.....

★)))((((★))))(((★

“What!”.

Ya faɗa cikin ƙaraji da mamaki yana miƙewa tsaye kamar wanda kunama ta halba a uwawu. Suma sauran duk kallonsa sukayi a razane, kowa na neman ƙarin bayani. Mr Specter ya kalla Oga Jush lips na rawa ya furta, “Wai kasan sun saki hanyar kuwa Oga!”.

Gaba ɗaya meeting room ɗin babu wanda bai nuna razana ba maimakon murna da farin ciki. Black Spider ya ce, “Kai ina akwai matsala. Zak-Shadow ba mahaukaci bane ba fa?.”

“Tabbas ba mahaukaci bane, dan gadararsa ma bazata bari yayi abinda muke so ba cikin awannin goma kacal.” Viper ya faɗa shima cikin tabbatarwa.

Scythe ya ce, “To mi hakan ke nufi?”.
Babu mai wannan amsar, dan haka duk suka zubama Oga Jush da baice komai ba idanu. Sai dai bashi da alamar zai ce ɗin tsahon mintuna uku. Sai da ya gama zuƙe sigarinsa tas kafin.
“Ba mahaukaci bane, sannan ba TSORO yaji ba. Amma dole yay hakan bisa dalilai biyu. Na farko Imran, shine zai tirsasashi dan yarinyar ta dawo, sannan zartarwa da gidan soja a hannun Imran kawai take yanzu tunda shi bai koma aiki ba. Na biyu yana SONTA. Hakan ya nuna a randa ya je station kan case ɗinsu na makaranta...” yaja iska yana ƙoƙarin kunna sabuwar sigari. Dan gaka Iron Fang ya samu damar faɗin, “Amma Oga baka ganin zai yi hakan da wani abu a ƙasa?”.
Baki Oga Jush ya taɓe. “Wannan tunanin naka nakan hanya, dan yana aiki da WAYO fiye da Ƙwaƙwalwa. Amma kar wannan ya dame ka. Ayi mata allurar da zata karya halin da take ciki. A daren nan a kaita inda next plan ɗinmu yake. A ɗorata kan komai cikin awannin da suka rage. Dan hannun karɓa, hannun bayarwa za'ai, kuma a cikin mintunan ƙarshe biyar kacal”.
“What! Oga yanzu nan sakar masa yarinyar nan zamuyi?”.
[10/02, 9:35 am] Abue Saleh: “Muma yin hakan dole ne a garemu. Dan munfi buƙatarta a wajensa fiye da a wajenmu a yanzu. Sannan tana da muhimmanci fiye da komai a garemu a yanzu. Ku ɗauka mune GANGAR JIKI, ita kuma ITACE NUMFASHI. Mi kuke tunani idan da ɗaya babu ɗaya?”.
Tabbas wannan maganar ta Oga ta masifar girgiza su. Dan yanzu sun fahimci girman yarinyar ya wuce ƙaramin tunaninsu a wannan tafiyar. Kuma sai da ita sannan zasu cimma nasarar da suke buƙata. Ashe ba ƙarya bane da akace da yawan yaƙe-yaƙen waɗan nan ƙarnukan suna fara ne ta sanadiyyar MATA. Ga kuwa zahiri suna gani a yau ɗinsu. To bara suga yaya za'a kwashe wannan wasan. SU-NE ko SHI-NE..
Cikin sauke numfashi mai nauyi Viper ya furta, “Tabbas oga mun fahimce ka. Sannan mun gamsu da wannan shirin. Musamman idan mukai dubi da She is a very clever girl. Dan ni ban taɓa ganin mace data bani mamaki ba irinta, idan har a wannan ƙarancin shekarun nata tana a haka ya kake gani nan da wasu 5-years masu zuwa kuma?....”
“A gaskiyar ka Viper, yarinyar KADARA ce mai daraja. Kuma ya kamata ubanta ya ci wannan baiwar tata yanda ya kamata Oga. Lokaci yayi da ƙungiya zata ƙara duba ma Mole ko kuwa ƴan uwa?”.
Yanda ya ƙare maganar da kallonsu su duka. Kai tsaye suka nuna amincewa. Dan girman kai irin na Mr Specter kaga ya yaba wani lallai ko waye ya ciri tuta...........✍
[11/02, 4:36 pm] Abue Saleh: “Kiyi addu'a, in sha ALLAHU nan da wasu awanni zaki ganta. A yanzu haka muna kan aiki tuƙuru, hasali ma mun san inda take amsota kawai ya rage....”
“Dada da gaske?”.
Ta faɗa cikin washe baki.
Murmurshin gefen baki ya mata yana mai lumshe idanunsa da buɗewa alamar tabbatarwa. Ba Ruƙayya kaɗai ba har Mammah da Ammar zancen sa ya musu daɗi. Dan sai da Mmamah ta kauda kai gefe tana ɗauke ƙwallar da suka taru mata a ido, Ammar kuwa ya ɗauki waya ya turama sauran ƴan uwan bayani ta cikin group ɗin su na WhatsApp. Sarai Dada na lure da su su duka har Ammar ɗin. Sai dai baice komai ba. Tea mammah ta haɗa ta bashi. Zai yi magana ta hararesa, murmurshi yayi dole ya amsa. Da zata zuba dankali ne ya lallaɓata yace tea ɗin ya ishesa. Da ƙyar ta yarda. Bai ma wuce sha biyar ba kiran Imran ya shigo masa. Dole ya ajiye yana miƙewa.
“Mammah inaga zan barku, su Imran sun kammala shirinsu. Dole kuma zan rigasu wucewa. Ai mana addu'a”.
Ko bai fito fili ya faɗi inda zasu je ɗin ba Mammah ta fahimta. Dan haka ta fara jera addu'oi masu nauyi sosai a garesu dama al'umma baki ɗaya. Daga haka ya shafa kan Ruƙayya batare da yace komai ba ya fice Ammar biye da shi. Har mota ya rako shi. Sai da ya shiga har ya mata key sannan Ammar ya matsa ya bashi hanya.

Dada akwai nutsuwa, sannan komai nashi zaka sameshi a nutse yake. Sai dai akan aiki baya ƙaunar ƙalula ko wasa, in za'ayi kawai ayi, in baza'ai ba a bari, amma maganar wasa anan ɓangaren ba'ayinsa da shi. Yana da zafin nama irin na jaruman maza...

===============

Kamar yanda suka buƙata an janye sojojin ƙofar yamma tun a daren jiya ƙarfe goma sha ɗaya. Sai dai a maimakon bada Nimrah ko wucewa da abinda suke sonyi wani waje suka kai Nimrah ɗin. Sun kuma nuna mata duk abinda suke son ta sani ta kuma gamsu da su akan zuri'arta. Da farko rashin kunya ta fara zubama su Jagwa dake tare da ita bayan farkowarta, haka ma koda aka kaita gaban wanda sukafi su Jagwa ɗin bata risina ba sai da suka buɗe mata abinda yay matuƙar gigizata. Tabbas tayi shaidar gani da ido, ta kuma shaidar ji da kunne na zahiri. Tayi kuka har hawaye sun daina fita mata. Daga ƙarshe tayi alwashin ɗaukar fansa akan Dada ta hanyar tabbatar masa da DAN HAKKIN DAKA RAINA SHI KE TSOLE MAKA IDO. Dan haka ta ɗauki alwashin zamewa Haysam Abdul-rasheed Shehu Shehu Kobi KIƊA A RUWA. MAI TADA HANKALIN DODO. Idan shi yace ya ƙware a iya FUSKA BIYU zata tabbatar masa da ita kuma RAINON SA ce. Zatai kwanciyar RUWA a gabansa, domin samawa kanta HANYAR wucewa harta ƙofofin gashin jikinsa.....

★★★★

Ƙarfe 12:pm su Imran suka samu saƙon inda zasu amshi Nimrah. Ba kuma a ko'ina bane sai ta inda suka janye sojojinsu. Dan su Oga Jush sunyi alƙawarin a gaban idanun su Imran zasu wuce da kayansu dan su nuna musu MANYAN ƘWARI ne da sukafi ƙarfin kowa. Dan haka suka shirya sosai kuma akan Nimrah da shirin da ita kanta bata sani ba.

Koda Imran ya turama Dada saƙon ya jima yana maimaita shi shiru cikin nazari, dan ya tabbatar zasu iya wasa da hankalinsu. Idan kuma sukai irin wannan tunanin zasu iya aikata yanda suka ce. Ya kamata ace duka kada suyi sakaci, musamman ma shi, dan wannan shine zaren da zai kama na fara shinfiɗa aikinsa akan su.

Bayan ya gama ƙullawa da kwancewa ya turama Imran saƙo shima. Daga haka ya tashi ya fara shirin cikin uniform ɗin soji domin yin ɓadda kama. Dan shi a yanzu ba jami'in sojoji bane a zahiri. Shi Special Presidential Intelligence & Covert Operations Commander ne a yanzu, amma a wannan gaɓar dole yay ɓadda kama cikin sojojin dan samun abinda yake buƙata. Duk da ya san Imran da Faro zasu iya yin duk abinda zai iya yi in sha ALLAHU..

Kodan ya jima bai saka kanyan ba, ko kuwa dan ya ƙara canjawa da cikar kamalar shekaru ne da nutsuwa. Kayan sun masa ƙyau fiye da shekarun baya ma da yake sakasu da ƙuruciya. Buɗaɗɗen jikinsa, zuwa shafaffen cikinsa sun zauna fyaram a cikin kayan. Kai da kaga wannan ZAKIN a cikin waɗan nan kayan manyan kasan kasan ba zakin ajiyewa a gidan zoo bane domin kallon yara.

Received at 7:46 PM

[11/02, 4:37 pm] Abue Saleh: Zaki ne na farauta da in ba'a ma saka masa linzami ko takunkumi ba ɓarnar da zai yi sai ya zama abar rubutawa a tarihin da za'a kafe a bangon gidan gwamnatin ƙasa dan ya zama barazana ga BABBA DA JAKA. Bayan ya saka  Handkachiff kamar facemask ya saka baƙin eyeglass daya ɓoye idanunsa da ainahinsa gaba ɗaya. Sai da ya tabbatar kayan aikin da duk zai iya buƙata na cikin jikinsa sannan ya fito compound ɗin gidan. Dan yana a UNIT ZERO ne shi kaɗai. Parking space ya nufa kai tsaye cikin takun sa na masu ƙarfin jini da babu wasa a ciki ko wani rangwaɗar shashanci, dan wannan mazan a mazansu suke kai tsaye. Hannu ya kai kan blue tempol da aka rufe wani abu ya yaye shi, sai ga wani gingimemen ƙaton mashin baƙi wulik mai shegen ƙyau da tsari ya bayyana. Da allama madadin tsohon mashin ɗinsa ne ya dawo a sabon salo, sabon zamani. Hularsa dake ajiye

samansa ya ɗauka ya saka, kafin ya haye yana karanta addu'a yay masa key. Koda yazo gate remote ya danna ya buɗe da kansa, yana gama ficewa ya maida ya rufe kansa. Shi kuma ya ɗauki hanya..........✍

Mun tafi amso Ninah. Wanda ya shirya muje zuwa♀♀♀♀😎.
Received at 7:46 PM
[11/02, 4:37 pm] Abue Saleh: 4

........“Mtsowww!!”. Wani soja yaja tsaki yana kallon agogon hannunsa. Tun 12:30 suke a wajen nan, gashi har 3pm babu alamar abinda suke zaman jira ɗin zai samu. Gashi ko zaman cin abinci a nutse oga ya hana su. Salla kawai ake basu damar yi, wanda ma basayi su basu da ko minti na hutawa. A kaikaice ya ɗan wurgama Imran harara, yana ganin zai juyo ya tsume ya gyara tsaiwarsa. Oho shi Imran ɗin ma bai san yanayi ba, umarni ne dai ya bayar matsayinsa na oga kuma dole-dole abi.

A daji suke iya daji, dan ko dabbobin jeji akace za'a samu masu haɗari a wajen baza'ai musu ba. Dajin mahaɗa ce ta ƙasashe guda uku, daga nan zaka iya shiga kowacce ƙasa cikin sauƙi. Hakan yasa akowane iyaka akwai jami'an soji da aka ajiye na kowacce ƙasa da sauran jami'ai. Sai dai kowa da yanda yake gudanar da aikin sa da kuma iyakarsa. A tasu iyakar babu soja ko ɗaya bayan su ɗin nan da aka kawo awanni uku da suka gabata, gaba ɗayansu su ashirin ne kuma har oganni su guda uku. Abin takaicin kuma wai an kawosu ne kawai dan amsar rai guda ɗaya, ran ma na mace, macen ma yarinya ƙarama ƴar 16years. Wannan wane kalar abin haushi ne, duk da su jami'ai ne masu bada kariya ga al'umma ai bai kamata ace dan rai ɗaya an lalatar da lokacinsu a wajen ba, lalatarwar kuma da suma zasu iya rasa nasu ran. Tunda basu san wane shiri mutanen nan ke da shi ba a kansu. Zata iya yiwuwa sun shirya musu wani tuggu ko kisan mummuƙe bayan sun samu cikar burinsu. “Mtsoww!!” ya sake jan tsakin dai yana kallon agogo. Gulma yake son suyi dana kusa da shi, amma ba dama oga na kallonsu. Dole ya haƙura kamar kowa shima ya dake. A haka 4pm ta cika. Masu salla har sun gabatar.

4:23pm dai-dai kira ya shigo layin Imran. A tare Imran da Dada daya saje cikin yaran Imran ta yanda babu wanda ya gane shi ne suka kalla wayar. Sai kuma suka haɗa ido. Idanu Dadan ya lumshe masa alamar ya ɗaga, sai kuma ya gyara tsaiwa cikin basarwa ya koma kamar yanda yaran keta kai kawo. Sai dai duk abinda Imran ke saurare a cikin wayar shima yana ji, dan sun raba bluetooth ɗin ne kowa da ɗaya a kunnensa.

“Nan da mintuna talatin da bakwai kayanmu zasu iso. Zasu wuce zamu baku ita. Idan kukace zakuyi wani yunƙuri zakuga sakamakon hakanne a kanta. Daga yanzu ka fara ƙirga lokaci, sannan ga saƙo ka faɗama oganka, YA KULA DA KANSA. Idan ya shagala a kula da wannan ƘASAR, shine zai zama ƘASAR dan a maimakon kejin prison wannan karon CIKIN KABARI zai shiga”. Ƙittt. Wayar ta yanke kafin Imran ya iya cewa komai.

Kamar yanda Imran ya ji komai, shi ma Dada ya ji komai. Sai dai wannan ba shine lissafin sa ba a yanzu. Ta inda Nimrah kawai zata bayyana yake kallo.

4:40pm dai-dai baƙar mota mai duhun glass ta iso wajen, sai dai nesa da su kaɗan. Sannan ta ɗayan ɓangaren ba ɓangaren da suke ba. Gaba ɗaya hankalinsu akan motar yake, sai dai tunda ta tsaya babu wanda ya fita a ciki sai da ƙurar da suka tayar ta gama kwanciya kusan mintuna uku. 4:45 aka buɗe murfin motar, jibga-jibgan garada guda biyu majiya ƙarfi suka fito cikin shigar rufe jiki gaba ɗaya dan babu abinda ake gani nasu. Ɗaya ya buɗe baya Nimrah ta fito. Kayan dake jikinta ne dai na jiya, sai dai yanzu an rufe mata baki, hakama idanunta da baƙin ƙyalle. Ƙafarata babu takalmi. Sannan an ɗaure mata hannayenta da aka maida baya. Sun lulluɓa mata towel alamar akwai abinda suka rufe a jikinta. Dan Imran har ya motsa

saukar idanunsa akan towel ɗin da suka rufa mata ɗin ne ya saka shi tsayawa cak. Shi fa jam'in soja ne, daya kwashe shekaru yana aiki tun ƙuruciya. Ta ya zai gagara gane kowanne makirci koda daga nesa ne.

Inda Dada yake ya kalla, sai ya ga shima Dada ya kallo shi. Da ido Imran ya masa magana, Dada ya mayar masa murtani alamar ya gane komai. Sake maida dubansu sukai kan Nimrah, a kuma dai-dai lokacin mutanen dake tare da ita suka yaye towel ɗin jikin nata. Bayyanar rigar bomb ta saka yaran sojojin zabura baya a firgice, shi kansa Imran da Dada sai da zukatansu suka buga duk da dama abinda sukai hasashen gani kenan.

Received at 7:46 PM

[11/02, 4:38 pm] Abue Saleh: “Da....d...dah!”.

Ta faɗa lips ɗin nata na rawa sosai fiye da da. Murmurshi mai nauyi ya sakar mata. Murmurshin da zata iya rantsuwar bata taɓa ganin irinsa akan fuskarsa ba. Sai kawai hawaye suka shiga silalo mata. Ta sake buɗe baki zata yi magana ya girgiza mata kansa. Tare da ciro dabino a aljihunsa ya sashi a bakinsa ya raba biyu ya cire rabin ya nufi bakinta da shi...

“Haah”.

Ya faɗa a hankali. Ai bama tasan ta buɗe lips ɗin nata ba a hankali ya saka mata. Sai kuma ya shafa lips ɗin nata da yatsa yana sakar mata wani murmushin. Ita dai kallonsa take kamar sakara, tama kasa tauna dabinon. Yanda ma ta shagala a kallonsa kamar wadda ta suma sai da ya fara share mata hawayen da suka gagara tsayawa sannan ta kawo nannauyan numfashi alamar dawowa hayyacinta..

Baiyi magana ba, bai kuma daina murmurshin ba, ya dai maida hankalinsa akan wayoyin bomb ɗin cike da nazari, bayan ya kalla lokacin daya rage musu 18-minutes........✍

[14/02, 9:15 am] Abue Saleh: Sai ta samawa kanta lafiya akan ai yau ma rana ce. Dan haka yau ɗin ma ta matsu su taho da wurin nan.

Har akai la'asar ƙawayen nata na nan. Sai da suka gama shaƙiyancinsu da ɗirka mata abubuwa sannan wajen 5 suka tafi. Da Ismat kawai aka barta, dan su Amimah basu biyosu ba. Itama Ismat ɗin Momy bata san ta biyosu ba, so take kuma daga nan ta gudu gidan Abbansu kawai.

Ismat ɗin ta tura yau ma gano mata ko yana nan, idan ma baya nan taje wai dan su Mammah su san ta dawo, ai tasan Mammah ɗin zata saka shi zuwa inda take ko bai niyya ba. Sai dai me, Ismat na zuwa ta dawo mata da labari mara daɗi. Cewar shi baima kwana a gidan ba. Su Mammah kuma duk suna asibiti Ruƙayya babu lafiya. Ga kuma Lailah ma ta faɗi an shiga da ita cs har yanzu ba'a fito da ita ba.

Maimakon hankalin Nabeeha ya tashi tace suje asibitin sai tayi shiru. Sai ita Ismat ɗin ce ta ce, “Aunty kodai asibitin zamuje muma. Dan na fahimci abin fa babbane, hankalin masu aikin nasu duk a tashe yake wlhy”.

“K rabani da wani asibiti Ismat babu inda zanje gaskiya. A gama zuba min wannan uban ƙamshin a jiki da gyara ni na kuma ƙare a asibiti. Ƙamshi nake son D. ya ji ba warin magunguna ba”.

“Amma Aunty.....”

“Kefa matsalata dake kenan. To ALLAH zan kora ki gida yanzu. Haba ki fahimceni mana. Ke bama ƙya ganin idan nace zan fita daga kawoni akwai ganganci a ciki. Karfa ki manta yanda D. Ya tsani yawo”.

“Hummmm”.

Ismat ta faɗa kawai. A ranta ko faɗi take (Baki san ya tsani yawon ba sai yanzu. Bayan tunda yabar gidan kema baki zauna ba Aunty. Kina tunanin kuma baza'a sanar masa ba. Ke matsalar ki baƙya son gaskiya da ɗaukar shawara. Kin bar Momy ta tasirantar da ƙiyayyar dangin mijinki kuma ƴan uwanmu ma ta wani fannin a zuciyarki. ALLAH yasa ki gane, dan inba haka ba wannan karon ma zaman nan naki bamai ɗorewa bane. Dan yanzu mutanen gidan nan bana da bane da suke miki kawaici, sun ɗanɗana zama da wasu surukan sun ji daɗi)...

<<••>><•••••><<••>>

“Dada zan MUTU ko? Zan mutu bazan sake ganin Mammah da Ruky ba, bazan sake ganin su Uncle's Ja'afar ba da su Mu'azz”.

Dada da hankalinsa gaba ɗaya ke kan aikinsa ya saki murmurshi kaɗan. Sai kuma ya ɗan taɓe baki da faɗin, “Bayan kin shiga labor room sau goma sha biyu, kin haifo magadan SOJA, jikokin Abdul-rasheed Shehu Kobi ko Kiddo?”.

Ita sam bata wani fahimcesa ba. Shima kuma yanda yay maganar a basarwarsa yana kuma aikinsa bama zakace shi ya faɗa ɗin ba. Ya sake kallon mintinan da suka rage. 9 kawai. Dai-dai nan Imran dake nufosu ya taka wani abu. Cak ya tsaya yana kallon ƙafarsa. Dan haka Faro dake kallonsa shima ya ce, “Yaya dai?”.

Ƙafarsa ya nuna masa sannan yay masa alamar bomb. Sai kuma yay masa nunin yay shiru kada Dada yaji. Ya ilahi wata muguwar bugawa zuciyar Faro tayi, a take jikinsa ya kama rawa. Ya kalla Imran ya kalla su Dada. Ya rasa ma ina zai kama. Suma sauran sojojin hankalinsu ya tashi matuƙa. A take suka fara zagaye wajen da na'urorin bincike bomb. Dan tunda ogansu ya taka hakan na nufin akwai wasu a wajen. Ai ko sai gasu cikin ikon ALLAH kusan bakwai a cikin ƙasa irin wanda Imran ɗin ya taka. Tuni masu ilimin akansa suka fara aikinsu. Sauran jami'an suka ja baya sosai. Sai dai Faro ya kasa yin hakan. Ya kafa ma su Dabo idanunsa kawai da sukayi jazur na tashin hankali...

“Dada ƙara min Dabino”.

Nimrah ta faɗa idanunta a rufe dan ta sadaƙar kawai lokaci yayi. Shi kansa uban gayyar hankalinsa ya gama kaiwa ƙarshen tashi. Dan saura minti huɗu ya rage musu. Gashi ya katse waya har biyu basu bane, saima ƙara na ƙidaya lokaci da suka saka bomb ɗin ya fara. Dabinon ya ciro ya saka mata a baki, batare daya bar abinda yake ba.

A dai-dai wannan lokacin kuma Faro ne ɗauke da wani ƙaton dutsi yana tafiya a hankali a hankali ta bayan Imran dake tsaye cak a wajen nan har yanzu idanunsa a rufe. Babu abinda yake maimaitawa sai kalmar shahada a zuciyarsa. Dan ya riga ya sadaukar ya kuma sadaƙar yau babu makawa ranar amsa kiran UBANGIJI ce. Babban fatansa Nimrah da Haysam su tsira a idanunsa kafin lokaci ya cika.....

Received at 10:47 AM

[14/02, 9:15 am] Abue Saleh: 6

.........Fitowar doctors ya sanya gaba ɗayansu zabura, Gwaggo Khadijah da Mammah ne kawai basu tashi ba. Doctor ta saki murmushi mai faɗi ganin duk sun zubo mata idanun cike da ƙaguwa. “Alhamdullahi congratulations. Mun samu nasarar ciro Baby girl cikin ƙoshin lafiya”.

Wasu irin nauyayan ajiyar zuciya suka shiga saukewa a tare. Yayinda Ma'aruff ya kai duƙe yay sujidar shukur. Dai-dai nan Nurse ɗin dake ɗauke da jaririyar ta fito daga bayan doctor. Hannu biyu Ammar dake kusa da ita ya saka ya amshi Babyn, fuskarsa washe da murmushi ya nufi Mammah. Amma saboda kawaici irin nata sai ta nuna masa Gwaggo Khadijah. Ƙaramar dariya yayi cikin jin kunyar abinda yay ɗin shima ya miƙama Gwaggo Khadijah ɗin...

Suna cikin farin cikin kallon Baby aka fito da Lailah da za'a miƙa ɗakin hutu. Ma'aruff ya kai duƙe gaban gadon yana mai kama hannunta. Itama kallonsa take dan idanunta biyu har akayi aka kammala Alhmdllh. Yanda shima ya zuba mata idanunsa da suka rine saboda tashin hankali ya sata sakar masa murmushi. Sai kuma ta ɗaga hannunta takai fuskarsa ta shafa. Hannun nata ya kamo, ya matso da shi a hankali kan lips ɗinsa ya sumbata. Kafin ƙasa-ƙasa ya furta, “ALLAH yay miki albarka Mar'atussaliha. ALLAH ya baki lafiya”.

Kai ta jinjina masa kawai cikin lumshe idanunta da sukai mata nauyi. Isowar su Mammah wajen yasa ta fara ƙoƙarin janye hannunta da har yanzu yake akan fuskarsa. Shi ko idanunsa akanta suke bai gansu ba, sai ya sake damƙeshi. Sai da

Ja'afar ya zungure shi cike da shaƙiyanci. Ya ɗago da nufin harararsa sukai ido huɗu da Mammah da Gwaggo Khadijah. Ai da gudu yay ƙasa da kansa yana sakarma Lailah hannu. Su Bilal suka gimtse dariya. Ƙasa-ƙasa Ammar yay magana a kunnen Bilal. “Yaya Billa muma dai ALLAH ya aurar damu. Dan gaskiya an tafi da ni”.

Mintsini mai zafi Bilal ya sakar masa ya gefen ciki. Ya ce “Unch!”. Duk juyowa sukai suna kallonsa. Ruky ta saki dariya batare da tayi niyya ba. Juyawa yay inda take yana kai mata rankwashi. Da sauri ta maƙale jikin Gwaggon Alawiyya. Mammah dake harararsa ta ce, “Yanzu wadda ke gadon asibiti zaka daka Ammar?”.

“Mammah dariya fa tamin”.

“To wannan ihun da tsallen daka buga ba dole tai dariya ba, sai kace wanda kunama ta harba”.

Caraf Ruky ta ce, “Mammah mintsini ya sha wajen Uncle Billa, wai aure yake so dan ALLAH a gaggauta a masa kada ya.....”

Da bala'in sauri Ammar ya waro idanu waje jin harda sharri ta ƙara masa. Bilal ya kwashe da dariya. Dan gaba ɗaya yanda Ammar ɗin ya daburce har yana damƙo Ruky ya rufe mata baki dole abin ya ta baka dariya. Su kansu su Ja'afar daƙyar suka danne. Ruky nata mutsu-mutsun san ƙwacewa yaƙi sakinta sai da Mammah tace, “Malam sakar min yarinya kada ka cire mata haƙori. Badai aure ba, bari Muhammad yazo za'a maka”.

Bashi da zaɓin daya wuce sakin Ruky yabar wajen saboda kunya, ji yake kamar ƙasa ta tsage ya shige. A ransa kam ayyanawa yake sai yayi maganin bakin Ruky. Murmushi kawai su Ma'aruff sukai suna girgiza kawuna. Sai Mu'azz dake ma Ruky gwalo tana harrarsa da gyara hular kanta da Uncle Ammar ya zame tana maƙale da Mammah.

An shigar da Lailah dan haka suma suka koma ɗakin jiyyar Ruƙayya aka fara kiran ƴan uwa da abokan arziƙi kuma. Duk da hankalinsu a rarrabe yake akan al'amarin Nimrah, amma an fita daga wata matsalar Alhamdullah. Dan kasancewar jaririyar a hannunsu har yanzu har hirar da yanzu tana nan data hana kowa ɗauka akayi. Atake damuwarsu ta sake dawowa sabuwa. Kowa ya shiga jero addu'oin gareta. Mammah da batace komai ba kuwa layin Dada ta fara ƙoƙarin kira. Sai dai gashi tana ringing amma ba'a ɗaga ba. Bata damu ba dan tasan tunda har ta yanke bai ɗaga ɗin ba yana kan aiki ne........

××××××××××××××××

Vibration ɗin wayarsa dake jikinsa ne ya farko da shi daga ƙaramar sumar da yayi sakamakon azababbiyar bugun zuciyar data riski ƙirjinsa a lokacin da ƙarar fashewar bomb ɗin ta nema tarwatsa dodon kunnensa. A hankali ya buɗe idanunsa, ya zubama sauran baƙin hayaƙin dake yawo a samaniyar inda suken.

Received at 10:47 AM

Viewed 1 time

[14/02, 9:15 am] Abue Saleh: Sai kuma tarin sauran sojoji daya karaɗe wajen da ƙananun hayaniya...

“Innalillahi wa-inna ilaihiraji'un
Imran...”

Kalma ta farko data sakashi tashi a razane. Bai damu da ƙasar data wanke jikinsa ba. Ya kai dubansa inda ake kiran Imran ɗin. Ganin Faro ya ɗago shi fuskarsa wanke da jini ya saka duniyarsa sake girgizawa. Baima san ya miƙe kan ƙafafunsa ya nufi inda suke ba. A lokacin su ma su Yusuf suka iso da gudu ɗauke da ɗan gadon bada taimakon gaggawa. Dada ji yake kamar kansa zai tarwatse. Dan yana isowa daga can wani soja cikin ƙaraji ya furta, “Bomb ɗin nan ya tashi da yarinyar nan f....”

Ai baima ƙarasa ba duhu ya mamaye idanun Dada. Kawai yaci tuntuɓe da Faro zai zube sai da aka riƙoshi. Dole Faro ya sakar musu Imran ya miƙe yana kama Dada. Zaunar da shi yayi, tare da amsar gorar ruwan da wani soja ya kawo ya ɓalle murfin ya saka masa a baki. Hannu yasa zai ture Faro yay saurin dakatar da shi...

“Dan ALLAH kasha ko kaɗan”.

Kurɓa ɗaya yayi ya kauda kansa. Faro zai sake magana wani soja ya katse hakan ta hanyar ƙwala kira, “Sirs!!!!!”.

Ai a tare suka zabura. Sojoji sukai wajen da gudu. Dole Faro ya miƙe shima. Sai kawai Dada ya miƙe cikin ƙoƙarin danne firgicinsa shima ya nufesu. Yayinda motar data ɗauki Imran tabar wajen dan nufar asibiti da shi...

“Bata mutu ba!”.

Furucin daya nema sakashi amayo zuciyarsa ta baki. Tuni ya fasa sojojin ya shiga. Caraf ta riƙe sojan dake ƙoƙarin kai hannu kan Nimrah dake kwance ƙasa ta buleta har ba'a ganinta da ƙyau. Sojan zai yi magana Faro ya ce, “Leave...”

Dole yaja jikinsa baya. Dada yakai duƙe wajen yana saka hannayesa ya zarota gaba ɗayanta, bai damu da ƙasar dake jikinta ba ya sakata a nashi jikin kawai ya rungume yana sauke wani irin bahagon wahallen jerarrun ajiyar zuciya. Ganin haka Faro yama sojojin umarnin barin wajen domin bincika ya akai haka. Dan bomb ɗin daya tashi dai na jikinta ne. Wanda Imran ya taka yayi nasarar danna masa dutsi a dai-dai lokacin da na jikin nata ke fashewa, shi kuma Imran ya ɗaga ƙafarsa saboda razanin tunanin wanda ya taka ne, shine sukai tsalle gefe kan Imran ya daki dutsin....

“Tabbas yarinyar nan nada wayo, dan sai dai idan cire rigar nan tai tayi jifa da ita Sir”.

Sosai Faro ke jin gamsuwa da abinda sojan ke faɗa. Haka ma sauran sojojin dan sun gama dube-duben su da aune-aune. Kuma gaba ɗaya alama ta nuna musu a sama Bomb ɗin ya tashi musamman yanda yay nesa da inda suke. Sannan itama aka cillata gefe ƙasa ta rufeta. Dada dake ƙoƙarin sake zubama Nimrah ruwa a fuska da Yusuf ke zuba masa a hannu duk yana saurarensu. Sai dai hankalinsa ba'a kansu yake ba. Zubawa ta uku babu alamar zata farfaɗo. Ga masu son bata taimakon gaggawa yaƙi basu dama. Ya zuba mata na huɗu yana ɗan bubbuga kumatunta wani ya yunƙuro zai yi maganar kodai a wuce da ita asibiti kawai saita wani irin banƙare, da sauri ya riƙota da ƙyau ya matse a jikinsa. Wata razananniyar ƙara ta saki mai firgitarwa tana fisga zata fita a jikin nashi gaba ɗaya. Da yake ƙarfin ba ɗaya ba dannawa ɗaya ya maida ita. Dole hankalin su Faro ya dawo wajen gaba ɗaya, cikin sauri aka kawo mota wajen, dan dole a wuce da ita asibiti da gaggawa....

©©©©©©©©©©©©

“Done Oga. Komai yazo hannu”.

Wani murmushin ƙasaita Oga Jush ya saki yana kallon Viper. Sai kuma ya miƙa masa hannu alamar yazo gareshi. Matsawa yay suka rungume juna.

“Proud of you darling”.

Oga Jush ya faɗa yana bubbuga bayan Viper. Matuƙar farin ciki Viper ya ƙara jinsa a ciki. Ya rissina cike da girmamawa shima ya ce, “Proud of you too Sir”.

Oga Jush yay murmushi mai faɗi yana jinjina masa kai da lumshe idanu. Kafin ya gyara zama da faɗin, “Yarinyar fa?”.

“Gaskiya tana da wayo, ta kuɓuta. Amma kaɗan ya rage a samu matsala”.
Received at 10:47 AM
[14/02, 9:15 am] Abue Saleh: “Hakan na nufin zatai mana abinda muke buƙata sosai ai”.

“Tabbas zata iya, sai dai Oga data mutu fa?”.

“Dama ɗayan biyu ne tsarin ai, kota mutu a wannan gaɓar ubanta ya ƙarasa aikin, shi kuma mu gigita duniyarsa da rashinta. Kota tsira tayi mana aikin. Kaga tunda ta tsira ƴar sa'a ce kenan.”

“Gaskiya ƴar sa'a ce kam Sir. Abinda ma zai saka ka farin ciki shine, duk abinda muka nuna mata tayi na'am da shi, damma bata san waye ke aureta nata ba”.

"Wannan ai shine babban makamin mu a kanta, shiyyasa nace kada ku faɗa mata waye mijin, taje ta bincika da kanta. Yaya batun yaran?".
"Duk sun bamu haɗin kai. Sannan da yawansu ta tuna fuskokinsu".
"Good. Sai mu je Batch B. A sanar da kowa akwai meeting gobe da safe."
"Okay Sir"..........✍
[14/02, 7:48 am] null: KIƊA A RUWA 3

7

........★9:pm★

Sai a wannan lokacin Dada da Faro suka sami damar ganin Imran. Duk da tun ɗazun ya farfaɗo allurar da sukai masa ta saka shi barci ya saka sai yanzu aka basu damar shiga inda suke. Duk da daga shi har Nimrah sun kawo su wani sirrintaccen asibiti ne.

Kalma ta farko da ya fara furta musu shi ne, "Ina Nimrah?".

Murmushi Faro yayi da faɗin, "Relax Colonel. Ɗiyarka na nan lafiya lau Alhamdullah. Duk da itama muna jiran ji daga doctors ne akanta amma in sha ALLAHU komai mai sauƙi ne, bakaga mijinta na tsaye kan ƙafafunsa ba".

"Alhamdullahi".

Ya sake faɗa a hankali yana kallon Dada daya zuba masa juyayyun idanunsa. Murmushi kwantar da hankali ya sakar masa. Sai kuma ya motsa a hankali zai tashi. Fuska ya yamutse da saurin kai hannu saman kansa da yay masa nauyi. Riƙe san da yaji anyi ya sashi buɗe idanunsa daya lumshe. Akan Dada ya sauke su, dan shine ya riƙe san.

Hararar da Dadan ya sakar masa ta saka shi yin murmushi. A hakanli ya furta, "Miye na hararata?".

"Gaggawar ta miye?".

Ya faɗa yana maida shi ya kwantar. Sai kawai Imran ya sake yin ɗan murmurshi. Koda ya sake jeho musu tambayar miya faru da batun tashin bomb?.

Kaɗan Faro ya masa bayani dan ya samu nutsuwa. Sauran yace sai ya samu lafiya. Dada dai na tsaye yana saurarensu. Sai dai ya zubama Imran idanunsa cike da yanayi na damuwar halin da yake ciki, dan ji yake kamar ya ɗauke ciwon daga jikinsa ya maido nasa jikin. Motsin da wayarsa tayi alamar shigowar kira yasa ya ɗan ja numfashi ya fesar. Batare da yayi magana ba ya ciro ta a aljihu.

Ficewa yay a ɗakin cikin muryarsa data koma ƙasa sosai alamar gajiya, dan rabonsa da abinci ma tun safe. Shima ba wani breakfast ɗin kirki bane ba. Normal black tea ne da dafaffen ƙwai uku.

Daga can Mammah tai ɗan tsai tana sauraren gaisuwar da yake mata, sai dai maimakon amsawa tambaya ta jeho masa.

"Yana jika haka? Ko akwai wata matsalar ne?".

Sai da yay ƙaramin murmushi daya tsaya masa iya lips kafin ya ɗan sauke ajiyar zuciya. "A'a kawai gajiya ce Mammah...."

"Da yunwa kuma ba. Tunda kai da abinci maƙiyan juna ne Muhammad. Yanzu dai ga su Bilal nan zasu kawo muku abinci. Dan naga alamar ba sallamoku zasuyi ba a yau ɗin nan. Kai kuma ka hanamu muzo, gashi kowa ya ƙagu yaganta".

Yanzu kam murmurshin sa har sai da ya bayyana akan fuskarsa. Ya ɗan zubama ɗakin da Nimrah ke kwance idanunsa. "Ba hanaku nai ba, kawai dai yanayin aikin ne a haka. Suma su Bilal ɗin su bari zan turo Dabo ya amsa abincin".

"Muhammad kodai wani abu ya samar min Nimrah ne kake ɓoye min?".

Yasan za'a rina. Dan tun bayan zuwansu asibitin yay kiranta ya sanar mata suna asibiti amma bawani damuwa firgita ce ta sakata suma amma basai sun zo ba saboda yanayin tsaro. Amma sai da yaji Mammah ta jinjina kamar dai bata so ace kar su zo ɗin ba....

"Muhammad!".

Ta faɗa cikin sanyi dake bayyana damuwarta. Iska ya ɗan furzar da gyara muryarsa, cike da kulawa yace, “Mammah ki kwantar da hankalinki. Babu wata damuwa. Da acema ba barci take ba da tuni na haɗaki da ita. Amma in sha ALLAHU zuwa da safe zasu sallameta. Idan basuyi hakan ba zanzo na ɗaukeki da kaina na kawoki”.

Ajiyar zuciya ta sauke mai ƙarfi. “Shi ke nan ALLAH ya ƙara musu lafiya. Yaya shi Baban nasu?”.

“Shima Alhamdullah, dan daga wajensa na fito ma ya farka.”

“Masha ALLAH. ALLAH ya kiyaye gaba to. Ka aiko to a amshi abincin. Zan haɗo da kaya kuma ko zaku buƙata dan nasan Nimrah da ƙyanƙyami, kayan jikin nan nata na tabbatar sun isheta”.

A hankali ya ce, “Uhmm”.

Daga haka sukai sallama Mammah najin nutsuwa. Suma da daren nan suka koma gida dan tunda Ruky taji anga Nimrah ta sake watsakkewa. Lailah suka baro da Ammie da taje zata zauna da ita...

★★★ Dai-dai yana katse wayar aka buɗe ƙofar ɗakin da Nimrah take. Ta ƙasan ido ya ɗan duba wajen, sai kuma ya janye lokaci guda. Dan duk ƙwaf ɗinka zaka ɗauka hankalinsa akan wayarsa yake. Doctor da ke fitowa Nurse a tare da ita ta rage yanayin ɗan hanzarin data fito da shi. Dan gaba ɗaya kwarjininsa ya cika mata wajen. Itama ba yarinya bace, sannan da aurenta, sai dai Dada ya girmeta sosai gaskiya. Tun ɗazun yanayin tsare gidansa da gizago yasa ya cika musu idanu. Dan irinsu Dada ko babu alaƙa, ko baka taɓa saninsu ba a gani ɗaya kamalarsu da cikar haiba ke siya musu girma ga mai kallonsu.

“Barka ranka ya daɗe, dama neman ku na fito”.

Baiyi magana ba, bai kuma kalleta ba. Amma ya janye wayar daga idanunsa alamar yana saurarenta. Itama fahimtar hakan ya sakata cigaba da bayaninta kawai. Itako Nurse a kaikaice ta zubama masa idanu tanata tasbihi ga UBANGIJI mahaliccin wannan nutsatstsiyar halitta...

“Ta farka, sai dai jikinta akwai zafi sosai, dole ko yaya a goge mata shi da ruwa mai ɗan sauƙin sanyi. Sannan akwai yunwa a tare da ita. Ga Nurse zata goge mata jikin yanzu sai abinda zata cin muke buƙata”.

“Uhmm”.

Kawai yace a taƙaice. Doctor data fahimci amsar kenan sai itama ta ɗan sake risinawar girmamawa tana barin wajen. Nurse kam da taso ita kam dai taji yayi magana sai taji kamar ta fasa ihu. Dole tabi umarnin doctor data bata na zuwa ta samar da abin zuba ruwan. Fin minti guda da wucewar su ya taka zuwa kofar ɗakin. Hakan yasa Faro daya tunkaro shi komawa baya kawai yana ɗan murmurshi. Shi ko Dada da bai gansa ba har ya shige...

Yanda ta duƙunƙune jikinta cikin blanket ya sashi zubama gadon ido sosai. Ta rufe har kanta, sannan a dunƙule take waje guda. Hakan na nufin a tsorace take har yanzu, ko tana jin sanyi. Shiru kamar bazai ƙarasa ba, sai da kunnensa ya fara ji masa kamar tana jan shashshekar kuka sannan. Matsowarsa gaban gadon da ƙyau ya tabbatar masa kukan take kuwa. Maimakon yin magana hannu ya kai zai janye blanket ɗin duk da bai ma san ina kanta yake ba saboda yanda take a cure.

Firgigit Nimrah ta zabura. Dan tana cikin wani yanayi ne na wanda abu ke dawo ma a rai. Cikin zafin nama Dada ya tarota, saboda yanda ta zaburan sai ta tafi gaba ɗaya zata wantsalo ƙasa. Ita kuwa batare da tunanin waye ba kawai ta cukuykuye shi a yanda yake a tsayen. Dan kanta ta kwantar a saman shafaffen cikinsa ta zagayo da hannayenta a bayansa ta matse tsamm. Da ace ragon namiji ne babu abinda zai hanashi jin matsar nan har cikin ƙashi. Amma da yake mazan mazan fama ne ko gezau, sai dai abin yazo masa a bazata daya tilasta shi lumshe idanunsa kawai. Fin minti guda suna a haka, zafin zazzaɓinta ya fara shiga jikinsa. Sai ɗumin hawayenta dake sauka masa akan riga har danshin na taɓa jikinsa, ga jikinta na ɗan rawa-rawa kaɗan, sai dai bai sani ba na tsoro ne kona jin sanyi...

Kai tsaye Nurse da bata san da shi a ciki ba ta buɗe ƙofar. Sai da ta juyo bayan ta rufe tai arangama da shi. Da gudun tsiya taja ta tsaya. Lips na rawa ta ce, “Ka...k....”

Wani mugun watso mata idanu yay da mata alamar tai shiru. Aiko kamar wata sokuwa tasa hannu ta dafe bakin nata tana risinar da kanta. A haka ta ƙaraso gaban gadon ta ajiye ƙaramin botikin hannunta na roba. Sai towel ƙarami shima sabo a ledarsa. Ta gefen ido take satar kallonsu da yin gulma a zuciyarta. (Uhumm lallai wannan ƴa na son Babanta. Kaga ƴar shagwaɓa. Ai dake zan kama ƙafa na samu shiga wajen wannan Barden mazajen. Dan daga gani kam ke ƴar lelensa ce...)

Da alama dai Nurse ita tasan ma tana yi. Dan shi dai Dada na tsayensa har yanzu. Ga Nimrah ta masa ɗaurin goro. Shi kuma ya ma gagara yin komai, sai da Nimrah ta ɗan zabura har tana neman sakashi yin baya sannan ya ɗora duk hannayensa biyu a jikinta batare daya shirya ba. Ɗaya a gadon bayanta ɗaya akanta da ɗan kwalin ya fita. Sai dai akwai kitso ƙanana da suka mata ƙyau cikku dan tana son cikku sosai. Itama Nurse ɗin zaburowa tai kamar zata tare Nimrah ɗin duk da taga a jikinsa take amma da yake neman uwawun zama take itama sai tazo nuna bajinta.

Received at 10:47 AM Yanzun ma kallo irin na ɗazun yay mata, dole ta dakata da gudu tana kai hannu ta sosa ƙeya tana jan jikinta baya. Shima daya tabbatar wannan yanayin zai iya saka cutuwa, a karo na farko ya furzar da iska yana shafa kan nata, ƙasa-ƙasa ya furta, “It's okay Babie” sai kuma ya kamata slowly ya maida saman gadon ya zaunar. Taƙi sakin hannunta dake zagaye da ƙugunsa, dole ya kai nasa hannun da kansa ya janye natan. Kuka ta sake fashewa da shi tana ƙoƙarin sake cusa kanta a jikinsa. Bai bari tayi hakan ba ya kai zaune kusa da ita. Sai kawai ta sake faɗa masa a jiki tana cukuykuye kan nata dai..........✍

[14/02, 7:48 am] null: KIƊA A RUWA 3

8

.........Nurse data fahimci yanayin Nimrah ɗin cike da son birge shi ta zabura tana faɗin, “Yallaɓai bari na sanar da Doctor, dan kam akwai matsala a firgice take. Dama Doctor tayi magana ɗazun data farka akan ALLAH yasa kada ta shiga yanayin...”

Yanda bai tanka ba a ɗazun yanzu ma hakan ne. Itama bata jira amsar tashi ba ta fice a hanzarce. Ai ko babu jimawa sai gasu sun shigo. Har yanzu kuma Nimrah ta hanashi ko motsi tsabar yanda ta cukuykuye sa. Dan zuwa yanzu gaba ɗaya rabin jikinta akan nashi yake. Cikin lallashi Doctor tai magana tana kamo hannunta. Amma sai ta fisge tana fashewa da kuka da sambatu irin na tabbacin bata cikin hayyacinta...

Doctor ta rasa yanda zatai aikinta saboda yanda take jikinsa. Gashi maganar duniya Nimrah taƙi ɗagowa....

“Miye matsalar?”.

Dada ya faɗa yana ɗan kallon likitar a karo na farko. Sai kuma ya janye idanun nasa duk a lokaci guda. Itama ba iya kallonsa take ba, dan haka ta fara masa bayani yanda zai fahimta...... Da ga ƙarshe ta ce, “Yanzu akwai allurar dazan mata, in sha ALLAHU ƴan mintuna ne nutsuwarta zata dawo, dan har yanzu abinda ya faru bai bar brain ɗinta bane gaba ɗaya. Rashin tabbacin zata tsinta kanta a hakan yasa ban mata allurar ba tun ɗazu.”

Bai ce komai ba, sai dai ya gamsu da bayanin nata, dan haka ya kama Nimrah da kansa ya ɗagota sosai. Tana mutsu-mutsu da son ƙwacewa dai akai allurar. Kusan a tare shi da Doctor suka sauke ajiyar zuciya bayan wasu mintina ganin Nimrah ta fara nutsuwa. Sai dai shi a ciki yay tashi, doctor kuma a bayyane. Knocking ƙofar da akai ya saka Nurse da Doctor kallon wajen, sai kuma Nurse ɗin taje ta duba. Dabo ne ɗauke da kaya, bayan sun gaisa ya miƙa mata kayan, ya ɗauki sauran ya nufi ɗakin Imran.

Itama bayan ta ajiye kayan inda ya dace doctor ta bata umarnin gogema Nimrah jikinta dake sake ɗaukar zafi. Miƙewa Dada yay abinsa, dan tun da akai allurar ya kwantar da Nimrah gefensa yanzu ba'a jikinsa take ba. Sai da ya maida ƙofar ya rufe Nurse ɗin dake binsa da kallo ta ƙasan ido ta sauke ajiyar zuciya mai nauyi tana nufar Nimrah. Murmushi Doctor tayi, sai ma taji Nurse ɗin ta bata tausayi...

÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷

Wani wawan birki Malam Buba yaja yana waro idanun mamaki ganin wanda ke ƙoƙarin tsaida shi. Duk da ya rufe fuska da handkachiff ga p-cap hakan bai hana shi gane shi ba. Wuff Dagger ya buɗe motar kuwa ya shigo. Ya furzar da iska mai nauyi yana janye handkachiff ɗin daya rufe fuska da shi...

"Amma Oga wannan gangancine da mu duka zai iya sakamu a haɗari. Mizai sa kazo har nan anguwar, gari da haske kuma irin haka?".

Harara Dagger ya jefama Malam Buba kafin ya janye handkachiff ɗin da yake goge fuska yana gyara zama. "To faɗa min ya kake so nayi Mole? Tun randa ka kirani an ɗauke Nimrah ka sake nemana? Tsabar rashin mutunci ma waya ka kashe min gaba ɗaya. Jiya da shekaran jiya duk naje gidanka ance baka dawo ba. Sai da na kira Ari akan ya bincika min tunda na tabbatar bazai rasa huɗɗa da wani a gidan ba ya tabbatar min kana nan anan ma kake kwana. Mole mi kake nufi? Mi kake shiryawa? Ko Nimrah na hannunka?".

"Amma Oga wannan wace irin magana ce? Kasan dai duk wuya bazan ci amanarka ba, duk abinda zakaga nayi ina da dalili na, ko bakazo ba zan zo na kawo maka dukkan bayanai. Na farko dai kwana a gidan nima a gareni tilas ne, dan yarinyar nan Ruƙayya ce babu lafiya, sai kuma wajen jiyyarta ɗayar matar waɗannan ƙannen nasa ta faɗi akan ciki sai ta akai mata tiyata aka riro haririn. Hakan yasa inata kai kawo na jigilar kai abinci da abubuwa. Sannan wlhy hankalina ba'a kwance yake ba, ina nane da su ko zanji bayanin an sami Uwa dan har yanzu mutumin nan bai sake dawowa gidan ba daga shi har Imran...."

"Amma ba waya ya kamata ka kashe min ba, tunda nima ina buƙatar son jin abinda ke faruwa ko."

Received at 10:47 AM

3 people reacted with "Itama fa wayar ba kashewa nai ba oga. Wannan wawan Sanda ɗin ne ya ara ya shiga bayi saboda fitilar bayin ta lalace shine ya tsumbulata a ruwa, yanzu haka inda zan kai gyara nake nema".

"Mtsowww!".

Dagger yaja tsaki. Sai kuma ya miƙa masa hannu da faɗin, "Bani wayar."

Ba musu Malam Buba ya cirota ya bashi, Dagger ya ɗan jujjuyata a hannunsa sai kuma ya saka a aljihu. Wata ƙarama ya ciro ya bashi. "Ga wannan, daga yanzu na dinga sanin halin da ake ciki".

"Amma Oga ya batun Nimrah? Wlhy abin ya fara bani tsoro."

"Nima a tsoracen nake, dan itace rayuwata. Amma ina kan bibiyar iyayen yaron can da suka daka a makaranta satin daya gabata".

"Tsohon shugaban ƙasa fa naji ance".

"Eh su. Dan ina zarginsu gaskiya. Musamman matarsa bata da mutunci daman."

"To amma ta yaya Oga?".

Wata dariya Dagger ya kece da ita. Sannan ya ce, "Humm Mole har yanzu kanka a tukunya yake kai kam. Baka san waye Dagger ba a ƙasar nan. Kodan kai kana ganina arhar banza ne. To bara kaji, wannan damar ina baka ita ne saboda Nimrah. Za kuma ka iya samun fiye da hakan. Kai dai bari na aureta".

Harga ALLAH sai da ƙirjin Malam Buba ya jijjiga. Har ya kasa dannewa cikin suɓutar baki ya furta, "Aure Oga?".

"Eh mana, ko bazaka bani ba?".

Dagger ya faɗa cikin tsatstsareshi da idanu. Yawu mai kauri Malam Buba ya haɗiya, zuciyarsa kuwa wani irin dukan take yi. Cikin rawar baki ya ce, “Ba..b...ba haka nake nufi ba Oga. Kawai dai naga ita ƴa take a wajen ka”.

“A'a a wajenka dai, dan kai ka haifa. Ni masoyiya ce, kuma uwar ƴayƴana. Sai dai idan baka son bani”

Yawu mai ƙauri Malam Buba ya sake haɗewa. “Oga ai kaima mai aurama wani ce. Kawai dai kasan ance wannan mutumin yana au.....”

Cikin katseshi Dagger ya ce, “Oh kai harma ka ɗauki wannan auren aure? Shi jakin wace ƙasa ce zai aure ta babu iyayenta. Sannan ma wannan tsohon da aƙalla ma zai iya girmarka ne bakinka ke iya jinginawa da ƴarka. Jibeshi mutum a murɗe kamar ɗan damben turawa, dan ni banga abinda ya rage ba a zaman prison ɗin shiyyasa bamma yarda a can yake shekara takwas ba......”

Sam Malam Buba ba jin Dagger yake ba a yanzu. Dan tsakani da ALLAH hankalinsa ya tashi. Ai koda rayuwa ta maidashi haka baya fatan yarsa ɗaya tilo ta auri mutum irin Dagger da babu sbinda ya sani a rayuwarsa sai mugunta da kisan kai. Ga neman mata kamar ɗan bunsuru. Tabbas baya ƙaunar Zak-Shadow, kuma ko zai rasa ransa wannan auren bazai bari ya tabbata ba akan ƴarsa. Amma kuma bazai so Dagger ya maye gurbin Zak-Shadow ɗin ba a rayuwar Nimrah. Dole ne yayi wani motsi a wannan gaɓar, kuɗin nan da su Oga suka bashi gida zai nema ya saya a wata ƙasa cikin maƙwaftan ƙasashen nan, ya ɗauke ƴarsa ya maida can, ya sama mata ma'aikata masu kula da ita, ya biya mata ta cigaba da karatunta har ta samu miji irin wanda yake fata a gareta amma ba Dagger da Zak-Shadow ba.....

“Wai tunanin mi kake yi?”.

Dagger ya faɗa cikin tsawa-tsawa. Ajiyar zuciya Mole ya sauke yana girgiza kansa. “Ba komai Oga, babbar damuwata kawai ina ta shiga? Waye ya ɗauke ta? Saboda mi ya ɗauke tan?”.

“Karka damu zata dawo. Yanzu haka su Ayu nakan aikin nemanta. Bari naje yau inada meeting dasu oga aiki zai fara da zafinsa saboda kayan aiki sun iso, duk halin da ake ciki dai na dinga sani. Kaima kuma ka zama cikin shiri, idan ta kama kazo dole zaka zo”.

Kai Mole ya jinjina masa. Daga haka sukai sallama ya fita a motar anata kiran sallar magrib shi kuma yaja motar ya ƙarasa gida. Dan dama daga asibiti yake yakai abinci. Sai da ya dakata wata mota da Malam Almu ya buɗe ma gate ɗin ta fito sannan ya shige, har yay parking idanunsa akan Nabeeha dake komawa ɓangarenta da alama motar data fita baƙinta ne.....

°°°°°°°°°°°°°°

°°°°°°°°°°°°°°°

Kusan mintina ashirin Nurse ɗin ta ɗauka tana gogema Nimrah da barci ya ɗauka jiki. Ta canja mata kayan da aka sako marasa nauyi. Dan simple doguwar riga ce sai hula. Tana ƙoƙarin saka mata hular ne ta buɗe idanun ta da sukai jazur tana yamutsa fuska. Hannu takai ta dafe kan.

Received at 10:47 AmDan haka Nurse ɗin ta dakata daga saka mata hular tana tambayarta kanta na ciwo ne?. Kan ta jinjina mata tana lumshe idanu, a lokacin Dada ya sake dawowa ɗakin.

Tunda ya iso gaban gadon Nimrah ta buɗe idannunta a kansa, sai kuma tai narai-narai da su hawaye na taruwa a ciki. Cikin muryarta dake fita ƙasa sosai ta ce, “Dada kaina”.

Bai wani jita da ƙyau ba, sai dai a motsin lips ɗinta ya fahimci abinda take faɗa. Maimakon zama a kujerar gaban gadon sai ya zauna a bakin gadon kusa da ita sosai, bayan hannunsa ya kai saman goshin nata. A dai-dai lokacin Nurse ɗin ta fito daga bayi hannunta ɗauke da ƙaramar tasa da ruwa a ciki, sai towel ɗin data goge mata jiki data ɗaurayo. Cikin in-ina take sanar masa zata sake saka mata towel a kanta. Hannu kawai ya miƙa mata alamar ta bashi, ai ko da hanzarin ta ta matso towel ɗin

daga ruwan ta miƙa masa. Amsa yay batare daya kalleta ba, ya janye hannun Nimrah data riƙe kan ya ɗora towel ɗina. Sosai ta sauke ajiyar zuciya, tana mai ɗora hannunta akan nashi da yake ɗan daddana towel ɗin. Idanun su ne suka shige cikin na juna a hankali. Tai saurin janye nata tana rufesu. Shi ko ya cigaba da kallon fuskarta da tai fayau..........✍
Received at 10:47 AM

9

..........Ita dai Nurse nata kallonsu kamar ta samu television, sai in ya cire towel ɗin ya miƙa mata ta sake jiƙashi da ruwa ta matse ta miƙa masa. Sai da sukai haka sau kusan uku ya tabbatar zafin kan ma ya sauka sannan ya barta. Badan Nurse ɗin taso ba ta shige ta fita. Shi kuma ya fara ƙoƙarin haɗa tea. Sai da ya kammala a karo na farko yay mata magana. Idanunta dake rufe ta buɗe, sai kuma ta janye ganin ita yake kallo, ga hannunsa ɗaya ya miƙa mata alamar ta kama. (Sun ɗaura miki aure da wani a gidan tun kina 7years, sunyi hakan ne kuma dan cimma burinsu akan ki da mu. Babu shakka a yanzu kuma zasu fara aiwatar da bukatarsu a kanki. Sai ki lura, ki kuma fahimce su musamman shi tun kafin yay miki illa, ki yaƙe shi tun kafin ya karasa kassara mu ahalinki. Dan yana da wayo, bazai taɓa nuna miki saɓanin abinda yake so ki sani akansa ba. Mun baki assignment kuma ki nema sanin wanda suka aura miki idan kin koma.....) Waɗan nan zantukan ne keta dawo mata acikin kai. Ƙirjinta ya sake bugawa sakamakon dawowar hirar Dada Da Daddy Imran da taji kalmar aure suma a bakinsu. Mi hakan ke nufi? Wa aka aura ma ita ne? Waye mijin nata?. Bata da mai bata wannan amso shin a yanzu, dan haka ta zubama hannun nasa idanu har kusan mintina biyu. Ita bata kama ba, ita bata tashi bisa umarnin daya bata ba.

Dada dake kallonta cike da nazarin yanayin nata yay ɗan gyaran muryar data sakata yin firgigit, sai kuma ta sauke ajiyar zuciya mai nauyi tana risinar da idanun nata. Zuwa yanzu ta ɗan ji daɗin jikinta saboda goge matan da akayi, daddafawa tai ta tashi kawai batare data kama hannun nasa ba. Shima bai ce da ita komai ba ya miƙa mata tea ɗin kawai. Maimakon ta amsa sai ta fara magana cikin rawar murya...

"Dada! Dan ALLAH zan je wajen Mammah."

"Ni zan cinyeki ne anan?".

Yanda yay maganar kai tsaye yana danna waya ya sata saurin girgiza kai. Sai ga hawaye sharrr. Hannunta ɗaya takai tana sharewa. Hakan yasa shi ɗan dubanta, sai kuma ya janye idanun a lokaci guda. "Kisha ga magani da safe zaki je".

Kamar wadda bata gane yaren nasa ba ta ce, "Wajen Mammah ɗin?".

Yanzu kam gaba ɗaya ya ɗago yana kallonta sosai. Da sauri ta janye nata idanun data wara a kansa ta fara shan tea ɗin. Sai faman sauke ajiyar zuciya take a jajjare. Bata sake gigin kallon inda yake ba dan yaƙi ɗauke idanunsa a kanta harta shanye tea ɗin tas. Sai ga zufa na wanke mata jiki alamar ƙoshi...

"Zaki ci abincin?".

Da sauri ta girgiza masa kanta. Shima sai kawai ya jawo ledar maganin nata da robar ruwa. Duk yanda suka rubuta haka ya bata, tana gama sha ta zame zata kwanta...

"Tashi zaune".

Ya faɗa cikin umarni. Ba haka taso ba, amma bazata iya masa musu ba duk da itama dai kwanciyar ta isheta daman. Da kansa ya gyara mata filo ta jingina. Knocking ƙofar da akai ya saka Dada bada umarnin shigowa. Faro ne, dan haka Nimrah dake lullumshe idanu ta buɗe su da ƙyau tana gaishe shi. Ya amsa mata da kulawa yana tambayar jikinta. Tace masa da sauƙi. Hankalinsa ya maida kan Dada yana magana. Sai kawai Dadan ya miƙe alamar yafi son suyi maganar a waje. Dole Faro ya take masa baya suka fitan. Nimrah ta bisu da idanu abu na tsaya mata a maƙoshi. Dan taso maganar da Faro ɗin ya fara ayita a gabanta ƙwarai da gaske.

Amma yanda Dadan yayi sai maganar mutanen can ta sake samun gurbin tasiri a zuciyarta.

Fin mintuna talatin da fitar tasu, tun tana saƙe-saƙe har barci ya fara ɗibarta a hakan. Koda Dada ya dawo bataji motsinsa ba. Shima daya ƙaraso ya ɗan zuba mata idanu daga tsayen da yake, kafin ya duƙo kanta a nutsensa cikin rashin gaggawa ya fara gyara mata kwanciya. Ya rufa mata bargo zai janye jikinsa caraf ta riƙe hannunsa kawai ta juya kwanciyarta ta kwantar da fuskarta akan tafin. Da wani irin ƙarfi ta sauke ajiyar zuciya. Shi sai abin nata ma yaso bashi dariya. Amma sai ya gimtse yana kallon kyakkyawan fuskarta da hannun nasa. Kaɗan yay ƙoƙarin janye wa ta sake cikukukyesu ta matse har tsintsiyar hannun na kwanciya a ƙirjinta. Hakan ya saka shi kaiwa zaune dole.

Received at 10:47A ransa kam ayyanawa yake (Yarinyar nan tana da son tada zaune tsaye fa) a fili kam lips kawai ya ɗan damtse da haƙori. Vibration da wayarsa keyi ya tilasta masa buɗe idanunsa dake rufe. Dole yay amfani da hannunsa na haggu. Ganin Mammah ya sashi ɗagawa.

Yanda yay sallama muryarsa a ƙurya gashi tana shaƙewa ya saka Mammah faɗin, “Lafiya dai?”.

Gefen fuskar Nimrah ya ɗan zubama idanunsa da launinsu ya canja. Kamar Mammah na kallonsa ya girgiza kai kaɗan. “Ba komai Mammah. Har yanzu baki kwanta ba?”.

“Yanzu dai nake shirin kwanciyar. Ina fatan dai kunci abincin ko?”.

“Tasha tea tasha magani har tayi barci. Nima yanzu zanci. Dan ALLAH ki kwanta ki huta Mammah. In sha ALLAHU da safe da wuri zan kawo miki kayar ki”.

Murmurshi Mammah tayi har yana iya jiyo sautinsa. Ta ce, “To ALLAH ya tashe mu lafiya. Kadai ci abincin kaima. Sannan kai mata addu'ar barci, dan ALLAH kada kai nisa da ita wani ya sake sace min ita”.

Kaɗan ya rage yayi dariya. Ya dai daure ya murmusa kawai. Yana yanke kiran ƙasa-ƙasa ya furta, “Ni ai gashi nan tana neman sace ni idan ita wani bai sace miki ita ba Mammah.”

Tamkar Nimrah ta jishi ne, tai juya kwanciyarta zuwa rigingine. Har yanzu dai hannun nasa bata saki ba, sai ma gyara shi tai akan ƙirjinta ta rungume sosai kamar wadda ta samu filo. A yanzu kam ya fahimci dukan zai masa yawa. Dan an kai wani matsaya ne na ga mari ga tsinka jaka. Ba arziƙi yay dabarar janye hannunsa, zata warto ya warce abinsa yana miƙewa. Yafi ganewa ƴar nesa-nesa, in ba haka ba za'ayi ja ya faɗo ja ya ɗauka ne a asibitin mutane....

=============

Gaba ɗaya ran Nabeeha a dagule yake. Ta rasa inda zata tsoma ranta taji sanyi. Ga Ismat tayi tafiyarta saboda taji haushi ta bata shawara taƙi ɗauka. Ko yanzu datai ma wata ƙawarta rakiya da tazo wai tayata murnar dawowar Dada sai da ta sake tambayar maigadi yace ƴan gidan har yanzu suna asibiti babu wanda ya dawo.

Haka ta zauna ta zabga tagumi komai baya mata daɗi. Kewarsa take ji mai tsanani, so take ta ganshi cikin idanunta ta tabbatar gaskiya ne ya dawo. So take ta jita a cikin jikinsa kota samu nutsuwar shekara takwas da rabi data rasa. Amma sai ƙwalelen ɓoye kansa yake a gareta. Shin har yanzu yana fushi da ita ne? Miyasa bai nemeta ba? A tunaninta yana fitowa ita zai so fara gani duk duniyar nan. Amma sai taji saɓanin haka. Miyasa Haysam zai mata haka? Shifa ya mata laifi mai girma... Kiran daya shigo mata ne ya katse tunaninta. Ta sauke ajiyar zuciya tana ɗaukar wayar ganin Momy ce.

“Momy wlhy har yanzu fa bai dawo gidan ba. Suma kuma duk suna asibiti wai”.

Ta ɗan yi shiru alamar sauraren ɗayan ɓangaren.

“Ni gaskiya bana son zuwa asibitin, ai saina koma warin magani”.

“Shi ke nan naji Momy zanje goben”.

Bayan katsewar kiran ta harari wayar tana ƙunƙuni. Dan zuwa yanzu ta fara fahimtar akwai abinda Momy ke nema ne. Inba haka ba har itace ke mata faɗa akan ƴan uwan Haysam. Bayan da itace ke zugata ma akansu. Baki ta taɓe tana miƙewa ta wuce bedroom, dama a falo take.....

<%><%><%><%><%>

Barcinta yay nauyi sosai ta yanda yake jin saukar numfashinta na sauka a hankali. Dan haka ya sakama ƙofar key ya cire kayansa domin yin wanka. Dan gaba ɗaya a takure yake, kayan sun damesa ainun. A hakan ma ya canja su daga kakin da akai gumurzu a jejin can. Wanka ya fara gabatarwa yayo alwala. Koda ya fito jallabiyar da Dabo ya sayo masa ya saka, yay shafa'i da wutri sannan yay zaman shan tea da abinci kaɗan dan yunwa yake ji sosai. Duk da yanda ya cisa kaɗan sai da yaji ya takura, dan shi ƙa'idarsa baya wuce 8 na dare baici abinci ba. Amma gashi yau har kusan 12 ma ake magana. Yanayin takurar da abincin yay masa ya sashi buɗe ɗakin ya fita, ɗakin Imran ya leƙa, shima barci yake akwai kuma Yusuf a tare da shi. Sai kawai ya dawo wajen Nimrah. A cikin ɗakin ya gabatar da push-up da shi kansa bai san adadi ba, dan mintina kawai ya saita, suna cika ya miƙe yana sauke numfashi, a kujera ya zauna yasha ruwa, sannan ya kwantar da jikinsa ya lumshe idanunsa.
Received at 10:47Sai da jikinsa ya daidaita ya ɗauka laptop ya fara sana'ar tasa, duk da dai akan aiki ne...

Kusan 1:am Nimrah ta farka a firgice har tana neman faɗowa a gado. Cikin zafin nama ya miƙe ya tareta, gaba ɗaya zufa ta jiƙeta, ga jikinta na rawa tana sambatu. Dole ya sakata a jikinsa ya rungume ta ya fara mata addu'a. Ƙafafunsa ne suka fara dayi, dole ya zame ya zauna a gadon jiyyar tata, har lokacin kuma tana a jikinsa. Ƙoƙarin kwantar da ita yay amma ta ƙanƙamesa har tana ƙunƙunin kuka a cikin barci. Babu yanda ya iya dole ya barta, sai ma zama daya gyara ya sakata a tsakanin ƙafafunsa shi kuma ya jingina da filo. Kanta na saman jikinsa ta zagaye cikinsa da hannayensa duk biyu. Hakan yasa numfashinsa ke sauka a saman cikinsa..........✍
Received at 10:47 AM
[14/02, 9:15 am] Abue Saleh: 10

........Iska yaɗan furzar kawai ya ɗauki laptop ɗinsa ya cigaba da aikinsa. Shima zuwa 1:47am idanunsa suka fara yajin barci. Dole ya rufe Laptop ɗin ya zama a hankali ya kwanta a gadon duk da ya musu kaɗan, sai dai ya tabbatar yace zai tashi wata sabuwar futinarce kuma. Dan shi kam lamarin Nimrah da rigimarta sun fara fin ƙarfinsa. Aiko kamar abinda take jira kenan. Mutuniyar ku sai aka sake gyara kwanciya a jikin Dada ɗare-ɗare.

Addu'a yayta ambata duk wadda tazo bakinsa. Har ALLAH ya taimaka tarzomar dake neman turniƙewa ta lafa cikin amincin ALLAH, daga haka shima barcin yay gaba dashi saboda yana jinsa sosai. Kiran sallar farko ya farka, baya buƙatar farkawarta taga a yanda suke kwance, dan haka cikin dabara ya zameta a jikinsa ya kwantar da ita a tsakiyar gadon yana gyara mata blanket shi kuma ya sauka. Duk yanda yaso tashi kasawa yay, sai da ya jinkirta zaune a bakin gadon hannunsa ɗaya dafe da kansa, ɗayan riƙe da cikinsa daya ƙulle masa tamau, ya ja mintuna a haka har ya ɗan sarara sannan ya miƙe zuwa bayi. Bayan wasu mintina ya fito yana goge kansa zuwa wuya alamar jiƙashi yayi, dan jallabiyar jikinsa ma ta nuna hakan kasancewarta coffee color. Sauri-sauri ya ƙarasa kimtsawa ya tafi masallacin cikin asibitin....

Kan Nimrah neman tarwatsewa yayi da mamakin ganin alamar fa Dada a ɗakin ya kwana. Duk da sai da ya dawo salla massalaci ya tashe ta. Daga yanda take zaune a bakin gado ta zubama ƙasan farar jallabiyar jikinsa idanu. Dan ba itace a jikinsa jiya da daddare ba.

Gyaran muryar da yay ya saka ta ɗagowa gaba ɗaya ta kallesa. Sai kuma tai saurin kauda idanun nata dan shima ita yake kallo. Miƙewa tai kamar wadda ƙwai ya fashe ma a ciki ta nufi toilet dake a cikin ɗakin. Dan ɗaki ne guda da gado guda biyu kacal, komai na buƙata akwai a cikinsa har fright. Abinda ya bata mamaki ɗayan gadon babu alamar an kwanta akai, shiyyasa taketa wasiwasin a ina to ya kwana shi? Badai a zaune a kujerar nan ba?. Bata da mai bata wannan amsar, dan haka ta fito a bayin, daga inda take ta ɗan ɗago ido ta saci kallonsa, tana ganin zai ɗago tai saurin maidawa gefe.

Shima dake binta da kallo ta gefen ido janyewa yay ya maida kan Alkur'anin hannunsa. Bata wani jimaba ta fito, sallayar data gani shimfiɗe alamar shi yay amfani da ita ta hau bayan ta ɗauki hijjab data gani ta saka. Koda ta idar sai da tayi har azkar sannan ta miƙe a wajen. Sum-sum ta iso inda yake, kanta a ƙasa takai duƙe a ƙasa kusa da shi tana faman cuɗa yatsunta cikin juna.

"Dada ina kwana".

Idanunsa ya ɗago a slowly daga kan Alkur'anin ya zuba mata su, cike da nazarinta yake kallon hannun da take cuɗawa cikin juna. Ita kuma jin shiru bai amsa ba ta sake maimaita gaisuwar tana ɗagowa da nufin satar kallonsa sai suka haɗa ido. Rasama ya zatai tayi sai kawai ta tura baki gaba.

Ɗan motsi lips ɗinsa sukai kamar mai shirin yin murmushi. Sai dai baiyi ɗin ba. Alkur'anin ya rufe ya ajiye a drawer gefen gadon jiyyar tata. Babu zato kawai taga ya miƙa mata hannunsa dake fari tas, ga faratan a gyare sai sheƙi suke fes-fes da su. Nata hannun ta kalla, sai kuma ta sake kallon nashi tana ƙoƙarin noƙe nata..

"Baƙya son mu samu ladan musabaha Kiddo?".

Wani irin yuuuu Nimrah taji tun daga yatsan ƙafarta har tsakiyar kanta sakamakon yanda Dadan yay magana muryarsa a shaƙe, gashi ƙasan maƙoshi kamar mai raɗa. Ya kuma kamo hannun nata cikin nasan harda ɗan matsawa yanda ya sata dole ɗagowa ta kallesa. Shima kallon nata yake da wani irin yanayi data kasa fassarawa, ya kuma riƙe idanun nata cikin nasa ta kasa janye wa.

Ruwa idanun nata suka fara tarawa, har yana iya ganin ƙyallinsu. Lips ɗinta na rawa kamar zata fashe masa da kuka ta ce, "Dadahhhh".

Idanun nasa ya janye daga cikin nata. Sai kuma ya janye hannun batare daya amsa kiran da tai masan ba ya koma cikin kujerar da ƙyau ya gyara zamansa. Sai da ya tabbatar abinda ke masa kai-kawo a maƙoshi ya koma ya kwanta sannan yay magana cikin dakewa.

Received at 10:47 AM

[14/02, 9:15 am] Abue Saleh: "Yaya jikin naki?".

Sharrr hawayen da ita kanta bata san na miye ba suka zubo mata. A haka ta furta, "Na warke".

Kallonta yay da mamaki. Ganin kuka fa take bil-haƙƙi abinta. Sai kawai yakai hannu ya shafa kwantaccen gashin fuskarsa. Itama dai-dai tana miƙewa zata bar wajen. Hannunta ya riƙo kawai ya dawo da ita, sai dai yanzu tana daga tsaye ne tana sharɓar hawaye taƙi kallonsa.

"Negar! bana son kukan banza fa. Ko kina son bugu ne?".

Kafaɗa ta maƙe masa tana ƙara matso hawayen.

"Wani guri na miki ciwo ne?".

Nan ma kafaɗar ta noƙe. Jimm yay yana kallonta, sai kuma ya sake faɗin,

"Mi kike so?".

Yay maganar yana matso da ita sosai jikinsa ta sake duƙawa cike da lallashi, har tana ɗora hannunta saman cinyarsa bata farga ba.

Cikin rawar murya tace, "Ina jin tsoro".

Wani irin motsawa zuciyarsa tayi, ya dai dake ya furta,

"Tsoro dai? Na miye?".

Kuka ta sake fashe masa da shi taƙi magana. Sai kawai ya miƙe itama ya miƙar da ita ya sakata a jikinsa ya rungume. Daburcewa tai gaba ɗaya, dan abin yazo mata a

bazata. Kodan jiya ba cikin hankalinta take ba duk bata san mita dinga masa ba da yanda shima yayta rungumeta.

"Kar kiji tsoro Kiddo. Matsoraci baya zama gwani. Kiyi addu'a, amma miyasa kike jin tsoro? Sun miki wani abu ne?".

Kanta dake kwance a jikinsa ta girgiza.

Ɗagota yay ya zaunar a bakin gadon, ya matso kujerar sa kusa da ita sosai har jikinta na gogar nashi, dan ƙafafunta ma tsakiyar nashi ƙafafun daya ɗan wara suke. Idanunsa a kanta, hannayensa cikin nata ya ce, "Faɗa min tsoron mi kike ji?".

Ta kasa danne abin, dan ya tsaya mata a rai matuƙa har zuciyarta da ƙwaƙwalwa sun kasa ɗauka kamar sauran abubuwan. Tana kuka sosai ta ce, "Dada sun ce an min aure. Da wani mutumi".

Wani irin Bimmmb!! Yaji zuciyarsa ta bada sauti. Ya danne da ƙyar yace, "To shine abin kuka Kiddo. Dama duk mace dole tai aure ai ko?. Kuma kema ai kin girma."

"Dada ni dai zan zauna wajen Mammah ta. Ban girma ba. Ba'aina Small Mom aure ba da su Uncle Billa sai ni".

Murmushi yayi kaɗan a ransa yace (Kiddo ki illatani har duniya tasan halin da nake ciki kawai ki huta). A zahiri kam ɗan gyaran murya yay da faɗin, "A'a Kiddo, zama wajen Mammah kam na lokaci ne. Sai dai randa na aurar daku halan da Mammah zaki tafi?".

Jin abinda ya faɗa ya sata kallonsa, ganin ita yake kallo tai saurin janye wa tana shagwaɓe fuska da faɗin, "Ni bazan yi auren ba fa kwata-kwata bana so Dada?".

Idanunsa ya ɗan waro waje shima kamar yanda ta waro masa nata a furucin ƙarshe.

"Kice malam gari su fara addu'a, Kiddo bata san aure ai asirin Dada ya gama tonuwa".

Kunya ce taji ta kamata a karo na farko, duk da dai dama dakewa kawai take tun ɗazun, dan maganar ta mata nauyi, amma tana son ta amayar ko zataji sauƙin nauyin da ƙirjinta yayi saboda girman ta a ranta. Tasa ɗayan hannuta ta rufe idannunta tana haɗiye ƙwallar da suka sake cika mata ido. Shima da yanayin ya fara masa tasiri sai ya gyara zama yana ɗan matsa hannunta da har yanzu ke riƙe a cikin nashi.

"Uhmmm faɗa min miyyasa. Kinga idan naji dalilin ki mai ƙarfi ne sai nima na yarda bazan miki auren ba. Kawai muyi zaman mu muna cin tuwon Mammah kullum".

"Ai banda kai. Tunda kana da mata".

Ɗan tsai yay yana kallonta cike da nazari. Sai kuma ya basar da faɗin, "Waya gaya miki?".

"Na sani ai. Ba itace ta taɓa yankamu ba, ga tabon a cinya na ma. Ranar ma kuma ta dawo sunyi jere a part ɗinka itada masu kama da karuwan nan." takai ƙarshen maganar tana yaye rigar jikinta cinyarta ta bayyana. Da sauri ya haɗiye yawun dake neman sarƙe shi, ya ɗan zubama tabon da ya zama dogo sosai idanunsa da suke rinewa, ga yanda fatar jikinta ke wani sheƙi da kwanciyar ɗaukar idanun mai kallo ya saka tsigar jikinsa tashi. Yanda yanayinsa ke canjawa yasa shi kai hannu da kansa yaja rigar ya maida mata.

Received at 10:47 AM

[14/02, 9:15 am] Abue Saleh: Cikin rashin damuwa ta gyara zama da faɗin, "Dada kaga nasan kana da mata ko?".

A ransa yace (Wata sabuwa, wannan ficikar fa da wayonta) a zahiri kam sai ya basar ta hanyar faɗin, "Shike nan ke faɗa min miyyasa baƙya son kiyi?".

"Saboda bana son na bar Mammah da su Uncle's, da Ruky. Da Daddy, da su Ammie. Nafi son muyita zaman mu a haka lullum-kullum muna jin daɗin mu, muna hira. Dada ƙarya suke ai ba'a min aure ba ko?".

Ji yay kamar ya kwashe da dariya saboda yanda tai tambayar cikin marairaicewa, amma ya gimtse abarsa “Uhmm ƙila da gaske suke yi dai, amma miyasa baki tambaye su waye mijin ba to tun acan?”.

Baki ta sake turawa. “Wai sunce assignment ne naje na bincika kai ko Mammah zaku faɗa min”.

Maimakon ya bata amsar sai ya waske da faɗin, “To amma ai naga kina son yara sosai. Kuma sai anyi aure ake haifar yara ai ko, yaya zakiyi kenan?”.

Yanzu kam har cikin ranta ta ce, “Dada baga su Afrah ba. Kuma su Ammy suna ƙara haifo mana wasu, ai sun ishe mu mu duka.”

“Duk da haka kema zamu so ni da Mammah da Uncles ɗinki muga naki ai”.

“To kawai basai na haife su a haka ba?”.

“Babu auren?”.

Ya faɗa cikin ɗan waro idanu. Kawai sai abin ya bama Nimrah dariya, ta shiga ƙyalƙyalawa. Shi kuma ya shagala kawai yana kallonta. A ranta ko rayawa take (Dada fa kallon ƴar yaye yake min ko? Bari muje a hakan to). Sai da tai dariyarta sosai sannan ta jinjina masa kai. Kai tsaye ta ce, “Eh, ai ko bakai aure ba idan malamai suka maka addu'a sai kawai kaga ka samu Baby”.

Samun kansa yay da tsareta da idanu kawai. A ransa yace (Zakiga malamai kuwa yarinya, harda ma masu addu'ar saukar aljanu nan kusa kaɗan).........✍

🙏🙏Zamu so ganin malam saukar aljanun nan kuwa Dada🙈🙈.

Received at 10:47

[14/02, 9:17 am] Abue Saleh: “Yaya jikin naki?”.

Sharrr hawayen da ita kanta bata san na miye ba suka zubo mata. A haka ta furta, “Na warke”.

Kallonta yay da mamaki. Ganin kuka fa take bil-haƙƙi abinta. Sai kawai yakai hannu ya shafa kwantaccen gashin fuskarsa. Itama dai-dai tana miƙewa zata bar wajen. Hannunta ya riƙo kawai ya dawo da ita, sai dai yanzu tana daga tsaye ne tana sharɓar hawaye taƙi kallonsa.

“Negar! bana son kukan banza fa. Ko kina son bugu ne?”.

Kafaɗa ta maƙe masa tana ƙara matso hawayen.

“Wani guri na miki ciwo ne?”.

Nan ma kafaɗar ta noƙe. Jimm yay yana kallonta, sai kuma ya sake faɗin,

“Mi kike so?”.

Yay maganar yana matso da ita sosai jikinsa ta sake duƙawa cike da lallashi, har tana ɗora hannunta saman cinyarsa bata farga ba.

Cikin rawar murya tace, “Ina jin tsoro”.

Wani irin motsawa zuciyarsa tayi, ya dai dake ya furta,

“Tsoro dai? Na miye?”.

Kuka ta sake fashe masa da shi taƙi magana. Sai kawai ya miƙe itama ya miƙar da ita ya sakata a jikinsa ya rungume. Daburcewa tai gaba ɗaya, dan abin yazo mata a bazata. Kodan jiya ba cikin hankalinta take ba duk bata san mita dinga masa ba da yanda shima yayta rungumeta.

“Kar kiji tsoro Kiddo. Matsoraci baya zama gwani. Kiyi addu'a, amma miyasa kike jin tsoro? Sun miki wani abu ne?”.

Kanta dake kwance a jikinsa ta girgiza.

Ɗagota yay ya zaunar a bakin gadon, ya matso kujerar sa kusa da ita sosai har jikinta na gogar nashi, dan ƙafafunta ma tsakiyar nashi ƙafafun daya ɗan wara suke. Idanunsa a kanta, hannayensa cikin nata ya ce, “Faɗa min tsoron mi kike ji?”.

Ta kasa danne abin, dan ya tsaya mata a rai matuƙa har zuciyarta da ƙwaƙwalwa sun kasa ɗauka kamar sauran abubuwan. Tana kuka sosai ta ce, “Dada sun ce an min aure. Da wani mutumi”.

Wani irin Bimmmb!! Yaji zuciyarsa ta bada sauti. Ya danne da ƙyar yace, “To shine abin kuka Kiddo. Dama duk mace dole tai aure ai ko?. Kuma kema ai kin girma.”

“Dada ni dai zan zauna wajen Mammah ta. Ban girma ba. Ba'aina Small Mom aure ba da su Uncle Billa sai ni”.

Murmushi yayi kaɗan a ransa yace (Kiddo ki illatani har duniya tasan halin da nake ciki kawai ki huta). A zahiri kam ɗan gyaran murya yay da faɗin, “A'a Kiddo, zama wajen Mammah kam na lokaci ne. Sai dai randa na aurar daku halan da Mammah zaki tafi?”.

Jin abinda ya faɗa ya sata kallonsa, ganin ita yake kallo tai saurin janye wa tana shagwaɓe fuska da faɗin, “Ni bazan yi auren ba fa kwata-kwata bana so Dada?”.

Idanunsa ya ɗan waro waje shima kamar yanda ta waro masa nata a furucin ƙarshe.

“Kice malam gari su fara addu'a, Kiddo bata san aure ai asirin Dada ya gama tonuwa”.

Kunya ce taji ta kamata a karo na farko, duk da dai dama dakewa kawai take tun ɗazun, dan maganar ta mata nauyi, amma tana son ta amayar ko zataji sauƙin nauyin da ƙirjinta yayi saboda girman ta a ranta. Tasa ɗayan hannuta ta rufe idannunta tana haɗiye ƙwallar da suka sake cika mata ido. Shima da yanayin ya fara masa tasiri sai ya gyara zama yana ɗan matsa hannunta da har yanzu ke riƙe a cikin nashi.

“Uhmmm faɗa min miyyasa. Kinga idan naji dalilin ki mai ƙarfi ne sai nima na yarda bazan miki auren ba. Kawai muyi zaman mu muna cin tuwon Mammah kullum”.

“Ai banda kai. Tunda kana da mata”.

Ɗan tsai yay yana kallonta cike da nazari. Sai kuma ya basar da faɗin, “Waya gaya miki?”.

“Na sani ai. Ba itace ta taɓa yankamu ba, ga tabon a cinya na ma. Ranar ma kuma ta dawo sunyi jere a part ɗinka itada masu kama da karuwan nan.” takai ƙarshen maganar tana yaye rigar jikinta cinyarta ta bayyana. Da sauri ya haɗiye yawun dake neman sarƙe shi, ya ɗan zubama tabon da ya zama dogo sosai idanunsa da suke rinewa, ga yanda fatar jikinta ke wani sheƙi da kwanciyar ɗaukar idanun mai kallo ya saka tsigar jikinsa tashi. Yanda yanayinsa ke canjawa yasa shi kai hannu da kansa yaja rigar ya maida mata.

Received at 10:47 AM

[14/02, 9:17 am] Abue Saleh: Cikin rashin damuwa ta gyara zama da faɗin, “Dada kaga nasan kana da mata ko?”.

A ransa yace (Wata sabuwa, wannan ficikar fa da wayonta) a zahiri kam sai ya basar ta hanyar faɗin, “Shike nan ke faɗa min miyyasa baƙya son kiyi?”.

“Saboda bana son na bar Mammah da su Uncle's, da Ruky. Da Daddy, da su Ammie. Nafi son muyita zaman mu a haka lullum-kullum muna jin daɗin mu, muna hira. Dada ƙarya suke ai ba'a min aure ba ko?”.

Ji yay kamar ya kwashe da dariya saboda yanda tai tambayar cikin marairaicewa, amma ya gimtse abarsa “Uhmm ƙila da gaske suke yi dai, amma miyasa baki tambaye su waye mijin ba to tun acan?”.

Baki ta sake turawa. “Wai sunce assignment ne naje na bincika kai ko Mammah zaku faɗa min”.

Maimakon ya bata amsar sai ya waske da faɗin, “To amma ai naga kina son yara sosai. Kuma sai anyi aure ake haifar yara ai ko, yaya zakiyi kenan?”.

Yanzu kam har cikin ranta ta ce, “Dada baga su Afrah ba. Kuma su Ammy suna ƙara haifo mana wasu, ai sun ishe mu mu duka.”

“Duk da haka kema zamu so ni da Mammah da Uncles ɗinki muga naki ai”.

“To kawai basai na haife su a haka ba?”.

“Babu auren?”.

Ya faɗa cikin ɗan waro idanu. Kawai sai abin ya bama Nimrah dariya, ta shiga ƙyalƙyalawa. Shi kuma ya shagala kawai yana kallonta. A ranta ko rayawa take (Dada fa kallon ƴar yaye yake min ko? Bari muje a hakan to). Sai da tai dariyarta sosai sannan ta jinjina masa kai. Kai tsaye ta ce, "Eh, ai ko bakai aure ba idan malamai suka maka addu'a sai kawai kaga ka samu Baby".

Samun kansa yay da tsareta da idanu kawai. A ransa yace (Zakiga malamai kuwa yarinya, harda ma masu addu'ar saukar aljanu nan kusa kaɗan).........✍

Zamu so ganin malam saukar aljanun nan kuwa Dada.
[16/02, 10:58 pm] null: KIƊA A RUWA 3

11

........."Amma mutanen nan ƴan iska ne Haysam. To taya ma suka san ka auri Nimrah? Nifa abin nan na bani mamaki".

Dada dake zaune a kujerar kusa da gadon jiyyar Daddy Imran ɗin yaɗan furzar da iska yana jan ƙaramin tsoki.

"Imran ba abin mamaki bane dan nasan mutanen nan dama dole suna zagaye damu. Kawai yanda suka gaya mata wannan zancen ne sai na fahimci akwai manufa, akwai kuma abinda suke son isarwa ga yarinyar musamman da suka ce taje ta bincika mijin da kanta..."

"Tabbas nima na fahimci hakan, tunda kaga harta kasa riƙewa ta faɗa maka. Indai haka ne to ya kamata mu zauna da ita a mata bayani. Dan a yanzu ni kaina banga amfanin cigaba da ɓoye mata kai mijinta bane. Sannan dolene fa ta koma kusa da kai gaskiya....."

"Imraaan!".

"Haysamm!".

Shima ya tari numfashinsa. Sai kawai suka zubama juna idanu. Babu wasa sam a idanun Daddy Imran ya cigaba da faɗin, "Wai mi kake shakku ne? A tunaninka Nimrah bata san komai bane? Kana ganin lafiya-lafiya idan tana hannun iyayenta ne zuwa yanzu basu jima da mata aure ba, maybe ma ta haihu to wlhy. Balle yanzu da a cikin birni take tana samun abinci mai ƙyau. Ni bance dole sai ka kasance da ita ba, amma ta zama kana sanin duk motsinta tunda har mutanen nan suka fara da wannan salon. Sannan karka manta Nabeeha ma ta dawo gidan a yanzu. Ita kanta idan taga kana cigaba da ɗaukar Nimrah yarinya har yanzu zata tsiro maka da wasu fitinu ne. Amma idan ta tabbatar da fa da gaske kake shike nan sai kowa tai yaƙin kanta. Kaifa kake gaya min yanzu Nimrah ta gama faɗa maka tasan kana da mata, harma bata manta ta yanke ta ba. To kasan waye Nimrah kuwa a rashin ji? Har yanzu ƙananun ayyukansu kake gani wlhy, amma tunda har bata manta wannan batun yankan ba ni nake faɗa maka sai tayi wani abu....."

Yanda Dada ke masa kallon mamaki yasa shi yin ƴar dariya.

"Hummm sa wasa, kai dai ka saka ido kawai a kanta. Amma kasan ALLAH Nimrah Zakanya ce ta gaske. Kawai sauƙin abun tana shakkarka ne tunda baƙo kake a idanunta har yanzu. Amma ka ma shirya, dan in dai tsoro ne Nimrah bata san wani abu wai shi tsoro ba".

Hararasa Dada yayi da faɗin, "Duk baku kuka ɗaure mata take yi ba. Yanzu haka idan ta sakani gaba da fitina rasa ma abin yi nake yi. Ina ga ta dawo kusa dani, ai wannan aikin ma bazai yiwu ba, dan bazan iya haɗa rikicinta da aikina ba gaskiya. Kana maganar ta girma, to yanzu take cemin ai idan malamai sukai addu'a ko ba'ai aure ba ana samun Baby, ina hankali anan Imran?".

Duk yanda Daddy Imran yaso gimtse dariyarsa ya kasa, sai da yayi mai isarsa.

Sai kawai Dadan ya kuma zuba masa harara. "To miye abin dariya anan kuma?".

“To kai miye na tsarguwar? Ko kaji nace wani abu?. Tunda dai in malamai sukai addu'a ana samun Babyn kai ba sai ka zama Malamin nata ba. Miye abin wahala a ciki ba koyar da karatu bane kawai ta fahimci baƙaƙe da wasilla”.

“Wlhy kaji kunya uban banza”. Dada ya faɗa yana miƙewa ya nufi hanyar fita. Shima Imran miƙewar yayi yana ƙyalƙyala dariya dan an sallamesu har Nimrah ɗin ma. Duk da bakwai sun zama normal bane gaba ɗaya musamman ma shi mai rauni akai. Kawai dai zaman asibitin ne bashi yiwuwa a wannan gaɓar.....

©©©©©©©©©

A ɓangaren shugaban ƙasa Yusuf Shu'aibu Tafida ƴan jam'iyya sun bala'in saka rayuwarsa gaba ta ƙarƙashin ƙasa akan naɗin muƙamai. Dan tun suna ƴar percentage har sun fito masa ƙuru-ƙuru da sunayen waɗan da suke buƙatar a bana manyan muƙamai. Hankalinsa ya tashi, duk da kuwa wanda suka kawo ɗin shi bazai ce suna da wani baƙin hali na zahiri bane. Amma a muƙaman da suka riƙe a baya a bayyane take su masu rauni ne ga sauke haƙƙokin talakawa. Babu abinda suke yi sai raya kansu da iyalansu da dukiyar ƙasar. Shiyyasa babu wani ayyukan cigaba na zahiri da suka fito daga yankunan su a sanda suke mulki na shugabanci ko na wani office da suka riƙe.

Received at 12:22 PMReactions: Rasa wazai tunkara yay shawara yayi. Gashi kwanaki uku kacal suka bashi. Yau hatta office yaƙi fita da wuri har kusan sha ɗaya. Wani gefe na zuciyarsa keta kawo masa Zak-Shadow da Imran. Kuma tabbas yana jin gamsuwa da yaran. Dan wannan rikitaccen mulkin baya yiwuwa sai da ɓoyayyun mashawarta. Wlhy badan fidda Haysam da yayi ba da yace shi wannan mulki baiga amfaninsa ba, dan rikicin cikinsa da kitumurmura sun wuce tunanin mai tunani. Wanda ke waje shike kallon shugaban ƙasa a mai zartarwa sama da kowa. Amma a zahiri hotone kawai a kujerar mulki shugabancin ƙasar nan. Ainihin masu mulkar ƙasar suna gefe ne kawai suna busa sigari kalar wadda suke buƙata. Sai abinda suke so, sai abinda sukace dole za'ayi, idan kace zaka bijire su ƙasƙantar da kai a idon talakawan ƙasar a bayyane, a ɓoye su raunana lafiyarka da kuzarinka. Duk mai baka goyen baya su siyesa da kuɗi, idan yaƙi bi shima su ɓatar da shi ko su tsigesa a kusa da kai ɗin. Wannan itace zahirin ƙasar da talaka bai sani ba, wata shari'ar dai sai anje can kawai.

Wayarsa ya ɗauka da mutane masu muhimmanci ne kawai a ciki yay gajeren text ya tura. Daga haka ya miƙe domin shirin fita office.....

°°°°°°°°°°°°°°°°°°°°

Saƙon shugaban ƙasa ya shigo wayar Dada ne a dai-dai lokacin da motar su ke hawa kan babban titi bayan fitowarsu a cikin asibiti. Dabo ne ke driving ɗin, gefensa Imran. A baya Nimrah sai Dada dake ta aiki da laptop a kusa da ita. Tana lafe ne jikin ƙofa idanunta a lumshe, ji take kamar tai tsuntsuwa ta ganta a gida saboda ɗoki. Duk da dai akwai ajiyayyar damuwa dake danƙare da zuciyarta da brain ɗinta. Amma kamar yanda tai alƙawari zata bi komai a sannu kamar yanda ta fara. Dan a yau ta sake fahimtar gane ainahin Dada ba abune mai sauƙi ba. Dole ta dake, dole ta shirya, dole ta jajirce, dole ta ƙara wayo da taka tsantsan. Sai dai duk da haka maganar auren nan na ɗaga mata hankali. Tana son taji tabbaci a bakin Mammah da sauran Uncles ɗinta da Daddy Imran. Harga ALLAH indai da auren nan batama san yanda zata fassara shiga ukun da take ciki ba. Waye wannan miji? Tana son ta sanshi, ta ƙagara ta sanshi.

Duk halin da take ciki Dada na lure da ita. Dan yanda take yamutsa fuska, ta cije lips, ta matse idanu yasa shi fahimtar akwai abinda take tattaunawa da zuciyarta. Kuma ko minene yana da girma da rikitarwa a gareta. A lokacin da yake ajiye wayarsa dake tsakkiyarsu bayan kammala karanta saƙon Mr President sai yaga tasa hijjab ta share hawaye. Hakan ya sake tabbatar masa da zarginsa. Baiyi magana ba

ya cigaba da aikinsa yana sauraren tattaunawar Imran da Dabo akan Ojo da suke ƙoƙarin gano inda yake yanzun...

Gidan Daddy Imran suka fara zuwa domin sauke shi. Nimrah nason shiga taga Ammie tana kuma zumuɗin zuwa taga Mammah. Sai kawai ta saka a ranta tunda weekend za'a shiga zasu zo ita da Ruky. Isowar su gate ɗin nasu gidan sai taji ƙaguwar a buɗe, dan badan Dada bane a motar da tuni ta ɓalle murfin ta shiga da gudu. Amma jikinta sai tsuma yake ta yanda har shi ma ya gane. Aiko Dabo na tsayar da motar ta buɗe ta fice dan haƙurinta yakai maƙura. Dada ya bita da kallo kawai, dan kamar ƙyatawar ido har taje ƙofar falo.

Kansa ya ɗan girgiza yana miƙama Dabo daya buɗe inda yake laptop ɗin daya rufe. Daga haka ya sakko ƙafafunsa ya fito gaba ɗaya. Sauran kayan Dabo ya tattauro, dai-dai kuma isowar maigadi da malam Buba dake noƙewa a baya wajen. Cikin girmamawa suka fara gaida Dadan. Dada ya janye idanunsa daga kallon da yay ma malam Buba na seconds, kafin ya amsa gaisuwar tasu. Suka ɗora da nuna farin cikin dawowar Nimrah, sunata ambaton godiyar ALLAH. Shi dai wajen yay ƙoƙarin bari. Amma sai maigadi ya miƙo masa abinda ke hannunsa yana faɗin, “Af naso na manta. Ranka ya daɗe dama ga saƙo yanzun nan babu jimawa wani ya kawo shi a baka. Dan zanje nakai ciki ne ma kuka iso na dakata buɗe muku ƙofa.”
Received at 12:22 PM
reacted with ❤ Idanu Dada ya ɗan zubama hannun maigadi, sai kuma ya miƙa hannu ya amsa batare da yace komai ba. Yana barin wajen Malam Buba ya sauke ajiyar zuciya mai nauyi da har sai da maigadi ya kallesa. Kamar zai yi magana sai kuma yay shiru suka koma bakin gate. Sanda da ya shige ɗaki wufff tun buɗe gate da akai ya fito shima sum-sum yana leƙa hanyar sashen Mammah da har Dada ya shige....

Yanda Dada ya samu falon ya kacame da murnar ganin Nimrah sai yama tsaya kawai yana kallonsu. Dan Ruƙayya na rungume da ita tana kuka ana lallashinsu. Su duka biyun suna jikin Mammah. Mu'azz ma sai sharar hawaye akeyi na farin ciki. Shigowarsa tasa su Bilal dake zagaye da su maido hankalinsu kansa. Sai kuma duk suka zaburo cike da farin cikin ganinsa suma. Mammah kanta yau ta kasa dannewa kallonsa take farin cikinta a bayyane. Gwaggo Alawiyya tazo ta kama hannunsa tana faɗin, “Sannu kaji Haysam, ALLAH yay maka albarka. Maza zo ka zauna ansha fama kwana biyu”.

Murmushi kawai yayi yana kaiwa zaune. Ya gaida Mammah sannan su Gwaggo Khadijah. Suma su Ja'afar suka gaisheshi. Kafin wani lokaci Aunty Mimi ta kawo masa ruwa. Dan suma duk suna gidan daga asibiti suke duba Lailah. Mammah tasan duk yanda suke son jin yanda aka samo Nimrah bazai faɗa ba, dan haka ta tambayesa a shirya masa abinci ne. Miƙewa yay yana amsa mata da zai yi wanka tukunna. Ya ɗan kalli Nimrah da Ruƙayya ke bama abinci a baki itama yana bata ya wuce abinsa. Dai-dai Ammar na sakkowa daga kai kayansa ɗaki da Dabo ya kawo. Umarnin kawo masa coffee ya bashi yana wucewa...........✍


********************* ⬇ *************************

********** Ai Hausa Novels ****************

************************ ⬆ *********************

DOWNLOAD More complete Hausa Novels, Education Books, Adventure, Drama, Mystery, Religion, Fiction, Non-Fiction, Romance, Meimor, True Life Stories & Others from our blog.

Visit > https://www.aihausanovels.com.ng

Ka tura mana sako ta adireshinmu na email, domin tuntubarmu ko turo mana hausa novel ko kuma post.

Email > aihausabooks@gmail.com

******* FOLLOW US ******

Facebook: Ai Hausa Novels

Twitter: Ai Hausa Novels

Telegram Channel: https://t.me/Aihausanovels

WhatsApp Number: 09017242889

Haka kuma domin shiga kowanne daga cikinsu za ku iya ziyartar shafin ku yi search na AI HAUSA NOVELS, hatta facebook group dinmu ma za ku samu.

********************** ⬇ *************************
*************** Ai Hausa Novels ****************
********************** ⬆ *************************

[16/02, 10:58 pm] null: KIƊA A RUWA 3

12

.........“Aunty wlhy Dada ya dawo”.
Zimbur Nabeeha ta tashi daga barcin da take yi tana kallon Rayhana mai maganar. Dan yanzu babu jimawa suka zo gidan ita da Amima. Iske Nabeeha na barci yasa sukai zamansu a falo suna kallo bayan sun saka mai aiki da suka zo da ita yanzun nan shiga kitchen ta musu abinci batare da ko matar gidan sun bari ta san da zuwanta ba. Momy ce tace su kawota kasancewar Nabeehar tayi mata complain a jiya game da aikin gidan. Tasan ragwantar Nabeeha sarai, ita kuma a wannan lokacin bata son a samu matsala kodan First Lady shiyyasa tai gaggawar samar mata da mai aikin, ko muce First Lady ta samar.

“Aunty badai can ɓangaren zakije ba?”.

“To mi kike so nayi Rayhana. Kin san dai mugayen can bazasu faɗa masa na dawo ba. Gara naje da kaina ya ganni.”

“Hu'umm da dai kin bari ya kawo kansa wlhy. Amma kije ai babu aji, bayan kin san shegiyar yarinyar nan tare suka dawo. Ƙilama babu wani saceta da akayi shiyya ɗauketa yaje yasha shagalins.....”

Kallon da Nabeeha ke mata ya hanata ƙarasa faɗa, sai kuma tace, “ALLAH ya baki haƙuri. Amma magana ta gaskiya yanzu fa ba da bace Aunty. Dole ne ki gyara wasu abubuwan musamman zumuɗin nan akansa.” tana gama faɗa ta fice a ɗakin. A ranta kuwa tana saƙa abinda ya daɗe a zuciyarta ne. Dan wannan karon tayi alwashin zatayi yaƙi domin kanta. Bazata iya haƙuri da ciwon dake ranta ba. Sai dai ayi ɗayan biyu. Kota samu, ko kuma kowa ya rasa...

Nabeeha kuwa ƙwafa tayi kawai. Ta nufi bathroom. Babu jimawa ta fito fuskarta jiƙe da ruwa alamar wankota tayi. Gaban mirror taje ta fara gyara fuskar da kayan kwalliya, sannan ta cire kayanta ta canja da wani arnen lass da yay masifar ƙyau ta saka turare sosai a jikinta. Koda ta fito daga Amima har Rayhana da kallo suka bita. Amima data saki baki na mamaki ta ce, “Aunty ina zuwa haka da rana tsaka?”.

“Sashen Mammah”.
Ta bata amsa a taƙaice tana ficewa abinta. Kallon juna sukai ita da Rayhana, Rayhana ta taɓe baki da faɗin, “Kin san bata da wayo sam.”

“To ALLAH ya ƙyauta wannan ai zubar da mutunci ne”. Cewar Amima...

()<>()<>()<>()<>()

Tunda Nabeeha ta shigo falon kowa ya saki baki yana kallonta. Mammah kam kallo ɗaya tai mata ta ɗauke kanta. Koda ta gaisheta ma a haka ta amsa hankalinta akan Nawal ɗin Aunty Mimi. Su Ma'aruff da suka zo wuya zasuyi magana Gwaggo Khadijah tai musu gargaɗi da idanu. Dole sukai shiru. Sarai Nabeeha ta lura da yanayinsu, amma ta danne dan a ganinta basu bane a gabanta. Idanunta akan Mu'azz ta tambayesa ina Dada yake.

Mu'azz ba komai ya sani game da lamarin Nabeeha ba. Duk da dai da wayonsa tabar gidan amma ba komai ya sani ba. Da hannu kawai ya nuna mata sama. Bakuwa ta sake magana ba, ba kuma kunyar kowa balle jin nauyi ta nufi stairscase ɗin tana taku ɗai-ɗai cike da gadara ita ga matar boss.

Aunty Ummi dake jin kamar ta amayo zuciyarta dan takaici taja hannun Aunty Mommy suka shige kitchen bayan tama Mimi signal da ido. Fakar idanun su Mammah tai itama tabi bayansu.

Basu wani jima ba suka fito, hannun Aunty Mimi da tray an haɗa kayan abinci akai. Cikin sa'a dai-dai nan Nimrah da Ruky da Biebah ke fitowa. Nimrah tayi wanka ta canja kayanta. Kuma wando ne fari daya kwanta a jikin nata da riga iya gwiwa Pakistan style na yadi mai taushi. Sai siririn gyale kalar yadin rigar. Babu wata kwalliya a fuskarta sai rosy lips data shafa daya saka lips ɗin taushi da santsi, yay pink sosai, ko daga nesa kake da ita zakaga hakan....

“Yauwa Nimrah zoki miƙama Dada abincinsa”. Aunty Mommy ta faɗa kai tsaye. Ɗagowa Mammah tai da sauri, ta buɗe baki zatai magana Gwaggo Alawiyya ta katseta da faɗin, “Dama yanzu zan yi magana kuwa. Amsa kinji ƴar albarka. Ruƙayya ke kuma zo nan na sakaki aiki”.

Haɗa ido Mammah da Gwaggo Khadijah sukai, Mammah tayi yanayin kai ƙara gareta, amma sai Gwaggo Khadijahn ma tai mata murmushi alamar tana goyon bayan abinda ƴan ta kife ɗin ƴaƴanta ke shirin yi. Kanta ta girgiza kawai tana kallon su Ma'aruff, a mamakinta suma duk sun washe fuskoki ba kamar yanda suka ciskule ba tun shigowar Nabeeha.

Received at 12:22 PM

reacted with ❤ Nimrah dai da ba sanin abinda ya faru sukai ba tuni ta shagwaɓe fuska zata fara langare. Aunty Ummi ta balla mata harara dole tazo ta amshi tray ɗin. Wucewa tai tana ɗan tuttura baki, dan harga ALLAH tana son yin ɗan nesa da shi har sai taji amsar tambayiyinta akan batun nan ɗaya tak daya zame mata ƙayar kifi a maƙoshi....

A wannan lokacin da Nabeeha tuni ta iso ƙofar ɗakin na Dada bayan ta hauro taci karo da Afeef dake fitowa a ɗakinsu shi da Mu'azz ta tambayesa ya nuna mata. Knocking tayi a hankali, sai dai shiru babu motsi balle ta samu amsa. Sanin halinsa yasa ta sake yi har sau biyu, daga nan ta buɗe Kofar kawai ta shiga dan ta kasa daurewa. Da wani irin ƙamshi ta fara cin karo, dan ƙamshin turaren wutar SHUWA INCENSE AND MORE +234 704 229 3387. na Maman Abdull ya gama kama lungu da saƙo na sashen Mammah. Sai da ta lumshe idanu ta buɗe tana sauke ajiyar zuciya kafin ta ƙarasa shiga ɗakin. Ko ina fes a gyare, babu tarkace kamar yanda ta sanshi mutum mara son hayaniya. Jin motsi a bayi yasata zama a bakin gadon tana murmushi, babu abinda take hangowa sai yanda zaiyi mamakin ganinta da farin ciki. Ta sake gyara zamanta da ƙyau. A dai-dai lokacin kuma Nimrah data iso itama tai knocking ƙofar. Sai dai jin shiru da sanin halinsa na in ba shi yaso ba bazai tanka ba yasata murɗa handle ɗin ƙofar kawai ta tura ta shiga da sallama.

Wani kalar zubo mata idanu Nabeeha da zuciyarta tai zallo cikin ƙirjinta tayi. Ta buɗe baki zatai magana tana ƙoƙarin miƙewa kawai aka buɗe ƙofar bathroom. Dada da bai san dasu ba su duka biyun ya ɗan yi tsaii yana kallonsu.

Nimrah kam jitai ƙirjinta ya buga, a lokaci guda tai saurin duƙar da kanta. Gaba ɗaya ji take ta daburce, a hakan ma ALLAH ya sota bathrobe ce a jikinsa ba towel ba.

Sai dai kuma abinda bata taɓa gani bane daga garesa dole ta rikice. Dan bathrobe ɗin ma dai kaɗan ta wuce gwiwarsa.

Har cikin ransa bai ji daɗi ba shima. Idan Nabeeha ta ganshi a haka normal ne ai, amma Nimrah ina, da sauran lokaci. Jallabiya ya ɗauka batare da yayi magana ba ya juya cikin bayin. Babu jimawa ya sake fitowa da ita a jiki. Abinda ya bashi mamaki har lokacin Nimrah na'a inda ya barta. Kanta a ƙasa ga kaya a hannu kamar wadda aka dasa. Yayinda Nabeeha ke mata wani mugun kallo sai dai itama bata iya tayi magana ba saboda wani curarren abu daya dunƙule mata ƙirji ko numfashi bata fitarwa da ƙyau. Zuciyarta tsara mata take taje ta fisgi tray ɗin abincin ta kife mata shi a jiki, sannan ta kamata da shegen duka har sai ta daina numfashi. Kai itafa da tana da dama ko macen sauro bazata sauka mata a jikin miji ba..

Tana can tunanin ya kwasheta kawai sai hango Dada tayi a gaban Nimrah. Itama Nimrahn daba sanin isowarsa tai ba jin an riƙo tray ɗin hannunta ta ɗago da sauri alamar dawowa hayyaci, dan ya fahimci tsayuwar da tayi tunani ta tafi mai zurfi.

“Kina lafiya?”.

Ya faɗa cikin zurfin lafazi daya sakata jin wani sanyi ya dira tsakkiyar kanta yana bin jijiyoyin jikinta yana sauka har ƙafafunta. Slowly ta ɗago idanun da suka kaɗe sosai da ja a ciki, kasancewar shima ita yake kallo sai suka shige cikin nasan har sai da yaji wani dummmm a ƙirjinsa. Dai-dai lokacin Nabeeha ta matso kusa da shi, cike da salon daya ƙona ran Nimrah kawai ta rungume shi ta baya tana kwantar da kanta a faffaɗan bayan nasa. Cike da shagwaɓar iskanci ta furta, “I miss you baby”.

Gefe Nimrah tai da fuskarta tana lumshe idanunta da suka cika da ƙwalla. Dan wani suka da ƙirjinta yayi zata iya rantsewa tunda tasan kanta bata taɓa jin irinsa ba. Gaba ɗaya taji duniyar ta mata ƙunci, wani irin tsanar Nabeeha da haushin Dadan suka zagaye ƙirjinta batare data san dalili ba. Bata motsa ba a wajen da take balle nuna alamar zata fita tabar ɗakin kamar yanda ta fahimci Nabeeha naso, sai ma ji tai a ranta saita baƙanta mata rai itama, sannan wlhy bazata bar ɗakin nan ba yau sai da su zauna su ukun, in banda iskanci da ballagazanci miye na wani rungumeshi a gabanta, ai ko ba komai shi uba ne, yakamata itama ta mutunta kanta a gabansu dan su bata irin darajar da suke bashi koda bata da ita
Received at 12:22 PMa zahiri kamar shi. Amma tunda tace ita ta iya yanzu zata nuna mata shege ma da ubansa ba aruwa ake shawosa ba. ALLAH saita gogema matar nan hadda yanzun nan. Idan ita mijinta ne ai suma Babansu ne.........✍

Tofa Madam Nimrah mutum da matarsa. Tunda kin yarda ita mijinta ne ku babanku ne basai ki fita ki barsu su jiƙa kansu ba🤔. Anya kuwa kikaji shine mijin ba akwai yaƙi ba? To bari muga ya wasan zai kaya a yanzu♀♀☺.
Received at 12:22 PM
[16/02, 10:58 pm] null: KIƊA A RUWA 3

13

.........Dada shi kansa jiyay wata kunya mai tsananin ta rufeshi. Haba shi girma abin a riƙe ne ai. Baiyi ma Nabeeha magana ba amma ya zame jikinsa daga nata, yana nufar kan center table ya ajiye tray ɗin abincin. Yazo ya sake raɓasu ya wuce gaban mirror, wayarsa ya ɗauka ya sake gittasu dai again ya koma kan sofa ya zauna.

Nimrah dake ƙoƙarin controling ɗin kanta ta kalli ƙafafun Nabeeha dake tsaye itama kamar an dasata, da alama abinda yay ɗin ya ɓata mata rai ne ko wani abu oho mata. Kawai sai taji murmushi na neman kufce mata sakamakon abinda zuciyarta ta ayyana mata akan matar. Amma sai ta danne shi ya tsaya cikin ƙirjinta. Dada dake ƙoƙarin kai waya kunnensa ya ɗago ya kallesu, shi sai ma suka nema sakashi yin dariya. Ya dai gimtse baiyi ba, dan saima ƙara ɗaure fuska da yay cikin bada umarni ya furta, “Kiddo zoki bani abinci”.

Duk da wani haushinsa da take ji saboda rungumar da Nabeeha tai masa sai ta jinjina kai tana nufarsa, dan kurama ai tasan gidan mai babbar sanda. A kusa da shi

gab takai duƙe gaban table ɗin, ta bubbuɗe kwanikan abincin sannan ta kalleshi, duk da waya yake da Imran dan taji ya ambaci sunansa bata fasa faɗin, “Dada mi za'a zuba?”.

Yanda tai maganar cikin raɗa da masa nuni da hannu tana wara masa idanunta manya ya sashi ɗan zuba mata nasa idanun. Sai da ta sake waro natan sosai ta ce, “Dadaaaah”. Sannan ya farga da abinda yake ya janye yana nuna mata da hannu. Ta jinjina kai ta fara zubawa, sai dai ta raba hankalinta a kallon Nabeeha da har yanzu ke tsaye inda suka barta tabbacin ta shaƙa da abinda yay mata. A cikin zuciya Nimrah tace (Tun banyi komai ba aunty masu miji) a zahiri kuwa sai da ta kammala zuba abincin tsaff kawai ta saka murfin kwanon tangaran ɗin da aka zuba salad ciki baki-bakin table ɗin da gangan ta kaɓoshi ya wantsalo ƙasa sai kuwa akan ƙafarta. Duk da dai tayi dabarar saka hannu sai da ya taɓa bisa tsautsayi. Zabura tayi cikin gigita sai kuma hannunta ya tsumbula cikin kular farfesu. Aiko ta fasa ƙarar data saka Dada sakin waya ya juyo kanta...

Itako tuni ta miƙe a zabure ƙafar damƙe a hannunta ɗaya tana tsalle da ɗaya, hannun daya shiga miya kuma tana yarfa shi har tana neman faɗawa kan abincin nasa. Ba arziƙi ya tarota gaba ɗaya sai kawai ta faɗa saman cinyarsa. Anan kam harga ALLAH bata san kansa take ba, dan da gaske zafin ya ratsata har cikin kai, gashi bibbiyu hannu da ƙafa, dama ga Nimrah da shegen ragwantaka.

Rasa ina Dada zai kama mata yayi, dan ita kanta Nabeeha sai da ta zaburo, sai kuma taja ta tsaya tuna wacece da kuma yanda ya riƙota jikinsa. Tai bala'in waro idanunta waje ganin ya kama hannun Nimrah kawai ya saka yatsun data saka a farfesu cikin bakinsa. Ɗayan hannun kuma ya riƙo ƙafar tata.

Itama kanta uwar haɗa wajen tsittt tayi a karo na farko, dan abune da yazo mata a matuƙar bazata, bazatar ma mai gigitar da zuciya. Dan yanzu kam ta fahimci an sauka daga layin abinda tai niyyar aikatawa an tafi wani layin sabo data gagara bama suna ko kalma. Dada da shima sai yanzu ya fahimci halin da suke ciki sai ya runtse idanu, kafin ya buɗesu a hankali kan fuskar Nimrah data zuba masa nata idanun cikin yanayin ruɗani. Sai kawai suka sarƙe cikin juna, kamar kuma waɗan da aka hana motsi kowanne ya kasa janyewa suka shagaltu. Shagala a kallon juna irin yanda basu taɓa yi ba cikin idanu dai kamar haka.....

=============

“Baƙo kuma?”.

Hajiya Hasiba ta faɗa da mamaki tana kallon maigadi. Kansa ya jinjina mata. “Eh Hajiya. Kuma kamar ma baɗan ƙas.....”

Ya kasa ƙarasawa sakamakon shigowar Adeel falon. Miƙewa Hajiya Hasiba tayi, dan ita kaɗaice a gidan su Amima na gidan Nabeeha. Cikin in-ina maigadi ya ce, “Ya....ya..yauwa Hajiya ai gama shi nan ya shig.....”

Hannu ta ɗaga masa. Sai kuma tai masa nunin ya fita. Babu musu ya nufi hanyar ƙofa yana waigen Adeel. A ransa faɗi yake (Yau gani ga Balarabe ikon ALLAH) sai da ya kusa cin tuntuɓe ya dawo hayyacinsa...

Received at 12:22 PM

Adeel dake kallon Hajiya Hasiba fuska a ɗaure hannayensa duk a cikin aljihun wandonsa ya kai zaune cikin kujera cike da isa da gadara. Sai wani bin falon yake da kallo a yatsine. Duk da kuwa ba laifi falon ya haɗu, kuma a gyare yake tsaff ga ƙamshin air freshener na tashi. Sake maida idanun nashi yay a kanta. Da sauri ta fara gaishe shi murya na rawa.

Maimakon amsa mata sai yaja siririn tsaki. Cike da wulaƙanci ya furta, “K! Nine zakima ƙaryar kinyi tafiya?”.

“Wlhy ba ƙarya nake maka ba. A cikin satin nan na dawo. Kuma na nemeka amma ban samu ba. Ban san ka dawo ƙasar nan ba shiyyasa nake neman layin Abu-dabi.”

"Mtsoww!" ya sake jan tsaki. Sai kuma ya sake watsa mata kallon banza. "Nayi alƙawari dake kin saɓa. Kince mijinta na prison na bincika ance ya fita. Baki zo kin min bayani ba saboda kina ɗaukata wawa...."

"Wlhy ba haka bane Sir! Idan baka manta ba nata ƙoƙarin mu haɗu kafin kayi tafiyar farko. Amma hakan bai samu ba. Lokacin daka dawo nan ma naso hakan amma baka ɗaga kirana ba, sai daga baya nake jin ka wuce a wajen First Lady".

"Wannan kuma damuwarki ce. Na baki kwana bakwai ku koma Dubai da ita. Idan ba haka ba zan yi abinda naga dama. Sannan duk abinda na baki komin ƙankantarsa ne babu sai kin cika. One week".

Daga haka ya miƙe abinsa ya nufi ƙofar fita. Cikin rawar jiki Hajiya Hasiba ta yunƙuro zatai masa magana. Hannu ya ɗaga mata tare da watsa mata kallon daya sakata dakatawa da sauri. Sai da ya fice ta bugo musu ƙofar ta zabura gefe.....

(Idan kwaɗayi.....♀)

>>>>>>%<<<<<<

A ɓangaren Daddy Imran da ƙarar Nimrah ta tayarma hankali tun yana kiran hello! Hello! Har ya haƙura ya yanke kiran. Vibration ɗin kiran daya sake yi da yanda Nabeeha da ke jin kanta na juyawa kamar zata sume a wajen ta nufo inda suke a matuƙar fusace jikinta har yana rawa ya dawo da Dada da Nimrah hayyacinsu. Hannu Nabeeha ta kawo a zafafe zata cakumi Nimrah. Amma sai aka riƙe hannun nata caraf a bazata. Ido cikin ido suka kalla juna ita da Dada. Da wani kalar kallon dake tabbatar da gargaɗinsa da barazanar da bata taɓa gani ba ya furta,

"Kada ki taɓa koda mafarkin tsallaka wannan layin a karo na biyu. Dan tabbas bazaki ajiye ƙafarki kan ƙasa tana tare da gangar jikinki ba. Ni mai RIKICI ne akan wannan ANANAR. Ba lallai na iya kauda idanun TAƁATA ba koda akan kaina ne."

Sosai zuciyar Nabeeha ke bugawa da sauri-sauri a cikin ƙarjinta. Lips ɗinta na rawa ta buɗe zatai magana.....

"Shiiii!!!" ya faɗa cikin ƙatseta yanama bakinsa alamar zipping da nuna mata hanyar ƙofar fita.

Nabeeha dai tasan halin kayanta, ta kuma san mi zai iya. Ta kuma san fassarar gargaɗinsa da umarni musamman idan har ya buɗe baki yay magana akan abinda ke ransa. Ita ko tsuntsuwar tasa bama ta fahimci inda kalaman nasa suka dosa ba. Hasalima ba maida murtani ga Nabeeha datai niyya bane a wannan gaɓar damuwarta, kasancewarta akan cinyarsa ne tashin hankalin ta. Gashi ya riƙeta ta yanda ta gagara koda motsi. Sai da Nabeeha ta buga ƙofar da ƙarfi Nimrah ta zabura, tsalle ɗaya tai ta wantsalo ƙasan lallausan carpet ɗin wajen jikinta na tsuma, ga zuciyarta na wani kalar bugawa diff-diff-difff. Dada ma idanu ya runtse da ƙarfi, sai wani motsa yatsunsa yake kamar mai kiɗa akan hannun kujerar. Sai da ya tabbatar ya samu nutsuwar da yake buƙata sannan ya buɗe idanun tare da yin gyaran murya yana sake tsuke fuska tamau.

Cikin dakewa a ainahin Dadan sa ya furta, "Naga hannun".

Nimrah dake jin kamar tayita kwarara ihu saboda kunya, har idanunta sunyi jawur ta ɗan kallesa. Sosai taji shakkarsa da kwarjinin sa na sake mamayeta. Dan duk da ba dariya yake mata ko surutu ba ƴar sakewar da yake da ita na sakata jin sauƙi. Amma yanda yay ɗin yanzu ita tasan wargi ma waje yaka samu. Sai da ya ƙarema yatsun kallo, ya kamo ƙafarta itama ya duba, duka farcinan sunyi ja daga na ƙafar harna hannun. Baiyi magana ba ya miƙe zuwa fright ɗin ɗakin, ice ya ciro babba ya dawo inda take ya zauna.

Received at 12:22 PMIta dai binsa take da kallon mamaki, handkachiff ɗinsa dake ajiye a saman kujerar ya ɗauka ya saka ƙanƙarar a ciki. Kai tsaye ya kamo hannun nata ya ɗora a wajen data ƙone ɗin duk da baiyi alamar tashi ba. Tako sauke ajiyar

zuciya da har sai da ya lumshe idanu ya buɗe. Sai da ya saka mata kusan na minti uku sannan ya miƙa mata alamar ta cigaba da sakawa. Shi kuma ya ɗauki wayarsa.

Bata san waya kira ba, kawai jitai cikin umarni ya furta, “Turo min Ruƙayya”. Daga haka ya yanke kiran.........✍

Hajja Ninah Ai wanda bai ji bari ba yaji hoi♀.

Received at 12:22 PM

[16/02, 10:58 pm] null: KIƊA A RUWA 3

14

........Anan falo Ammar na ajiye wayar su Aunty Ummi suka shiga masa alamar yaya dai. Dariya yayi, dama kuma ita suke yi tun fitowar Nabeeha da gudu tana kuka da basu san abinda ya korota ba. Tun wucewar Nimrah sama Mammah ta bar falon. Hakan yasa Gwaggo Khadijah da Gwaggo Alawiyya binta, dan sun san dai bai wuce lamarin Nabeeha ne ke damunta ba duk da tana ƙoƙarin ganin ta danne. Amma dai abinda Nabeehan tayi yau rashin kunyar tayi yawa ai.

Wucewar iyayen nasu ciki daɗi yay ma su Ja'afar, dan a take suka shiga amaye abinda ke bakinsu game da Nabeehan suma, kowa cin alwashi yake akan koyama Nimrah abubuwan da zata ƙona Nabeeha da ruwan jikinta. Sai kuma gata ta sakko a kiɗime harma tana kuka. Tsabar wulaƙanci sai suka fashe da dariya a tare har wasu na tafawa. Aiko kamar sun izata, sai ta ƙara gudu tana danne bakinta saboda tahowar wani sabon kuka mai ƙarfi. Suna cikin dariyar ne kiran Dada ya shiga wayar Ammar. Da sauri ya ce, “Kuyi shiru Dada ne”.

Tsitt sukayi ya gama amsa wayar, shine yana yankewa suke tambayar mike faruwa. Abinda Dadan ya faɗa ya sanar musu. Biebah ta ƙwalama Ruky dake kitchen tare da Mu'azz wai suna ma Nimrah special girki kira. Amsawa tai tana fitowa. Saƙon Dada ta gaya mata, da yake bata san wainar da ake toyawa ba ta nufi saman cikin farin cikinta..

Rikicewa Ruky tai da ganin Nimrah kamar tayi kuka. Ta shiga tattaɓata tana tambayar mike damunta. Har sai da Dada daya shagala a kallon su yay gyaran murya. Cikin shagwaɓa Ruƙayya ta kalleshi, kamar zatai kuka ta ce, “Dada Aunty Nabeeha ce ta dake ta?”.

Idanu ya waro waje dan mamaki. Wato dai halin iri ɗaya ne ita da aminiyar tata. Ji wani sharri kuma. Bashi da zaɓin daya wuce girgizama Ruƙayyan kansa, kafin cikin umarni ya ce, “Kamata kuje ta kwanta”.

Kamata Ruky tai, har suka fita yana binsu da kallo, a ransa kam yana jinjina wannan ƙaunar juna. Bayan soyayyar jini, da soyayyar ma'aurata soyayya mafi muhimmanci da ban mamaki ga ƴaƴan adamu itace ta abokantaka da babu alaƙar jini a ciki, lallai duk abokan da sukai tarayya akan soyayya ta gaskiya zasu shiga aljanna suna masu farin ciki da juna. Idan riya ko cin dunduniya ta shigo sai su ƙare da zage-zage da aibanta juna a ranar rarrabe ayyuka. (Ya Rabbi kasa mu rayu da masoya na gaskiya, mu kuma kasance a aljanna tare muna masu farin ciki da juna. Duk wanda zai zo garemu da fuska biyu, ya rabbi kasa shartinsa ya zamewa rayuwarsa bargo akan kansa can ya ƙarata shi kaɗai[illegible]).

Cahh iyayen nasu suka yo musu da tambayoyi a falo. Sai da Nimrah ta sanar musu abu ne ya faɗo mata a ƙafa sai kuma ta ƙone sannan suka nutsu. Amma da kowa ya hau da tunanin Nabeeha ce. Har sun fara ɗaukar alwashi a zukata. Dariya ce ta nema suɓuce ma Mammah dake ƙoƙarin fitowa. Ta girgiza kai tana gimtsewa. A ranta kam ta fahimci dole tai wani abu kafin waɗan nan iyayen banzar su ɗora Nimrah kan wani layin daban, a haka ma yaya lafiyar kura tunda itama ba ƙyalen bace ƙyallece ita da aminiyar tata Ruƙayya da basa ɓoyema juna sirri....

^^^^^^^^^^^^^^

A ɓangaren Nabeeha kam yanda ta shigo sashen nata ya saka Amima da Rayhana dake cin abinci kallon juna. Sai kuma suka taɓe baki a tare. Amima ta ce, “Lafiya kuwa?”.

“Ƙ'ya tambayeni bayan muna tare”.

Cewar Rayhana fuska a yamutse.

Amimah ta ce “Hummm maybe korota sukai ko”.

“Mtsowww matsalarta ce. Banda zubar da kai ka dawo miji baizo inda kake ba kai ka ɗauki ƙafa ka tafi nemansa. Itafa wannan da cikin aljihun baya aka haifeta muguwar kidahuma za'ayi. Bata gane komai sai son miji.”

“Ikon ALLAH to miye dan taso mijinta Rayhana. Wani kike so taso to ne?”.

Hararar Amima mai maganar Rayhana tayi, cike da takaici ta ce, “Kema fa wawuya ce wani lokacin. Inba hauka ba son miji ne kawai rayuwar aure?. Mijin ma irin Haysam daya san martabar kansa, wlhy sam bata dace da shi ba.”

Received at 12:22 PM Galala Amima tai tana kallonta yanzu kam. Sai kuma tace, “Tofa wata sabuwa. Sai yanzu duk kika san wannan? Toke auren kikai da kika san mima mijin ke buƙata? Anya Rayhana babu wani abu a ranki?”.

“Ubanki ne a raina. Shegiya munafuka”.

Cike da son tura haushi Amima ta kwashe da dariya tana miƙewa da faɗin, “Oh to lallai abin ya girma. Ubana kam ai ubanki ne kema dole ya zauna miki a rai. Adai bi a hankali. Kar wajen tone-tone kaza ta tono wuƙar yankanta. Shi wannan NAMIJIN ZAKI ne ba Mazan club ba. Baya ɗaukar wargi balle shashanci. Itama data samu bata kasance ballagaza bane kuma tana cin darajar Abbanta. Amma kinga matsayarta, balle ke da aka saba leƙe-leƙ...”

Jifan da Rayhana ta wurgo mata da saving spoon ya sata barin wajen da gudu tana dariyar iskanci data sake shaƙe wuyan Rayhana...

•••••••••••••••••••

9:pm na dare Dada daya fita a gidan shi da su Ma'aruff tun bayan sallar magriba suka dawo. Asibiti suka rakashi ya duba Lailah da Baby, daga can suka je duba Daddy Imran gida. Zuwa lokacin su Aunty Ummi duk sun wuce gida. Falon ma babu kowa alamar duk sun shige barci. Baiyi mamaki ba dan yasan masu ƙiriniyar gidan na fama da kansu. Mammah kuwa dama akwai barcin wuri. Su Bilal kuma office gobe. Har ya nufi upstairs sai kuma ya dawo da baya, ƙofar Mammah ya nufa, yay knocking a hankali. A mamakinsa sai yaji tana bada umarnin shigowa.

Koda ya shigo a zaune ya sameta bakin gado tana duba wani littafin addu'oi. Ta ɗago tana kallonsa da amsa sallamarsa. Dai-dai yana kaiwa zaune take faɗin, “Ai har na fara tunanin kiran wayarka. Dan zaman jiranka nake daman”.

Ƙaramin murmushi yay da faɗin, “To Mammah lafiya dai ko?”.

“Lafiya lau. Yaya jikin Imran ɗin?”.

“Alhamdullah ai ba a jigace yake ba. Kawai dai harda razani”.

“Alhamdullah ALLAH ya kiyaye gaba. In sha ALLAHU zan je na duba shi gobe nima.”

“ALLAH ya kaimu”.

“Amin ya rabbi. Shaiɗancin mutanen nan ya fara bani tsoro Muhammad. Tunda har tunaninsu ya fara basu yin amfani da makusantanka domin samun biyan buƙatarsu. Abin akwai haɗari sosai a ciki, idan na farko an tsallake rijiya da baya nan gaba kuma fa?”.

Ajiyar zuciya ya ɗan sauke, dan shi da farko ma yayi tunanin maganar Nabeeha zatai masa. “Kar ki damu Mammah in sha ALLAHU hakan bazai sake faruwa ba. Wannan ma da suka aikata zasu biya bashinsa harda riba da hannayensu. Akwai shirin da nake yi musamman akan su ƙananun nan. A cigaba da mana addu'a dai. Dan in sha ALLAHU nasara ce ke tunkaro mu. Ko ba komai abinda sukayi yanzu ɗin ya ƙara buɗe min tunani na akan sanin su waye su.”

“Addu'a har mu koma ga UBANGIJI bazamu daina yi muku ita ba, ALLAH ya cigaba da baku kariya. Ya ɗora nasararku akan maƙiyanku. Suma ALLAH ya shirye su su gane gaskiya kafin lokaci ya ƙure musu idan masu shiryuwa ne.”

“Hummm Mammah kenan, to Amin. Amma waɗan nan mutanen basa buƙatar shiriya.”

“A'a ba'a yankema UBANGIJI hukunci akan ikonsa ai.”

“Haka ne kam, ALLAH yasa mu dace. Ranar asabar iyayen Haydar zasu zo a tsaida magana. Kuma ina son ne kawai a saka rana batare da wani jeka ka dawo ba. Lahadi mu kuma sai muyi batun Bilal da Asma'u. Sai dai shima Ammar kawai zan haɗa da shi”.

Murmushin Mammah ya faɗaɗa sosai. Ta ce, “Alhamdullahi ALLAH yasa ayi damu. Ya kuma sanya albarka a ciki. Amma Auta yana da budurwa kuwa?”.

Yanzu kam sai da Dada ya ɗan murmusa. Kai tsaye ya ce, “Zan bashi Ruƙayyana in sha ALLAHU”.

Wani irin farin ciki ne ya daki zuciyar Mammah. Har bama tasan ta zabura ta kamo hannun Dada ba. Ta ce, “Muhammad da gaske? Aiko idan kayi haka ka gama min komai. Wannan tunanin ya daɗe a raina. Tsoron halin ɗan yau yasa na shanye abina. Ya rabbi yanda ka bani wannan farin ciki a wannan dare kaima ALLAH ya faranta maka har ƙarshen numfashinka”.

Received at 12:22 PM “Amin Mammah, tare dake da zuri'armu”.

Sosai take farin ciki, dan har sai da tai sujidar shukur. Bayan ta ɗago ne take masa maganar shima lokaci yayi da Nimrah zata san wanene shi a gareta. Dan ɗazun Imran ya kirata sun tattauna sosai. Shiru Dada yay baice komai ba, itama bata damu da shirun nasa ba ta cigaba da faɗin, “Tunda har sun gaya mata yin shirun mu zai sakata a wasi-wasi. Amma idan mun sanar da ita zata kasance a nutsuwa koda zata shiga ruɗani. Nimrah yarinya ce mai wayo, suna da iliminsu da fahimtar abubuwa gwargwadon iko, idan bamuyi saurin yin hakan ba a yanzu suke tasowa samari na kawo musu caffa, idan sun tsallake tarkon wani bazasu tsallake na wani ba dan zuciya ba'ai mata shamaki ƙo ƙa'idar wanda zata iya so. Makarantar ma idan zata zama damuwa kawai su zana ssce wannan shekarar, maybe idan suka ga kansu a jami'a a samu sauƙin wannan ƙiriniyar tasu”............✍

Hhuummmm!
Received at 12:22 PM
[16/02, 10:59 pm] null: KIƊA A RUWA 3

15

.........Ya gamsu da shawarar Mammah kam. Dan haka yace, “Hakan yayi sosai. In sha ALLAHU zan duba naga yiwuwar komai Mammah.”

“To ALLAH yay muku albarka. Ka sanar ma Jamilu ne?”.

“Eh, in sha ALLAHU. Yace ma yana tafe ranar juma'a. Sai dai Uncle Naseer zuwa gobe in sha ALLAHU zanje shima muyi maganar. Sai waɗan nan yaran, su basa komai ne a gidansu suka zo nan suka tare?”.

Ta san su Hanoon yake magana. Dan haka tai murmurshi. “To ban sani ba Muhammad. Amma dai nayi waya da Tasi'un ya tabbatar min sati mai zuwa shima zai dawo ƙasar. Amma ina son ka zauna dasu ko sau ɗaya ne ka tsawatar musu akan wasu ɗabi'u nasu marasa ƙyau kodan a taimaki rayuwarsu.”

“Hummm Mammah, nifa akan abinda na isa kawai nake tsawa. Ki bar masa ƴaƴansa a yanda kika gansu yazo ya kwashe abinsa. Ai ya fiki sanin ba'a dai-dai suke ba. Amma ya zaɓi barinsu a haka. Yanzu dai kwanta ki huta. Nima zanje barci nake ji sosai.”

Sarai ta fahimci dan ya kaucewa maganar ne kawai. Dan haka ta ɗan murmusa tana girgiza kanta. Har yay mata sallama ya fice tana binsa da kallo....

Koda ya maida ƙofar ya rufe dole ya ciro wayarsa ya kunna fitila dan an kashe hasken falon gaba ɗaya. Takunsa bai wuce biyar ba yaja ya tsaya gab da fara hawa staircase saboda kamar nishin kuka yake ji. Duk da anayi ne ciki-ciki ƙarfin ji da ALLAH ya bashi ya saka shi ji, ga kuma darene ko ina yay tsitt. Juyawa yay saitin inda yake jiyo sautin. Tabbas a kitchen ne, dan haka ya zubama ƙofar shiga idanunsa tsahon sakanni. Kafin ya ɗaga ƙafafunsa ya nufi wajen cike da takunsa na jarumta da lafiyar jiki irin ta baraden maza masu tsayin gaɓɓai. Hasken wayar ya ɗan rufe da hannu, kafin ya tura ƙofar kitchen ɗin....

Yanda ya shigo a bazata, tare da haska kitchen ɗin da fitilar wayarsa a lokaci ɗaya ya saka Nimrah zabura. Dan zaune take a ƙasa cikin ɗan lungun jikin cabinet, ta saka kanta a tsakiyar ƙafafunta. Fitilar kitchen ɗin ya kunna, ganin wanene ya shigo ya sata miƙewa tsaye gaba ɗaya jikinta na tsuma.

Dada kam idanu ya zuba mata kawai yana kallonta daga sama har ƙasa. Kayan barci ne wando da riga masu taushi a jikinsa. Wandon har ƙasa, sai rigar mai gajeren hannu iya gwiwa. Kanta da hula, sannan ƙafarta da bedroom slippers masu taushi. Tunda tai masa kallo ɗaya ta duƙar da kai bata sake ɗagowa ba. Tana ta dai cuɗa hannun nata cikin juna yanda aka saba....

“Ki dafa lemon tea ki kawo min”.

Ya faɗa kawai yana juyawa abinsa ya fita. Sharr hawaye suka sake zubo mata. Takai hannu ta share tana jan hanci. Batare da tace komai ba ta nufi inda tea pot ɗinsu suke ta ɗauka ɗaya ƙarama. Fanfo taje ta ɗauraye sannan ta saka ruwa dai-dai misali ta nufi gas. Ta ajiye tukunyar tana sake share hawayen da suka ƙi tsaya mata da shashshekar kuka. Abubuwane sun mata yawa a cikin ƙirji, musamman wanda ta gano a wajen mutanen can da wanda aka sanar mata game da zuri'arta da shi kansa Dadan da ƴan uwanta data gani jininta a karo na farko a rayuwarta, bayan labarin mahaifiyarta data rasu babu labarin wanda ta taɓa sani a danginta sai yanzu. Addu'ar da take ta ambato ce kawai ke saka mata nutsuwa da babu abinda zai hanata haukacewa a wannan gaɓar. Lemon tsamin data ɗauka babbar guda biyu ta wanke, tare da ganyen na'a-na'a da lemon grass ta koma wajen tukunyar ta zuba. Lemon tsamin kuma ta yanka ɗaya a ciki, ɗaya a cikin flaks data ɗakko shima....

Dada da yay ɗan jimm a bakin ƙofar kitchen ɗin yana kallo tamkar yana hangota jin ta fara kai-kawon aikin daya sakata, amma tana cigaba da shashshekar kuka sai ya furzar da iskar bakinsa kaɗan yana barin wajen. Sama ya haura abinsa. Sai dai bai wuce ɗaki ba sai da ya leƙa ɗakin su Mu'azz dana su Bilal ya tabbatar sun kwanta, sai Afeef ne ma ke latse-latsen waya, yana jin kuma za'a buɗe ƙofar ya kifeta shima yaja bargo yay likimo. Dan ya tabbatar Dada ɗin ne saboda duk dare haka yake musu..

Received at 12:22 PM Ɗakin sa ya wuce. Bayan ya zube wayoyinsa a saman mirror ya shiga kunce agogon hannunsa. Dai-dai nan Nimrah tai knocking.

“Shigo”.

Ya faɗa a taƙaice. Koda ta turo ƙofar ta shigo da sallama ƙasan maƙoshi saboda muryarta ta ma dishe, bai juyo ya kalleta ba amma ya amsa a lips. Hanyar bayi ya nufa yana rage botiran shirt ɗinsa da faɗin, “Ki jira ni anan” daga haka ya shige ya barta da bugun zuciya da kallon ƙofar bayin. Bata da zaɓin daya wuce bin umarninsa. Dan haka takai zaune a ƙasan carpet tana ɗan wasa da lallausan gashin jikinsa. Sai dai lokaci-lokaci tana share hawayen dake ciko mata idanu amma taƙi bari su zubo...

Ya ɗan jima kafin ya fito, sai dai kayan barci ne yanzu a jikinsa saɓanin kayan daya shiga da su. Tunda tai masa kallo ɗaya ta maida kanta ta duƙar. Shi kam baima kalla inda taken ba kai tsaye gaban mirror ya nufa yana ƙara tsane gashin fuskarsa da ƙaramin towel. Ya ɗan ja mintuna a wajen, dan sai da ya saka turare a jikinsa ya kammala uzirinsa kafin ya nufi gado abinsa. Ɗago kai Nimrah tai a karo na biyu tana kallonsa, a tunaninta koya manta da ita ne, ganin ya hau gadon sosai ya zauna, sai dai ya jingina bayansa da fuskarsa yaja bargo ya rufama ƙafafunsa zuwa ƙungunsa,

ya kuma kashe hasken fitilar ɗakin gaba ɗaya sai lamp itama ta side ɗin da yake zaune kawai.

"Bani".

Ya faɗa a taƙaice yana buɗe laptop daya ɗora saman cinyarsa bayan yasa ƙaramin filo. Shiru Nimrah bata motsa ba, dan batama fahimci da ita yake ba. Sai da ya ɗago ya kalla inda take, tare da faɗin, "Wai bada Nimrah nake ba".

Ƙirjinta taji ya buga, dan bayan a jeji data gudu sanda bomb zai tashi bata taɓa jin ya kira sunanta ba. Miƙewa tai gaba ɗaya ta ɗauki tray ɗin data saka ƙaramin flaks da tea cups guda biyu, sai tea spoons suma biyu da zuma cikin ɗan wani gora mai ƙyau alamar a haka aka sayeshi. A ƙasan carpet ɗin gaban gadon ta ajiye, daga tsugunne ta haɗa masa komai. Saman bed side drawer tai nufin ajiyewa sai ya miƙa mata hannu batare daya bar abinda yake a laptop ba. Hannun ta kalla, sannan ta ɗan kalla fuskarsa dake ciɗin-ciɗin kamar koyau she. Dole ta matsa sosai inda yake sannan ta miƙa masa. Maimakon amsa da ɗan plate ɗin da kofin ke a kai sai kawai ya kama hannun cup ɗin, ita kuma da ba haka tai zato ba sai taji kamar ya tafi zai ɓare ne, caraf ta kama hannunsa cikin nata hannun.

Idanunsa dake kan screen ɗin yaɗan lumshe tare da buɗewa a lokaci guda kan hannayen nasu. Da sauri ta janye nata tsigar jikinta na tashi batare data san dalili ba. Shima sai bai ce komai ba, ya dai kalleta shaaa ya ɗauke idanunsa. Daga haka ya fara shan shayin yana aikinsa. Ganin lokaci na ƙara jaa yaƙi cewa kuma ta tafi cikin rawar murya ta ce, "Dada na tafi?".

Shiru bashi da niyyar amsata, bai kuma daina aikinsa ba balle shan shayinsa da yake matuƙar jin daɗinsa. Sai yaji tama fi Ammar iya dafawa. Dan kullum shi yake sakawa ya dafa masa. Ammar daya fahimta ma ko bai buƙata ba sai ya dafa ya kawo ya ajiye a ɗakin in ma baya gidan. Yau ma gaba ɗaya ya shafa'a ne saboda kasancewar su Aunty Mimi a gidan.

"Tashi ki dawo sama".

Furucin yazo mata a bazata daga bakin wanda bazata iyama jayayya ba. Gadon ta kalla sannan ta kallesa, ganin har yanzu hankalinsa akan aikinsa yake sai taji kamar ta saki kukan da take ta faman dannewa. Bata da zaɓin daya wuce bin umarninsa, dan haka ta miƙe kanta a ƙasa ta ɗofanu acan ƙarshen ƙafafunsa dake cikin bargo. Sai da taja kusan mintina biyu kafin ya ɗago ya kalleta, kallo irin na tsaiii ɗin nan akan mutum dake sakashi yaji rikicewa, sai dai babu damar yin motsi balle yin magana dan anfi ƙarfinka.

"Mike damun ki?".

Ya faɗa kai tsaye idanun nasa dai a kanta ƙyam. Jitai ta sake daburcewa, dan ta tabbatar dai amsar yake buƙata daga gareta kuma dole ta bashi. Cikin rawar lips da in-inar da yanzu tazo mata ta buɗe bakin zata fara magana...

Received at 12:22 PM "Kar kimin ƙarya".

Ya katse hanzarinta cikin gizago. Sai kawai taji hawaye sun ciko mata idanu. Lips ɗinta sai rawa suke kuma. Idanunta ta ɗan ɗago kaɗan da nufin satar kallonsa sai taga nashi har yanzu ƙyam a kanta. Da gudu ta risinar da nata. Sai ga hawaye sharrr da take faman riƙewa sun ɓalle. Fuskarsa ya kauda gefe yana furzar da iska. Sai kuma ya janye laptop ɗin gefe, tare da ajiye kofin shayin da har ya shanye a bed side drawer ya miƙa mata hannu.

"Zo nan".

Kamar dama abinda take jira kenan ta miƙe, gabansa tazo zata durƙusa daga ƙasa ya hana hakan ta hanyar riƙo hannun nata. A bakin gadon ya zaunar da ita tana facing ɗinsa, har jikinta na gogar nashi duk da shi a rufe yake da bargo. Dan haka ta ƙara duƙar da kai sosai..........✍️

Received at 12:22 PM

Viewed 2 times

[16/02, 10:59 pm] null: KIƊA A RUWA 3

.........."Yaushe kika zama sha-sha-sha ne da komai kuka-kuka?".

Yanda yay maganar can ƙasan maƙoshi, da sigar lallashi yana ɗan matsa hannunta dake cikin nashi har yanzu ya sata ɗan jin sassauci. Cikin muryarta dake a ɗashe ta ce, "Dada ina son na Mutu ne?".

Idanu ya zuba mata sosai, sai kuma ya ɗan motsa lips kaɗan ya ce, "Mutuwa? To idan kika mutu wazai haifa ƴaƴan soja Kiddo?".

Da sauri ta ɗago tana kallonsa, duk da bawani ta gane zancen nasa ina ya dosa bane ba. Kai ya ɗan jinjina mata alamar tabbatarwa. Ita kuma sai kawai ta tura baki tana janye idanunta daga cikin nashi.

Mitsitsin murmurshin da bai shirya bane ya kufce masa. Sai dai bai bari ta gani ba ya gimtse abinsa. Gyaran murya ya ɗanyi, hakan ya sata sake ɗagowa, sai dai bata yarda sun haɗa idanu ba. Cikin son kamata a wuya ya canja salon sigar tambayar tasa. Dan ya fahimci ɗaya daga halayenta shine kafiya, dagiya akan abu. Idan ba ita taso ba akwai taurin kai. Sannan ya fahimci depression ne ke neman kamata.

"Miyasa kika daina raba damuwarki da ƴar uwarki, aminiyarki? Bayan kuma sanda na dawo ba haka naga kuna yi ba. Kin fara ɓoye mata abubuwa ne?".

Kanta ta girgiza masa da sauri.

"Magana nake so da baki".

"Bana ɓoye mata komai. Kawai dai yau ne naji ina son na dawo kitchen ɗin nayi kukan".

"Ko kuma kiyi mutuwar da kike so ba".

Shiru tai dan bata da abin faɗa. Kamar ma ya shiga ya karanta abinda ke zuciyarta ne. Shima fahimtar hakan ya sashi cigaba da faɗin, "Shike nan tunda baƙya son Ruƙayya tasan damuwarki itama ta damu. Ni kiyi abota da ni mana. Kinga tunda na riga na ganoki sai mu dinga tattauna matsalar a tare ko? Hakan bazai sa Ruƙayya taji ba balle hankalinta ya tashi kamar yanda baƙya so".

"Ai Mammah tace babu ƙyau abota tsakanin namiji da mace".

(Wata sabuwa) Ya faɗa a zuciya. A zahiri kam sai ya ce, "Haka ne gaskiya Mammah ta faɗa. To amma ai ni ne, Mammah bazata hana ba. Bakiga itama da ni take shawara ba. Amma tunda baƙya sona da abokin ai shike nan. Zan nema Ruƙayya mu ƙulla, kar kuma kiga mun ware ki kiji haushi. Dan zanyi duk yanda zan yi na ƙwace miki ƙawa".

Baki ta tura gaba tana kumbura kumatu. Ta ce, "Na yarda to".

Dariya ta kama shi, ya dai gimtse da ƙyar. Sai kuma ya miƙa mata ƙaramin yatsarsa alamar su ƙulla to. Yatsar ta kalla tsawon sakanni, kafin ta ɗago nata hannun slowly ta miƙa masa itama nata ƙaramin yatsan ya sarƙe waje guda.

"Shi ke nan daga yau mu abokai ne ba?".

Kanta ta jinjina masa. Shima ya jinjina nasa yana faɗin, "Good. Ƙara zuba min shayin, sai kizo ki bani labarin miya saka ki kuka yau?".

Shayin ta sake zuba masa kamar yanda ya buƙata. Sai dai bata dawo saman gadon ba tai zamanta a ƙasa. Shima baiyi magana ba ya ɗauki laptop ɗinsa ya cigaba da aikinsa. Hammar data saki a karo na uku ya sashi kallonta. Sai da ya sha shayi daya kai baki ya ajiye kofin sannan yay magana.

"Kinga barci yazo ma. Tashi na rakaki ki kwanta da safe ƙya bani labarin, maybe ma lokacin kin huce sosai daga fushin ko?".

Kanta ta jinjina masa nan ma, harta yunƙura zata tashi ya dakatar da ita. Cikin tsaurin murya ya furta, "Daga yau karna sake ganinki kina kuka a ko inama ba kitchen ba da daddare. Idan mutum yana cikin damuwa ba kuka bane mafita ko hana kai barci ko son a mutu ne hanyar yayewar damuwa ba. Alkur'ani ake ɗauka a karanta. Ko ai alwala ay salla a nema ɗaukin UBANGIJI. Dan shi mai Rahama ne da jin ƙai ga bayinsa masu dogaro da shi. Ko aita ma ANNABI salati ko istigifari".

Kanta ta jinjina. Tana mai cuɗa yatsunta waje guda ta ce, "In sha ALLAHU bazan sake ba Dada. Zan dinga yin kuma yanda kace".

"Good Negar. Idan kikai hakan zanyi alfahari da ke. ALLAH yay miki albarka".

"Amin".

Ta faɗa a hankali tana satar kallonsa. Ganin ita yake kallo shima sai tai saurin janye wa. Guntun murmushi yayi yana sakkowa a gadon. Dan haka tabar wajen da sauri tana ɗaukar tray ɗin kayan shayinsa.

Received at 12:22 PM

Viewed "Bar wannan".

Ya faɗa yana wuceta. Maidawa tai ta ajiye tabi bayansa. A haka suka fito a ɗakin tana biye da shi har suka sauka ƙasa. A bakin ƙofarsu yaja ya tsaya, sum-sum kanta a ƙasa ta ce, "Dada sai da safe nagode".

"Uhmmm".

Ya faɗa a maƙoshi kawai yana binta da kallo harta shige. Ta turo ƙofar zata rufe suka haɗa ido. Da sauri ta ƙarasa rufewa tana jingina a jiki tare da runtse idanun tana sauke numfashi. Sai kuma ta zabura tana leƙensa ta jikin Door peephole na ƙofar. Yana tsaye har lokacin shima ya zubama ƙofar idanu da wani kalar kallo data kasa bama suna. Kusan mintuna biyu kafin taga ya furzar da iska yana barin wajen. Itama iskar ta furzar tana sauke ajiyar zuciya. Kafin ta bar wajen zuwa gaban gadon Ruky ta gyara ma bargo daya zazzame a jikinta. Sannan ta nufi bayi yin alwalar barci......

Jin hawowar Dada staircase ɗin ya saka Afeef komawa da sauri cikin ɗakinsu yana danne baki da hannu. Kafin ya tsaida video ɗin da yake recording a wayarsa.

Daga waje shima Dada tsai yay yana kallon ƙofar, sai kuma ya wuce abinsa ɗaki batare daya ce komai ba.

Hummm Afeef video kuma?

---

Yau da wuri ya shigo gidan. Dan gaba ɗaya baida nutsuwa. Ganin har dare yayi hakan na nufin kwanaki biyu suka rage masa da wannan daren game da umarnin ƴan jam'iyya. Zuwa yanzu ya yanke ma kansa hukuncin da zai fishshe shi ya kuma taimaki ƴan ƙasa da wani abun koda ba komai da komai ba. Dan itace kawai mafitar data rage masa. Yayi alƙawari ma UBANGIJI da talakawan ƙasa da sukai faɗi tashi akan zaɓensa da tunanin ya cancanta wajen kamanta musu abinda ya dace matsayin shugaba. Idan kuma har ya miƙa wuya ga wancan layin ya tabbatar waccan burin nasa da alƙawarin zai tashi a banza ne. Dan shi bai ci ba, ƴan ƙasar basu ci ba, tabbas wasu zasu ci da saka hannunsa. Kuma dole ya amsa tambayoyi akan hakan ranar sakamakon rarrabe ayyukan bayi.

ALLAH ne mai kare bawa akan komai. Amma yana buƙatar wani jajirtaccen mutum kusa da shi da zai dinga rarrabe masa gaskiya da saɓaninta tako wace fuskar data dace. Babu kuma wanda zai iya yin hakan sai mutum ɗaya tak. Mutum ɗayan da ya yarda da shi ɗari bisa ɗari a wannan duniyar. Sai dai fidda sunansa akan muƙamin da yake kallo wani sabon kalubale ne da dole sai ya jure, dan hatta ga shi mai sunan zai iya fuskantar tirjiya kodan sanin da yay masa akan ƙyamatar al'amarin mulki da siyasar ƙasar a bayyane. Dan hakama ya yanke bazai sanar ma kowa ba sai bayan ya ƙaddamar ya kuma zartar. Da wannan tunanin ya saki murmurshi, tare da ɗaukar wayarsa yay kiran ogansa na siyasa.

Bayan sunyi gaisuwa cikin mutunta juna kamar yanda suka saba. Kai tsaye ya furta, "Sir na amince da buƙatun jam'iyya, sai dai da sharaɗi guda ɗaya tak nima daga gare ni".

Murmushi Oga yayi daga can, duk da yasan dama dole ne Janar ya amince ko yaƙi ko yaso. Kamar yanda ya saba cikin kwantar da kai ya ce, "Ina jinka General, kuma ni mai baka goyon bayane akan duk buƙatunka. Musamman a wannan gaɓar da ka faranta min ka saki wannan jayayyar da zata kawo ma kowa masalaha da kwanciyar hankali musamman ni da kuka saka a ysakkiya."

Murmushin takaici shima Janar yayi, kafin ya gyara zama da faɗin, “Ta ɓangarena Chef of staff zai fito”.

Ɗifff numfashin Oga ya ɗauke kamar an daki kansa da guduma. Fin mintuna biyu kafin ya ja iska mai nauyi ya fesar. Bisa ga abinda zuciyarsa ta ayyana masa kawai ya ce, “Shike nan yanda kake so haka za'ayi, zan zauna da su, kuma nasan zasu amsa. Sai dai kayi ƙoƙari kaima ka cika musu alƙawarin su duka”.

“Oga! Ni indai akai min hakan na amince da komai game da muƙaman da wanda ma suke buƙatar a baiwa. Daga yau kuma yanzu nan ma chapter closed kawai”.

“Shike nan ka saurare ni, zuwa safiya in sha ALLAHU zaka ji dukkan bayani”.

Received at 12:22 PM “ALLAH ya kaimu Oga na gode sosai a gaida iyali, mu kwana lafiya”.

“Zasu ji. Amin”.

Kai Janar ya jinjina kamar yana a gabansa shima yay murmushi yana ajiye wayar. Jinsa yake sakayau kamar an sauke masa kaya bisa kai. Sai ma ya miƙe ya shiga bayi dan watsa ruwa a jikinsa. Amma murmushi ya kasa barin fuskarsa saboda hango ƙurar da zai tayar a wannan satin cikin ƙasar dan tako wane fanni bai hango sauƙin al'amarin ba, dole ai kare jini biri jini tsakanin maƙiyan ɓoye dana zahiri.........✍

Received at 12:22 PM

Viewed 2 times

[16/02, 10:59 pm] null: KIƊA A RUWA 3

17

........Anan Gidan Mammah kam Nimrah ta tashi da ɗan dama-dama. Kasancewar ba makaranta suka koma ba suna gama aikin da duk suka san sunayi suka sake komawa barci. Sai wajen ƙarfe goma Mammah tasa Biebah tashinsu suyi kalaci.

Dada baya gidan, dan daga sallar asuba bai dawo ba. A waya ma ya kira Mammah suka gaisa babu jimawa, ya sanar mata yaje wani waje ne amma zai dawo nan kusa. Duk wani motsin Nimrah Mammah na hankalce da shi, ta kuma fahimci a sanyaye take tun jiya. Sannan bata yawan magana. Ganin yanda take kafe mazan gidan da idanu ɗaya bayan ɗaya a kaikaice yasa Mammah fahimtar batun auren da mutanen suka sanar mata ke damunta. Sannan tana son fahimtar waye mijin. Mammah tai ɗan ajiyar zuciya tana ɗauke kanta.

Sauran kuwa fahimtarsu daban data Mammah. Dan sunfi jingina batun kidnapping ɗin da akai mata ne da yanayin nata na shiru-shiru yau. Balle rashin lafiyar Imran ta basu tabbacin sai da akai gumurzu wajen samota, dan haka suka maida hankalinsu akan janta da labaran da zata saki jikinta. Alhamdullahi hakan kuma da suke yayi tasiri. Musamman da taji batun zuwa asibiti duba Lailah da babyn ta. Dama suna fitowa saida ta dangana da sashen Shariffa ta gano Nasir, yana mura ne ba'a son fitowa da shi shiyyasa ta haƙura ta barshi ta dawo.

Umarnin da Mammah ta bata na zuwa ta gyara ɗakin Dadan ya sakata miƙewa, dan a yanzu babu abinda tafi son buƙatar kusanci da shi kamar ɗakin Dada, ta fahimci dukkan abubuwan da take nema suna a ɗakin. Sai da taje ta tattara kayan sharar da duk abinda take buƙata sannan ta tafi. Bayi ta fara shiga domin gyarawa, sai ta samu underwers ɗinsa ajiye alamar zai wanke. Kunya taji ta kamata. Ta duƙar da kai kusan na mintuna uku tana shawarar ta wanke kota barsu a inda ta gani? Wankewar dai akwai ɗunbin kunya a ciki gaskiya, sannan idan ta bari ma tayi gyaran bayin dole zai san ta gani, idan ta tsallake bayin bata gyara ba bata ƙyauta ba, tunda daga shi har Mammah data sakata babu abin rainawarta a ciki.

Da ƙyar ta iya danne zuciyarta ta ɗibesu idanunta a rufe ta zuba cikin worshing machine, ta haɗa ruwan sabulu a ciki ta kunna. Gyaran bayin ta fara, sai da ta kammala tsaf ta dawo wajen worshing machine ɗin daya kashe kansa tun ɗazun ta fara cirosu. Nan ma idanu ta rufe sannan take matsesu ta sake canja ruwa. Sai da ta tabbatar sun mata yanda take so ta ɗauraye ta zuba a dryer ta busar. Sannan ta

kwaso su ta fito. A kujera ta ajiye su ta fara gyaran ɗakin shima. Tayi har mopping ta saka turaren SHUWA INCENSE AND MORE +234 704 229 3387. Har zata tattare kayan sharar sai idanunta suka sauka akan underwers ɗin data wanke. Da kunya ta barsu a wajen yana shigowa ya gani, sai kawai taje ta kwashe ta nufi wadrobe da su dan gyara takai can ta ajiye salin alin. Sai da ta babbuɗe harta gano inda ake ajiyesu sannan tai ƙoƙarin ajiyesu gefe domin fara shiryasu a wajen. Babbar brown envelope dake wajen data ɗorasu ta faɗo, take hotuna dake ciki suka watse a ƙasa. Binsu tai da kallo, sai kuma ta kai duƙe da sauri ganin fuskar Dagger, ba fuskar tasa ce ta ɗauki hankalinta kawai ba ganin wanda suke tare, drivern su ne Malam Buba. Gabanta ya faɗi, tuna itace sanadin haɗa Dagger da malam Buba, ta kuma tabbatar ita Dagger ɗin yazo nema. Sauri-sauri ta kwashe hotunan duka tana kallo. Guda uku duk mutumin ne, ɗaya zai buɗe mota data kasance ta gidan ce ya waigo alamar tabbatar da babu mai kwallon sa, sai kuma dai-dai ya fito daga motar dai, wanda ya fara gani suna cikin motar ne ta gaba aka ɗauka kuma tabbas basu san anyi ba. Sauran hotunan bata gane ƙomai ba, dan wasu mitanene daban.

Bata da zaɓin daya wuce kwashe hotunan Malam Buba da mutum nan da ko sunansa bata sani ba. Dan inta bari Dada ya gani ƙomai na shirinta zai rushe. Gaba ɗaya ta miƙe tana ware iya nasu, sai dai cikin rashin sa'a ta ɗaga rigar jikinta zata saka cikin skirt aka buɗe ƙofar a bazata. Ba ƙaramin daburcewa tayi ba, musamman ganin mai shigowar. Shima da bai san da ita a ciki ba sai yay ɗan tsaii yana kallonta, dan kai tsaye ya gane a firgice take.

Received at 12:22 PM

reacted with ❤Waccan ranar da taga file ɗin nan ne yazo masa a rai. Ya sauke idanunsa ƙasa da take ƙoƙarin cusa abu a jiki. Farin abu ya gani, sai dai bai san minene ba, dan itama da sauri ta saki rigar ganin inda yake kallo.

Nimrah da illahirin jikinta ke tsuma ta aro jarumtar dole ta yafama kanta tana haɗiye yawu masu ƙauri. Cikin gyara yanayin ta ƙwarai da gaske ta ce, “Dada sannu da zuwa. Ina kwana?”. Bata jira amsarsa ba ta juya tana fara ɗaukar underwers ɗin nan.....

Dai-dai lokacin ya ƙaraso wajen, ya tsaya a bayanta gab har tanaji hucinsa. Idanu ta runtse tana karanto addu'ar duk da tazo mata a zuciya. Sai kawai ta fara cusa kayan inda ba'a nan ya dace ba. Hannunta ya riƙo, hakan ya sakata ƙara rumtse ido da cije lips da masifar ƙarfi, ta kuma runtse vest ɗinsa dake a hannunta daya riƙo da nashi.

“Mi kike yi anan?”.

Wani busashshen yawu ta haɗiye da ƙyar, har tana jin kamar yana yanka mata maƙoshi. Da ƙyar ta iya fisgo kalaman bashi amsa da.

“Ina gyara kayan wanki n...ne”.

Kayan hannunta ya kalla na sakanni, sai kuma ya ɗan ja baya daga jikinta. Har tana murnar ta tsira murnar ta koma ciki. Dan kuwa kafaɗunta ya dafa ya juyo da ita suna facing juna. Cikin golden voice ɗinsa dake fita da tsantsar gizago da zurfin iko ya ce, “Buɗe idanun ki”.

Jitai idanun ma sun cika da hawaye kafin ta buɗe. Tadai yi jarumtar haɗiyesu tana sake kame kanta. Koda ta buɗe ta kasa kallonsa gaba ɗaya, sai dai shi tana jin kaifin nashi har a cikin magudanar jininta. Bata san mi yake kallo ba a jikinta, gashi yaƙi yay magana. Ta takura matuƙa saboda kwarjininsa da yanda ya cika mata waje. Jinta take kamar a gaɓar ramin gacci mai matuƙar zurfi, gabanta kuma zaki dake a yunwace ya zuba mata idanu...

“Kayi haƙuri Dada”.

Kalmomin uku suka suɓuto daga cikin bakinta batare data shirya ba.

“Ba sai anyi laifi ake bada haƙuri ba?”.

Idanunta da suka cika da ƙwalla ta ɗago ta kallesa. Zata maida ta risinar ya dakatar da ita cikin umarni.

“Idan suka zubo sai kin kwashesu kin maida.”

Mar-mar ta shiga yi da idanun tana maida hawayen kuwa. Dai-dai yana kai hannu ya ɗaga t-shirt ɗin jikinta baƙa. Dan skirt ne light brown da bai kai mata har ƙasa ba, sai da ya wuce gwiwa sosai, sai baƙar t-shirt ta mata da hoton katon teddy bear a gaban. Sosai kayan sun mata ɗas. Hannu takai da sauri zata hana shi. Ya wani ɗago birkitattun idanunsa da suka sake juyewa saboda halin da yake ciki ya watsa mata. Tare da faɗin, “Zan karya hannun nan”.

Ai da sauri ta janye hannun nata, shi kuma ya ƙarasa ɗage rigar ya jawo hotunan data saƙe a cikin skirt. Maimakon sakin rigar sai ya tsaya yana kallon wani tawwadan ALLAH dake gefen cikin nata babba sosai. Itama jin shiru ta buɗe idanunta, motsin da tai ya saka shi farga shima, sai kawai ya sake rigar yana ƙara tsuke fuska. Hotunan ya fara kallo, guda uku ne, ya zubama fuskar Dagger ido sosai cike da nazari, dan akwai handkachiff a fuskar tashi, ita kanta tsantsar basirar da ALLAH ya bata ne yasa a gani ɗaya ta gane shi. Duk da dai a na cikin mota babu handkachiff ɗin, amma kuma bai fita ba kamar na wajen. Shima ana cikin motar kai tsaye ya gane shi, hakama Malam Buba. Ɗagowa yay yana kallon fuskarta.

“A ina kika gani?”.

Ai ko musu batai ba ta nuna masa envelope ɗin data danne da ƙafafu. Hannu kawai ya miƙa mata. Dole takai duƙe ta ɗakko ta miƙa masa. Ya kalla fuskarta sannan ya buɗe envelope ɗin ya ciro sauran hotunan. Mutane ne mabanbanta har guda shida, yanayin inda aka ɗauka hotunan yay mugun jan hankalinsa. Cikin envelope ɗin ya sake maida hannunsa, sai dai babu komai kuma...

“Waya baki?”.

“Dada wlhy anan na gani”.

Tai maganar tana nuna inda ta ɗauka. Jimm yay na tunani. Tuna da kansa ya ajiyesu jiya ya sashi ɗan furzar da iska. Sai kuma cikin sauke murya ya furta, “Little Shadow kina da hannun ɓarna. Bincike ko?”.

Received at 12:22 PM

Viewed 5 times “ALLAH ba bincike nayi ba Dada. Kawai zan saka kayan nan ne na gani.....”

“Shine kika buɗe tunda kin raina Dada”.

Idanu ta waro sosai da jin furicinsa na ƙarshe tana girgiza kainta. “Wlhy Dada ban raina ka ba, na tuba bazan sake ba”.

Yanda tai maganar hawaye na zubowa ga kunnuwa ta kama ya sashi tsayawa yana kallonta kawai. Dan sai kawai tai masa ƙyau a hakan, har wani babban al'amari na tsarga masa. Dole ya kauda idanun nasa da sauri yana haɗiye yawu. Sai kuma ya bar wajen da sassarfa yana faɗin, “ALLAH ya shirya min ke. Shige ki tafi”.

Ai kafin ma ya rufe baki ta kusa ƙofa, shima sai kawai ya kai zaune yana sake kallon hotunan. A ƙasan zuciyarsa kuwa tunanin yake waye yayo masa wannan aiken?. Hannu yakai ya riƙe goshinsa, sai kuma ya miƙe tsaye ya fara kai-kawo.

Dole yana buƙatar zuwa UNIT ZERO yanzu nan. Hotunan ya maida cikin envelope ɗin, a ya da ya shigo a haka ya sake fita..........✍

Received at 12:22 PM

Viewed

[16/02, 10:59 pm] null: KIƊA A RUWA 3

18

........Lokacin da Dada ke fitowa babu wanda bai bishi da kallo ba a falon. Dan shi bai kalli kowa ba a cikinsu ya fice. Dama sun zagaye Nimrah ne da tambayar miya faru da ita. Dan yanda ya fito ba'a nutsuwarta ba. Duk da tana ta yaƙin danne kanta kuwa. Sai kuma ga Dada ya fito shima ba'a yanda ya shiga ba. Ko kallonsu baiyi ba kuma ya fice.

Ta tabbatar musu babu komai, badan sun yarda ba suka ƙyaleta saboda Mammah data girgiza musu kai alamar su barta. Sam Nimrah bata cikin nutsuwarta,

burinta ta kira Dagger yanzun nan a waya. Sannan tayi magana da Malam Buba. Amma ta rasa ta yanda zata bar falon ma balle yin hakan....

>>>>>★<<<<<

Gudu sosai Dada ke zubawa a titi dan shi ke driving ɗin da kansa. Kusan lokaci guda suka isa da Imran. Kowa na kammala parking ko gaisawa basuyi ba suka nufi hanyar shiga ciki. Daddy Imran ya saka Password ɗin ƙofar, bayan ta gama turance-turancenta daya sakasu matsuwa ta buɗe.

Ko zama basu gama yi ba Dada ya miƙama Imran envelope ɗin. Shima da sauri-sauri ya fiddo hotunan ciki yana kallo ɗaya bayan ɗaya. Sai da ya kai har ƙarshe kafin ya ɗago yana kallon Dadan.

"Tabbas drivers ɗin da suka wuce da kayan can ne. Domin kuwa motocin ne, sannan jejin ne. Waye da wannan aikin?".

"Wannan shine tambayata Imran."

"Shi kuma wannan waye? Nagansa tare da Buba driver?".

Maimakon amsawa miƙewa kawai Dada yayi zuwa ɗakin sirri. Dole Imran ya miƙe yabi bayansa. Anan ma sai da suka saka Password. Suna shiga Imran ya danna wani abu a jikin ƙofar bayan ta rufe, a take haske ya gauraye ko ina. Lallai wannan ɗaki ya tsaru, dole kuma a kira shi da ɗakin sirri. Wani ƙaton bakin allo dake liƙe da hotuna Dada ya nufa, kai tsaye ya ciro wani hoto a layi na biyu ya miƙama Imran.

Sosai Imran ya zubama hoton ido, sai kuma ya kalla Dada. Da ido yay masa nuni da waɗan can hotunan. Baiyi magana ba shima ya sake fiddosu. Cikin sa'a kuwa na cikin mota da fuskar Dagger ke buɗe ne farko. Imran ya kalla hoton ya kalla wanda Dada ya bashi sai kawai ya zaro idanun cikin razani.

"What?! Criminal 0079?!. Kenan da gaske binciken Dabo ya tabbata fitar da su akai basu mutu a haɗarin jirgin ba. Ya ARRAHAMAN. Abin mamaki!. To amma miya haɗa shi da malam Buba kuma?".

"Shi ne ɗan leƙen asirinsa. Sannan Nimrah ta san su".

"Nimrah?! How?".

"Wannan shine tambayata nima? Yarinyar nan ta fara rikita min lissafina Imran. Dan Driver ɗin nan yana ɓoye ainahin fuskarsa ne, tun a ran farko dana fara ganinsa na fahimci hakan. Aikina ne kawai bai biyo takansa ba shiyyasa ban damu da shi ba. Amma ya zama dole yanzu nayi hakan".

Rasa ma abin cewa Imran yayi, dan shi zuciyarsa ma bugawa take da ƙarfi. Ta ina Nimrah zata san Dagger to?.....

"Ina buƙatar su Faro yanzun nan. Dan daga nan zuwa 24h nake son information akan waɗan nan drivers ɗin".

Kai kawai Imran ya jinjina masa yana ciro wayarsa ya fita. Dan anan ɗakin kira baya shiga kai tsaye sai idan sune suka buƙaci hakan...

Zama Dada yay yana furzar da huci. Nimrah ce kawai ke dawo masa a zuciya da yanayinta na daren jiya da na yanzu, dan ɗazun ya danne kansa ne kawai kada ya rikitata. Yana buƙatar shan coffee ko nutsuwarsa zata dai-daita. Dan haka ya miƙe zuwa inda coffee maker take...

+++++++++++++

"Kulu ina abincin su maigadi?".

Kallonta Kulu dake ɗauke da babbar kular abincin gidan zata kai dinning tayi. Sai kuma ta nuna kular abincin su maigadin da Hinde ke zubawa. "Gashi nan Hinde na zubawa."

"Okay bani nakai musu".

Ba Kulu kawai ba, hatta Hinde sai da ta juyo ta kalli Nimrah. Duk da sun san hakan ba wani abu bane sunyi mamaki. Nimrah da taga sun zuba mata ido ta ce, "Akwai matsala ne?".

Da sauri suka shiga girgiza kawuna. Kulu tai ƴar dariya da faɗin, “A'a kawai dai yau naga Ninah abin arzuƙa take ji a gidan namu”.

Received at 12:31 PM Ƙaramar dariya Nimrah tayi tana nufar Hinde. Ta ce, “Kulu dama nasan kin saka min ido ai. Kawai so nake na ɗan miƙe ƙafafu, bana son fita hakan nan kuma Mammah tai magana”.

Sun gamsu da bayanin nata, dan haka Hinde na kammala zuba abincin ta tura mata kular. “Bari to na ɗauka miki plates ɗin ko?”.

“A'a barsu zan dawo na ɗauka”.

Cewar Nimrah tana ɗaukar abincin ta fita. Da lafiya lafiya ne zatace ya mata nauyi. Duk da kular ba irin ƙatuwar nan bace ba kuwa. Addu'a take ALLAH yasa ta samu baba driver harta ƙaraso. Aiko ta sauke ajiyar zuciya mai ƙarfi ganinsa zaune shi kaɗai a kujera yana latsa waya. Daga can gefe maigadi na alwala. Sai Sanda na barci a barandar ɗakinsu ya juya baya. Kai tsaye wajen Malam Buba ta nufa. Duk da yanda take jin bugun zuciyarta na ƙaruwa, hakan ya zame mata jiki a duk lokacin data kusanceshi. Tunma yana damunta har ya daina. Ƙasa takai duƙe tana ajiye kular da gaishe shi. Idanunsa a kanta ya amsa, itama sai ta ɗan ɗago ta kalleshi. Cikin raɗa ta furta, “Baba mutumin kwanaki yazo nemana da bana nan ko?”.

Sosai gaban Malam Buba ya faɗi, a ransa yace (A ina tasan hakan?) a zahiri kuwa sai ya fara inda-inda.

“Baba ka faɗa min dan akwai matsala ne. Wani munafiki ya ɗauki hotonka kai da shi kuna a mota ya kawo ma Dada......”

Kaɗan ya rage zuciyar Malam Buba ya fito ta baki. Ba arziƙi yaji fitsari na neman zubo masa. Ita kanta Nimrah taga firgitarsa a zahiri. Amma sai fahimtarta tasha banban da halin da yake ciki. Ta cigaba da faɗin, “Wlhy kuwa Baba nima hankalina ya tashi. Shiyyasa tun ɗazun nake son fitowa na amshi wayar Sanda na kira shi.”

Ai malam Buba bai ma san ya furta, “I...ina da lambarshi U...u..w...a. amshi maza kirashi. Idan kuma ni na kira shi to”.

“Baba ka tabbatar wadda zaka sameshi ce yanzu?”..

“In sha ALLAHU”.

“To Baba dan ALLAH kayi da sauri kawai ka kirashi kai. Dan Dada ya fita da hotunan, kuma ban san mi zaiyi akai ba”.

Kansa ya jinjina mata yana haɗiye yawun dake neman sarƙe masa numfashi. Ita kuma tabar wajen...

★Nimran na shigowa falon Abees daya fito a bedroom ɗin Mammah ya tareta da faɗin, “Aunty Mammah tace kizo”.

Kanta ta jinjina masa, sai kuma ta ce, “Muje to”.

“Aunty zanje wajen Mamy ne, ta aikoni na kawoma Mammah abu”.

Anan ma kan nata kawai ta jinjina masa. Ya wuce ita kuma ta shige bedroom ɗin Mammah. Afeef dake zaune a falon yana binta da kallon harara ya taɓe baki. Sai kuma ya saki murmurshi a fili ya furta, “Shegiya ƴar iska. Na kusa maganin ki ai. Sai na tona muku asiri a gidan nan. Dama na faɗa miki, idan na tashi ramawa sai na miki mai zafin da har ki mutu bazaki manta da ni ba.”

Daga haka ya miƙe ya haura staircase.

Nimrah kam ta samu Mammah na waya. Dan haka ta nema waje ta zauna tana jiranta. Sai da ta kammala sannan ta sake miƙewa ta koma kusa da Mammah ɗin. Mammah ta riƙota tana kwantar da kanta a kafaɗarta. Sai da ta shafa fuskarta cikin damuwa ta ce, “Autana duk kin rame min a ido. Inaga ɗurar abinci zan fara miki gaskiya”.

Murmurshi Nimrah tayi, ta kama hannun Mammah ta sumbata. Cikin shagwaɓa ta ce, “Mammah idan kikai min ɗura zan zama ƙatuwa ALLAH. Ni kuma bama son ƙiba no da Buddy.”

“Uhm-uhm yaran zamani sai a barku. Yanzu miye abin gudu a ƙiba kuma?”.

“Mammah ALLAH ƙiba ciwo ce. Mutanenmu ne kawai ke ganin sai kayi ƙiba wai kake jin daɗin rayuwa. Amma ƙiba ai ba abin so bace.”

Mammah tai dariya kawai da sake shafa kumatunta. Sai kuma cikin kulawa da iya sarrafa zuciyar yaro ta ce, “Tun juya nake son mu zauna ki bani labari, amma iyayenki sun zagayeki. Bani labarin miya faru da kika fita ranar?”.

Daga Ruƙayya har Nimrah basu san ɓoyema Mammah damuwa ko magana ba. Ko Dagger yaci galaba a kan Nimrah ne saboda barazanar kashe Ruƙayya da yay mata. A yanzu ma akwai dalilan da bazata iya sanarma Mammah komai da komai ba. Amma akwai abinda bazata iya ɓoye mata ba. Sannan tana son sanin wanene akai mata aure da shi, idan taji a bakin Mammah kuma zatafi gane abinda ake nufi.
Received at 12:31 PMDan haka ta gyara zama ta fara bama Mammah labari tiryan-tiryan. Har batun fashewar bomb bata ɓoye komai ba. Tadai yanke labarin daga inda su Leo suka fiddata a gidan da aka fara kaita, duk abinda ya faru a gaba bata faɗa ba. Ta share hawayen da suka zubo mata, cikin rawar murya ta ce, “Mammah sunce an min aure, kuma assignment ne naje na bincika waye mijin da kaina.”

Sosai ƙirjin Mammah ke duka, amma sai ta danne tana murmurshi da kamo Nimrah ta sake rungumewa a jikinta tana share mata hawaye.

“To shine kuma abin kuka Autar Mammanta. Ai aure alkairi ne, sannan Rahama ne. Ɗan gata kuma akemawa da ƙarancin shekaru. Ke da Ruƙayya kuma ƴan gatan Mammah da iyayenku ne. Tabbas basuyi ƙarya ba ke matar aure ce. Kuma kina da shekara bakwai aka ɗaura......”

“Mammah saboda mi?”.

“Saboda ke ƴar gata ce Nimrah. Duk da dai akwai ainahin abinda ya faru a lokacin, amma bazan faɗa miki ba sai kin ƙara girma”.

“Mammah waye mijin?”........✍
Received at 12:31 PM
2 people reacted
[16/02, 10:59 pm] null: KIƊA A RUWA 3

19

........Sosai Mammah tai murmurshi mai yalwa da hango ƙuruciyar Nimrah a fili. Sai kuma ta shafa kanta. “Miyasa kike son ji tun yanzu? Kiyi haƙuri zaki sanshi. In sha ALLAHU kuma zakiyi farin ciki.”

Kai Nimrah ta jinjina kawai tana sauke ajiyar zuciya. Sai dai taso tasan wanene mijin, amma bazata iya jayayya da Mammah ba. Zata cigaba da haƙuri, da juriya har lokacin da Mammah tace ɗin yayi. Mammah data fahimci halin da take ciki, sai ta ƙara gyara zama ta shiga lallashinta da nasiha mai tsada da daraja. Ta yanda a hankali komai ke shigar Nimrah tamkar ruwan allura a jijiyoyin jiki. Daga ƙarshe Mammah ta fara bata labarin tarihin rayuwarta. Ai gaba ɗaya sai Nimrah ta shagala, sai dai daga lokacin da tazo gaɓar rasuwar Baba Abdul-rasheed da ciwon Mama Yakura zuwa rasuwarta duk Nimrah ta rikice da kukan tashin hankali, ita kanta Mammah hawaye take, tama kasa ci-gaba. Sai da sukai kuka sosai sannan Mammah ta ƙarasa mata har ƙarshe lokacin da suka dawo garin nan da zama.

Nimrah ta share hawaye, idanunta jajur ta furta, “Mammah kun sha wahala ke da Dada. Amma miyasa tun sanda aka rufeshi na farko baki hanashi aikin soja ba?”.

Fuskar Mammah da murmushi ta shafa kan Nimrah. “Nimrah kowanne bawa da irin ƙaddararsa, kowa kuma da irin rayuwar da UBANGIJI ya tsara masa. Dadan ku na son aikin soja, kuma na gamsu da jajircewarsa akan ƴan uwansa marasa ƙarfi irinmu da yake ƙoƙarin bama kariya. Hanashi ba itace masalaha ba addu'a ce komai”.

“Hakane Mammah. Nima yau naji ina son nayi aikin soja”.

Yanzu kam sosai Mammah tai dariya da faɗin, “Soja fa Auta?”.

“Eh Mammah, ina son na zama kamar Dada da Daddy”.

“To bazance a'a ba, muyi addu'a ALLAH ya zaɓa mana abinda yafi alkairi”.

“In sha ALLAHU zanyi. Amma Mammah a ina shi ƙauyukan Bankaura ɗin da akaima kisan gilla ɗin suke? Ina son zuwa garin”.

Yanzu kam shiru Mammah tai tana kallonta. Ta bata labarin komai daya shafi su da al'amarin Muhammad, har abinda ya faru a ƙyauyukan Bankaura daya zama sanadin rufe Dada na shekaru 8. Amma bata gaya mata komai daya shafeta ba balle tasan ita ƴar wannan yanki ce, tayi hakan ne kuma dan tafi son Muhammad ya sanar mata komai da kansa.....

“Kinji Mammah”.

Nimrah ta katse mata tunani. Ajiyar zuciya Mammah ta sauke. Cikin jinjina mata kai ta ce, “Saboda mi kike son zuwa?”.

Nimrah tai murmushi tana haɗiye abinda ke ranta. Cikin nuna rashin damuwa ta ce, “Mammah haka nan kawai. Dan wani ma tunani nake yi...”

“Na mi?”.

“Zan fara rubutu a kansu. Mammah bayan aikin soja yanzu na ƙara jin ina son zama MARUBUCIYA”.......

×××××××××××

“Wlhy Daddy da gaske nake maka. Har video ma na musu jiya. Ai tun randa ya shiga ɗakinsu da daddare na fara saka musu ido. Sai naga ita ɗayar bata shiga ɗakinsa da daddare kamar yanda wannan shegiyar keyi. Aiko jiya dubunsu ta cika......”

“Kaga katse kiran nan ka tura min video ɗin”.

Babu musu Afeef ya katse kiran, yana wata ƴar dariyar ƙeta ya tura videon da jiya yay ma Dada da Nimrah batare da sun sani ba. Sai da ya kammala ya juyo yana kallon Hanoon datai tagumi...

“Afeef wai baka jin tsoro, mutum nan daga ganinsa wlhy ba imani zai yi ba. Itafa shaidar zina ance sai ka gani da idonka...”

“Ke ai dama wawuya ce, dan kina son shi shiyyasa ma kike kamar baki yarda da abinda na nuna miki ba. To kar ki yarda ɗin, ni ina ruwana da wani a addini sai an gani da ido. Sannan da kike wani magana baida imani ya kashe ni mana. Kuma ai itace taja masa, dama na rantse sai na mata abinda bazata taɓa mantawa dani ba.....”

“To amma tunda itace ta maka laifin ka rama a kanta mana ba shi ba. Sannan kai ne wawa, kuma ina ji maka tsoron Daddy ya fitar da maganar nan ta dawo cikin gidan nan kaine zaka sha wahala”.

Tana gama faɗa ta fice a ɗakin. Da kallo ya bita zuciyarsa na wani irin zafi. Sai kuma yay ƙwafa....

Received at 12:31 P ★A ɓangaren Uncle Tasi'u yana kallon video yana faman jinjina kai da sakin murmushi. Jinsa yake rai fess. Dan kuwa ya samu makamin da zai sami abinda yake so gun Adda A'isha. Duk da wani gefen zuciyarsa na gargaɗinsa akan halin Haysam. Amma wadda ke zugashi na dannewa.

Fitowa yay daga cikin videon, kai tsaye ya sayi ticket ta online, dan dole ne ya je ƙasar haihuwarsa. Zuwa na bazata a yau ɗin nan. Daɗi sosai yaji na samu jirgi mai tashi nan da awanni goma. Dan haka babu ɓata lokaci ya hau shiri......

>>>>>>>%<<<<<<

Washe gari safiyar juma'a aka sallamo Lailah mai jego, duk da jiya su Nimrah tun yamma har dare suna asibitin tuni suka rikice da farin ciki. Dan sun tattare inasu-inasu sun koma sashen su Lailah gaba ɗaya. Tunda dai jarirai sun zama biyu sai aka raba rigima kowa ya ɗauki ɗaya.

Sosai farin cikin kasancewa da babys ya kwashe rabin hankalinsu acan. Sai dai wani kaso na tunanin Nimrah nakan Dada ne. Dan tun fitar jiya da yayi bayan ya

amshi hotuna a hannunta har yanzu bai dawo gidan ba. Ga Baba Driver ma tun jiyan bata sake ganinsa ba. Abin ya dameta ƙwarai da gaske, batare da ita kanta tasan dalilin yin hakan ba. Bayan sallar la'asar sai ga Mu'azz ya shigo, dawowarsa kenan daga makaranta. Bai ko shiga sashen Mammah ba yayo nan shima. Suna cikin caftarsu Aunty Shariffa na rabon faɗan akai baƙi ƴan barka. Dole suka fito dan basu waje kasancewar suna da yawa.

Mu'azz ne ya takali Ruky sabuwar rigima, hakan yasa ta bishi da gudu. Nimrah uwar zuga ta bisu tana faɗin, “Yauwa Buddy na kada ki raga masa”. Tana maganar ne tana dariya har suka shigo falon. Da yake suna gabanta sun rigata. Ta shigo ta samesu tsaye cak, sai kuma muryar Mammah dake magana kamar cikin ɓacin rai ta daki kunnenta. Itama tsayawa tai dan in kaji Mammah na faɗa an kaita bango ne.

“Nace Tasi'u mi kake nufi?!”.

Furucin Mammah ya sake dukan kunnuwansu. Sai lokacin Nimrah ta fahimci ashe baƙo sukayi a gidan. Ba kuma kowa bane face Uncle ɗin nan da yazo kwanaki kuma Baban su Finga-fiyau kamar yanda Mammah ta sanar musu. Yana zaune a kujera gabansa da abinci da aka jera a Center table. Sai Mammah da itama ke zaunen tana facing ɗinsa. Da waya a hannunta fuskarta kuwa yanayi ne da zasu rantse basu taɓa gani ba...

Gwaggo Khadijah da Gwaggo Alawiyya da suka fito suma saboda tsawar Mammah suka ƙarasa inda suke. Gwaggo Khadijah ta zaune tana riƙo hannun Mammah da faɗin, “Ayi haƙuri Maman Ma'aruff. Mike faruwa ne?”.

Maimakon Mammah ta bata amsa sai Uncle Tasi'u ne ya amsa mata cikin ɓacin rai. “Yaya ki barta, na rasa miyasa Adda bata son gaskiya akan yaranta, dan fa kawai nace mata gyara kayanka, shine zai zama sauke mu raba......”

“Karka kawo min zancen banza zancen wofi Tasi'u”. Mammah ta katse shi a tsawace fiye da tsawar ɗazun da sai da ta saka su Nimrah zabura. Cikin nuna shi da yatsa tare da wurga masa wayarsa dake hannunta ta cigaba da faɗin, “Mika sani akan yarana da har zaka yanke musu hukunci? Dama ka kawo min yaranka gidana dan su dinga saka maka ido akan al'amarin mu.....”

Gwaggo Khadijah da hankalinta ya ƙara tashi ta riƙo Mammah. “A'isha dan ALLAH ya isa haka. Ya kuke abu kamar wasu ƙananun yara, wai mike faruwa ne? Ku fiddani a duhu....”

Kuka sosai Mammah ta fashe da shi, ta nuna wayar Uncle Tasi'u dake yashe a ƙasa. “Yaya Khadijah na gaji da halin Tasi'u wlhy, ki faɗa masa in dai ba alkairi ya dawo dashi cikin rayuwata da zuri'ata ba dan ALLAH ya tattara yaransa su koma. Wai ki duba video cikin yaran nan wani ya ɗauka na Muhammad da Nimrah, shine yazo yana zancen banza akan hakan. Wai Muhammad na neman Nimrah...” babu wanda bai razana ba a falon, Mammah ta cigaba da faɗin, “To bari kaji kai da masu ɗaukar Videon ko zaku dawo cikin hankalinku. Nimrah MATAR Muhammad ce. An ɗaura musu AURE tun tana da shekara bakwai. Sai ka sake wani shirin”.

Received at 12:31 PM

reacted with ❤ Wani irin duka kan Nimrah yayi tamkar an saki irin tsawar nan mai girgiza gari a cikin tsakiyar ruwan da ke sauka da manya-manyan ƙanƙara. Kalaman Mammah suka wani irin sake maimaita kansu a cikin illahirin duk wata ƙofa dake amsa suna ƙofa a cikin jikinta. (Nimrah MATAR Muhammad ce. An ɗaura musu AURE tun tana da shekara bakwai). Ai sai kawai tayi luuuuu zata zube. Da wani irin ihu su Ruƙayya da sukai sumar tsaye dan suma kalmar ta dake su da girgiza su suka zabure kanta. Sai kuma suka tsaya cakk sakamakon ganin Dada da babu wanda zaice ga sanda ya shigo falon, da ga gefensa Daddy Imran ne. Nimrah da ta tafi zata zube ya tare da jikinsa. Yana tsaye ne ƙyam akan ƙafafunsa, hannunsa ɗaya tallefe da bayanta saboda tareta da yayi, ɗayan na cikin aljihu. Sai dai idanunsa da sukai masifar juyewa da wani irin hargitsatstsen yanayi tsaye suke ƙyam akan Uncle Tasi'u da shima ya juyo wajen kamar su Mammah saboda ihun Mu'azz da Ruƙayya...

Tuni Hanoon da Afeef da Dayyan dake laɓe sun fito suma. Ganin Dada da basuyi zato ba tunda sun san tun jiya baya gidan tuni ya firgitasu. Dan Afeef ya jiƙe sharaf da zufa ga icayi na neman kufce mas a wando.........✍

Afeef tsuntsun da yaja ruwa ba shi ruwa ke doka ba□. Ka ragema su Mammah aiki □ □□..........A hankali Daddy Imran da shima ke kallon Uncle Tasi'u cike da ɗunbin mamaki dan duk abinda Mammah ta faɗa a kunensu ne. Shigowar su Nimrah babu jimawa suka shigo. Hakan ta faru ne kuma saboda su ta gaba suka shigo, su Nimrah kuwa daga sashen su Ma'aruff ta kofar baya suka shigo. Dan haka basu san da zuwansu gidan ba.

Idanun nasa da shima suka kaɗe ya janye daga kan Uncle Tasi'u ya maida kan Dada. Yasan waye Zakinsa, dan haka ya ɗan sauke numfashi da kai hannu ya akan kafaɗarsa ya ɗan bubbuga alamar lallashi. A hankali kuwa Dada ya juyo ya zuba masa idanun nasa, sai kuma ya lumshe su ya sake buɗewa. Batare da yace ma kowa uffan ba dai-dai Uncle Tasi'u da jikinsa ke rawa na zaburowa da nufin zuwa inda yake lips ɗinsa na motsi alamar magana zai masa kawai Dada ya ɗaga Nimrah dake a sume cak yau wucewarsa.

Ai ba Mammah data san halin kayanta ba hatta su Gwaggo Khadijah sai da suka ɗan waro idanu waje. Dan asalin manna wulaƙanci gangariya da babu gauraye Dadan yay ma Uncle Tasi'un. Imran ya duƙar da kai yana danne murmushin dake neman suɓuce masa da ƙyar. Sai kuma ya ɗan sake ɗagowa ya kalla Dadan dake haura staircase da wani irin salon ainahin jarumai. Sai ka rantse ba mutum ya ɗauka ba, dan babu alamar yana jin nauyinta duk da tana a sume ne....

Da wani irin sauri itama Nabeeha ta dafe kanta dake sara mata, sai kuma tai ƙoƙarin riƙo Ruky dake kusa da ita. Da sauri Ruƙayya ta juyo, hakama kowa na falon da sai yanzu suma suka farga da ita. Ashe itama komai a kunnen nata ya faru, dan su Amima na balcony na sashenta motar su Dada ta shigo, shine Rayhana ta kirata a waya ta sanar mata. Sai ko gata ta fito da hanzari, sanda take fitowa su kuma har sun kusa sashen Mammah. Sun shigo kenan itama ta afko amma taja ta tsaya ganin abinda ke faruwa alamar babu lafiya saboda ganin Mammah na kuka. Sai kuma ga bayani taji kamar yanda kowa ya ji. Zuciyarta na neman tarwatsewa duk da tasan wannan amma sai taji kamar ita Mammah ke ma bitar tunatarwar mijin Haysam mijin Ninrah ne ƴar cikinta da da'ace tana zuwa gidan ta samu ciki zata haifi kamar Mu'azz ne. Dai-dai ta ɗago zata kalla Dada dake gabanta kaɗan kawai taga ya matsa da wani irin zafin nama ya taro wadda keta gabansa kaɗan Da sai da ta faɗa jikinsa sannan taga fuskar Nimrah. Sai kawai taji numfashinta ya ɗauke komai ya tsaya mata cak, shine bata dawo a hayyacinta ba sai yanzu, duk da yanzun ma a wani yanayi ne saboda ganin abinda Dadan ya aikata kuma ko'a jikinsa ya ɗauki ƴar yarinya a hannu a gaban kowa ya haura sama inda kowa yasan ɗakinsa zai kaita.....

___

A dai-dai kuma wannan lokacin cikin hikimar UBANGIJI wani al'amari mai girgiza ƙasar da al'ummar cikinta, dama ɓoyayyun munafukai yay amsa kuwwa. Domin kuwa bayani ne mai girma, mai tsauri, daban al'ajabi ya fita daga fadar shubagaban ƙasa akan sunayen waɗanda aka bama muƙamai masu daraja da kima da zasuyi aiki a wannan gwamnatin tasa.

Akwai manyan ministoci guda takwas da sunansu ya fara fita, sai babban sakatare. Sai NATIONAL SECURITY ADVISOR (NSA) . da CHEF OF STAFF. Ba muƙaman ne suka girgiza ƙasar ba, sunayen mutanen da aka bama muƙaman biyun ƙarshe ne. Mr. Haysam Abdul-rasheed Shehu Kobi is appointed as the (Chief of Staff to the President). & Mr. Imran Abbas is appointed as the National Security Advisor (NSA).

Gan-gan-gan-gan. Wannan fa shine ainahin tashin bomb mai kai goma sha biyu. Shugaban ƙasa kuma na kammala bada umarnin sanarwar dan tun jiya ya rattaɓa

hannu a gidansa yau ya ƙaddamar a yanzu kuma ƙarfe huɗu na yamma. Yana badawa kuma yay shigewarsa gida. Gashi yau juma'a ce, za'a shiga hutun weekend.

Wannan fa shine (Tarwatsa wara wari jikan Tafida!, rai ya daɗe rai yayi ma alfarma. Kaga mazan aiki sun zo. Ya cika sittin mai ban mamaki....) Aba Nasiru Sarkin waƙa shawara ya yoma shugaban ƙasa Yusuf Shu'aibu Tafida irin wannan waƙar sak ta sarkin Kano shima. (Kai ku bamu kiɗan janaral a sama. Masu gudu su gudu, sai Baba Tafida, sai Baba Tafida. Bana dai janar shine a sama... Amma a KIDA A RUWA..... Masu gudu su gudu.
Received at 12:31 PMKu faɗama shaggun can su ware😂).

Tabbas Janar ma KIDA A RUWA ne MAI TADA HANKALIN DODONNI

Jama'a to ALLAH ya taroni, sanyi fa ya kankama sai kun haɗa da haƙuri magana ta ALLAH. Yo irin wannan waƙoƙi haka kamar babana ne Janar ɗin😎.

••••••••••••••••

"Amma kai Mole wawa ne, jaki ma dabbul arab. Shine sai yanzu kake gaya min?".

Wani irin tafasa zuciyar Malam Buba ta shiga yi a cikin ƙirjinsa. Ya kalla Dagger da idanunsa da suka kaɗe jazur saboda yanda kalamansa sukai masa zafi matuƙa. Amma sai ya danne a kan harshe ya furta. "Oga ya kake so nayi?. Tun jiya da Uwa ta faɗa min fa na baro gidan nake nemanka. Yanzu haka kalla jakkata anan na gama yanke binka sansani idan har ban sameka na ƙarshen nan ba. Sai kuma nayi sa'a kaga saƙona kazo."

Gaba ɗaya Dagger ji yake kamar kansa zai tarwatse dan tashin hankali. Ya dunƙule hannu da masifar ƙarfi ya daki bangon ɗakin Malam Buba yana wani irin ƙaraji daya saka Malam Buba zaro idanu yana kallon ƙofa. Duk da saida ya rufe windows da ƙofar tunda Dagger ya shigo yana tsoron wani yaji ihunsa a gida... "Oga kayi a hankali mana kada wani yaji. A ganina ba rikita kai bane mafita. Tunanin abinda ya dace. Kasan dai tunda Uwa tace taga hoton nan mutumin nan bazai ƙyale mu ba. Dole zai fara bincike akanmu......"

"Shiyyasa nace kai wawa ne Mole. Idan kai jaki ne shi ba irinka bane ai. A zatonka zai mance da fuskata ne har ya zauna wani bincike a kaina? Kaima badan wannan gemu da sajen ɓadda kamar daka sanya ba da wannan fentin da kake ma kanka an gaya maka bazai gane ka ba ne tun a ranar farko? Ko a yanzu na fara tantamar guy ɗin nan bai gane ka ba, ya barka ne kawai a cikin takunsa."

Tsuttt fitsarin tashin hankali ya zubo jikin Mole. Jikinsa na karkarwa ya ce, "Amma Oga miyyasa baka taɓa faɗa min haka ba?".

Wata muguwar Harara Dagger ya zuba masa kawai, batare da yace komai ba ya hankaɗesa ya buɗe ƙofar ɗakin ya fice abinsa. Ai gaba ɗaya sai Mole ya sake jin gudawa ma na neman zubo masa ba fitsari ba. Tuni ya zabura ya ɗauki jakarsa da dama ya haɗa komai nashi yabi bayan Dagger. Yana fitowa ya samu har ya shiga mota. Ai shima sai kawai ya buɗe ya shige wufff kusa da shi. Ko kallonsa Dagger baiyi ba ya tada motar yabar ƙofar gidan a guje.....

<<<<<<%>>>>>>

"Tabbas Oga magana ta tabbata. Nimrah matarsa ce. Dan yanzun nan Mammah ta faɗa da bakinta a gabanmu. Sakamakon cikin baƙin yaran nan sun naɗi video sun turama babansu cewar Dada na nema Nimrah. Shi ne shi kuma ya ɗakko ƙafa ya taho, yanzu dai haka shi ya ɗauketa yayi ɗakinsa da ita. Nan kuma falon ya birkice ga matarsa nan uwargidansa ta yanke jiki ta faɗi tana abu kamar mai farfaɗiya ƙannenta sun ɗauketa zuwa sashen ta".

"Hummm kice anzo dai-dai inda nake so?".

“Anzo kuwa ƙwarai da gaske Sir!”.
“ALLAH yay miki albarka, sai ki kasance cikin shiri dan aiki ki gab yake da fa ƙarewa. Lokacin bayyanata yayi.”
“In sha ALLAHU Sir”.
Ta faɗa cikin ƙamewa da salute ɗinsa tamkar tana a gabansa ne. Shima daga can sai ya saki murmurshi da jinjina mata kansa tamkar yana a gaban nata ya ce, “Proud of you dear”.
“Thank you Sir! Proud of you too.”
Murmurshi kawai yay mata da har taji fitar sautinsa a cikin kunneta, daga haka ya yanke wayar, itama sai ta ajiye tana sauke ajiyar zuciya. Sai dai kuma cak numfashinta ya ɗauke sakamakon fitowar ƴar uwarta daga bayi da bata san da ita ba. Yanda take kallonta cikin ido ya sakata fahimtar duk taji wayar tata. A rikice ta zabura kanta, sai dai da sauri ta ɗaga mata hannu alamar karma tazo gareta. Dole ta tsaya cak suna kallon juna tamkar tsaiwar zakaru...........✍

Tooooo barkanmu da juma'a. 🤗Dada ya shige da ƴar mutane marainiyar ALLAH ɗaki.

Ga shugaban ƙasa yayi bombing zukatan munafukai🤔😊🤗.

Ga Dagger da Mole a kwale-kwale😂🤣.

Ga Nabeeha uwargida mai capacity na farfaɗiya🤣🤣.

Ga Uncle Tasi'u da ƴaƴansa a lukutar masifa😱.

Ga ƴar leƙen asirin mai aiki a ƙaulani🤣🤣.

Kai wannan sati yazo da alheri🤗.
*********************** ⬇ ***************************
*********** Ai Hausa Novels ****************
************************** ⬆ ***********************

DOWNLOAD More complete Hausa Novels, Education Books, Adventure, Drama, Mystery, Religion, Fiction, Non-Fiction, Romance, Meimor, True Life Stories & Others from our blog.

Visit > https://www.aihausanovels.com.ng

Ka tura mana sako ta adireshinmu na email, domin tuntubarmu ko turo mana hausa novel ko kuma post.

Email > aihausabooks@gmail.com

******* FOLLOW US ******

Facebook: Ai Hausa Novels

Twitter: Ai Hausa Novels

Telegram Channel: https://t.me/Aihausanovels

WhatsApp Number: 09017242889

Haka kuma domin shiga kowanne daga cikinsu za ku iya ziyartar shafin ku yi search na AI HAUSA NOVELS, hatta facebook group dinmu ma za ku samu.

********************** ⬇ **************************
*************** Ai Hausa Novels ****************
********************** ⬆ **************************

[4/2, 10:27 PM] null: .........A hankali Daddy Imran da shima ke kallon Uncle Tasi'u cike da ɗunbin mamaki dan duk abinda Mammah ta faɗa a kunensu ne. Shigowar su Nimrah babu jimawa suka shigo. Hakan ta faru ne kuma saboda su ta gaba suka shigo, su Nimrah kuwa daga sashen su Ma'aruff ta kofar baya suka shigo. Dan haka basu san da zuwansu gidan ba.

Idanun nasa da shima suka kaɗe ya janye daga kan Uncle Tasi'u ya maida kan Dada. Yasan waye Zakinsa, dan haka ya ɗan sauke numfashi da kai hannu ya akan kafaɗarsa ya ɗan bubbuga alamar lallashi. A hankali kuwa Dada ya juyo ya zuba masa idanun nasa, sai kuma ya lumshe su ya sake buɗewa. Batare da yace ma kowa uffan ba dai-dai Uncle Tasi'u da jikinsa ke rawa na zaburowa da nufin zuwa inda yake lips ɗinsa na motsi alamar magana zai masa kawai Dada ya ɗaga Nimrah dake a sume cak yau wucewarsa.

Ai ba Mammah data san halin kayanta ba hatta su Gwaggo Khadijah sai da suka ɗan waro idanu waje. Dan asalin manna wulaƙanci gangariya da babu gauraye Dadan yay ma Uncle Tasi'un. Imran ya duƙar da kai yana danne murmushin dake neman suɓuce masa da ƙyar. Sai kuma ya ɗan sake ɗagowa ya kalla Dadan dake haura staircase da wani irin salon ainahin jarumai. Sai ka rantse ba mutum ya ɗauka ba, dan babu alamar yana jin nauyinta duk da tana a sume ne....

Da wani irin sauri itama Nabeeha ta dafe kanta dake sara mata, sai kuma tai ƙoƙarin riƙo Ruky dake kusa da ita. Da sauri Ruƙayya ta juyo, hakama kowa na falon da sai yanzu suma suka farga da ita. Ashe itama komai a kunnen nata ya faru, dan su Amima na balcony na sashenta motar su Dada ta shigo, shine Rayhana ta kirata a waya ta sanar mata. Sai ko gata ta fito da hanzari, sanda take fitowa su kuma har sun kusa sashen Mammah. Sun shigo kenan itama ta afko amma taja ta tsaya ganin abinda ke faruwa alamar babu lafiya saboda ganin Mammah na kuka. Sai kuma ga bayani taji kamar yanda kowa ya ji. Zuciyarta na neman tarwatsewa duk da tasan wannan amma sai taji kamar ita Mammah ke ma bitar tunatarwar mijin Haysam mijin Ninrah ne ƴar cikinta da da'ace tana zuwa gidan ta samu ciki zata haifi kamar Mu'azz ne. Dai-dai ta ɗago zata kalla Dada dake gabanta kaɗan kawai taga ya matsa da wani irin zafin nama ya taro wadda keta gabansa kaɗan Da sai da ta faɗa jikinsa sannan taga fuskar Nimrah. Sai kawai taji numfashinta ya ɗauke komai ya tsaya mata cak, shine bata dawo a hayyacinta ba sai yanzu, duk da yanzun ma a wani yanayi ne saboda ganin abinda Dadan ya aikata kuma ko'a jikinsa ya ɗauki ƴar yarinya a hannu a gaban kowa ya haura sama inda kowa yasan ɗakinsa zai kaita.....

___

A dai-dai kuma wannan lokacin cikin hikimar UBANGIJI wani al'amari mai girgiza ƙasar da al'ummar cikinta, dama ɓoyayyun munafukai yay amsa kuwwa. Domin kuwa bayani ne mai girma, mai tsauri, daban al'ajabi ya fita daga fadar shubagaban ƙasa akan sunayen waɗanda aka bama muƙamai masu daraja da kima da zasuyi aiki a wannan gwamnatin tasa.

Akwai manyan ministoci guda takwas da sunansu ya fara fita, sai babban sakatare. Sai NATIONAL SECURITY ADVISOR (NSA) . da CHEF OF STAFF. Ba muƙaman ne suka girgiza ƙasar ba, sunayen mutanen da aka bama muƙaman biyun ƙarshe ne. Mr. Haysam Abdul-rasheed Shehu Kobi is appointed as the (Chief of Staff to the President). & Mr. Imran Abbas is appointed as the National Security Advisor (NSA).

Gan-gan-gan-gan. Wannan fa shine ainahin tashin bomb mai kai goma sha biyu. Shugaban ƙasa kuma na kammala bada umarnin sanarwar dan tun jiya ya rattaɓa

hannu a gidansa yau ya ƙaddamar a yanzu kuma ƙarfe huɗu na yamma. Yana badawa kuma yay shigewarsa gida. Gashi yau juma'a ce, za'a shiga hutun weekend.

Wannan fa shine (Tarwatsa wara wari jikan Tafida!, rai ya daɗe rai yayi ma alfarma. Kaga mazan aiki sun zo. Ya cika sittin mai ban mamaki□....) Aba Nasiru Sarkin waƙa shawara ya yoma shugaban ƙasa Yusuf Shu'aibu Tafida irin wannan waƙar sak ta sarkin Kano shima. (Kai ku bamu kiɗan janaral a sama. Masu gudu su gudu, sai Baba Tafida, sai Baba Tafida. Bana dai janar shine a sama... Amma a KIDA A RUWA..... Masu gudu su gudu.
Received at 12:31 PMKu faɗama shaggun can su ware□□□😂□).

Tabbas Janar ma KIDA A RUWA ne MAI TADA HANKALIN DODONNI

Jama'a to ALLAH ya taroni□, sanyi fa ya kankama sai kun haɗa da haƙuri magana ta ALLAH. Yo irin wannan waƙoƙi haka kamar babana ne Janar ɗin😎□□□.

••••••••••••••••

“Amma kai Mole wawa ne, jaki ma dabbul arab. Shine sai yanzu kake gaya min?”.

Wani irin tafasa zuciyar Malam Buba ta shiga yi a cikin ƙirjinsa. Ya kalla Dagger da idanunsa da suka kaɗe jazur saboda yanda kalamansa sukai masa zafi matuƙa. Amma sai ya danne a kan harshe ya furta. “Oga ya kake so nayi?. Tun jiya da Uwa ta faɗa min fa na baro gidan nake nemanka. Yanzu haka kalla jakkata anan na gama yanke binka sansani idan har ban sameka na ƙarshen nan ba. Sai kuma nayi sa'a kaga saƙona kazo.”

Gaba ɗaya Dagger ji yake kamar kansa zai tarwatse dan tashin hankali. Ya dunƙule hannu da masifar ƙarfi ya daki bangon ɗakin Malam Buba yana wani irin ƙaraji daya saka Malam Buba zaro idanu yana kallon ƙofa. Duk da saida ya rufe windows da ƙofar tunda Dagger ya shigo yana tsoron wani yaji ihunsa a gida... “Oga kayi a hankali mana kada wani yaji. A ganina ba rikita kai bane mafita. Tunanin abinda ya dace. Kasan dai tunda Uwa tace taga hoton nan mutumin nan bazai ƙyale mu ba. Dole zai fara bincike akanmu......”

“Shiyyasa nace kai wawa ne Mole. Idan kai jaki ne shi ba irinka bane ai. A zatonka zai mance da fuskata ne har ya zauna wani bincike a kaina? Kaima badan wannan gemu da sajen ɓadda kamar daka sanya ba da wannan fentin da kake ma kanka an gaya maka bazai gane ka ba ne tun a ranar farko? Ko a yanzu na fara tantamar guy ɗin nan bai gane ka ba, ya barka ne kawai a cikin takunsa.”

Tsuttt fitsarin tashin hankali ya zubo jikin Mole. Jikinsa na karkarwa ya ce, “Amma Oga miyyasa baka taɓa faɗa min haka ba?”.

Wata muguwar Harara Dagger ya zuba masa kawai, batare da yace komai ba ya hankaɗesa ya buɗe ƙofar ɗakin ya fice abinsa. Ai gaba ɗaya sai Mole ya sake jin gudawa ma na neman zubo masa ba fitsari ba. Tuni ya zabura ya ɗauki jakarsa da dama ya haɗa komai nashi yabi bayan Dagger. Yana fitowa ya samu har ya shiga mota. Ai shima sai kawai ya buɗe ya shige wufff kusa da shi. Ko kallonsa Dagger baiyi ba ya tada motar yabar ƙofar gidan a guje.....

<<<<<<%>>>>>>

“Tabbas Oga magana ta tabbata. Nimrah matarsa ce. Dan yanzun nan Mammah ta faɗa da bakinta a gabanmu. Sakamakon cikin baƙin yaran nan sun naɗi video sun turama babansu cewar Dada na nema Nimrah. Shi ne shi kuma ya ɗakko ƙafa ya taho, yanzu dai haka shi ya ɗauketa yayi ɗakinsa da ita. Nan kuma falon ya birkice ga matarsa nan uwargidansa ta yanke jiki ta faɗi tana abu kamar mai farfaɗiya ƙannenta sun ɗauketa zuwa sashen ta”.

“Hummm kice anzo dai-dai inda nake so?”.

“Anzo kuwa ƙwarai da gaske Sir!”.

“ALLAH yay miki albarka, sai ki kasance cikin shiri dan aiki ki gab yake da fa ƙarewa. Lokacin bayyanata yayi.”

“In sha ALLAHU Sir”.

Ta faɗa cikin ƙamewa da salute ɗinsa tamkar tana a gabansa ne. Shima daga can sai ya saki murmurshi da jinjina mata kansa tamkar yana a gaban nata ya ce, “Proud of you dear”.

“Thank you Sir! Proud of you too.”

Murmurshi kawai yay mata da har taji fitar sautinsa a cikin kunneta, daga haka ya yanke wayar, itama sai ta ajiye tana sauke ajiyar zuciya. Sai dai kuma cak numfashinta ya ɗauke sakamakon fitowar ƴar uwarta daga bayi da bata san da ita ba. Yanda take kallonta cikin ido ya sakata fahimtar duk taji wayar tata. A rikice ta zabura kanta, sai dai da sauri ta ɗaga mata hannu alamar karma tazo gareta. Dole ta tsaya cak suna kallon juna tamkar tsaiwar zakaru..........✍

Tooooo barkanmu da juma'a. □Dada ya shige da ƴar mutane marainiyar ALLAH ɗaki.

Ga shugaban ƙasa yayi bombing zukatan munafukai□☺□.

Ga Dagger da Mole a kwale-kwale😂□.

Ga Nabeeha uwargida mai capacity na farfaɗiya□□.

Ga Uncle Tasi'u da ƴayƴansa a lukutar masifa😱.

Ga ƴar leƙen asirin mai aiki a ƙaulani□□.

Kai wannan sati yazo da alheri□.
Received at 12:31 PM
2 people reacted with □
[4/2, 10:27 PM] null: 21

........Fitar sanarwar shugaban ƙasa baifi da minti goma ba ƙasar ta shiga hayaniya. Kamar wutar lantarki da aka saki a ruwan sama. Wayoyi suna ringing a tsakani musamman manya masu faɗa aji. Screenshots na yawo a tsakanin talakawa. Hashtags na tashi tare da hotunan mazaje biyu da mukaminsu yafi na kowa ɗaukar hankali. Ire-iren sakwanin dake yawo a media sune......

“Chief of Staff? Zak-Shadow???”.

“Wannan ba shine mutumin da aka cire a prison ba kwanakin baya, aka kuma tabbatar ya ajiye aikin soja ɗin ma saboda rashin isashen lafiya?”.

“Imran Abbas NSA? Soja ne fa, ba ɗan siyasa ba!”.

A Twitter (X) ire-iren saƙonnin manya sune,.....

“Janar Tafida ya raina jam’iyya.”

“Wannan naɗin barazana ne ga tsarin dimokuraɗiyya.”

“Ko ya manta da gwamnatin ba tashi bace shi da sojoji, shima alfarma akai masa ne?”.

“ALLAH ya ƙara, bamu an hana mu shi an bashi ba. Saboda ya fimu iya munafunci”.

“Kaɗan ma kenan daga aikin tsohon soja, wataran ma ƴan jam'iyyar duk sai ya koro su ya canja da sojoji”.

“Amma mutumin nan fa makiri ne”.

“Makiri ko ɗan bariki”.

“Miye abin makirci anan, abinda ya dace shi yayi. Kuma ni yamun dai-dai. Wannan shine irin shugaban da muke so dama”.

“Hummm ai dama kune kuka ɗora shi”.

A Facebook groups talawa suma na nasu koda ba za'aji ko a gansu ba....

“Wannan shi ne ƙarshen siyasar tsofaffi.”

“Sun kawo sojoji cikin gwamnati.”

“Ina ganin akwai wani abu a ƙasa.”

“Kaima kasan dole akwai magana mutumin nan da ƙarfinsa yazo. Ai kaga duk ya rikita munafukai masu fuska biyu. Jeka manhajar X kaga yanda manyan ƙasar ke ɓarin zance alamar ƙirjinsu naci da wuta”.

“Ai tun ɗazu ina can dariya kamar zata kashe ni. Wai kaga shegen can mai tafiya kamar zai saki kashi mi yace? Amma naga ya samu amsa dai-dai shi wajen Na bature kasan shi baya barin sai ta kwana gwamnan mu abin alfarinmu”.

“Hahaaaaa anayi muna jin daɗi”.

“Ai Janar yana basu wuta.”

Ai ɗan ƙunar ɓakin wake ne, kan mai uwa da wabi yake yi. Ga kuma ZAKI ya shigo tawagar kowa sai yaci ƙwal ubansa. Yara da basu san waye ZAK-SHADOW ba duk sai su shirya saninsa yanzu”.

“ALLAH ya taimaki Janar.”

“A ƙarshe an samu mutum mai ƙashin mu na baya masu tasowa.”

“Idan wannan mutumin bai gyara ƙasar nan ba, babu wanda zai iya.”

“Mudai nema ALLAH ya gyara ba mutum ba”.

“To ina ruwanka ɗan hau”.

“Ai gaskiya na faɗa. Ya kamata Ku dinga sanin mi kuke rubutawa a media”.

“Anƙi a kiyaye ɗin. Kai wlhy sai na saka a nemomin kai naci uwarka”.

“Wanda ya fasa”.

Haka dai media ɗin ke a rikice taki ina. Talakawa sun kasu gida biyu. Masu kuɗi sun shiga shakku. Masu iko sun shiga firgici. Amma Jam’iyya ba hayaniya suke yi ba. Cikin shiru suke a zahiri, irin shiru na haɗa kai da neman juna a ɗakin meeting na gaggawa.....

Lallai Ƙura ta tashi a ƙasa gaba ɗaya fiye da yanda Janar yay tsammani. Dan wannan kujeru sun sake fito da ƙarfin alaƙar dake tsakaninsa da Imran da Zak-Shadow. Cikin abinda bai wuce minti talatin ba sanarwar tayi bala'in tafiya sama mai ban mamaki. Masu murna nayi, masu mamaki nayi a cikin talakawa. Ɓangaren jam'iyyun adawa sunyi caaa suma fiye da yanda kuka ga sakwanin wasu a sama...

A zahirance ka-ce-na-ce ɗin jam'iyyun adawa normal ne, dan abu ne da kowa yasan yana faruwa a siyasar ƙasar kuma dole ne ma ayi. Babbar ƙurar data tashi a cikin gida ga ƴan jam'iyya itace ainahin rikita-rikita, dan cikin abinda bai wuce awa biyu ba suka haɗa meeting da tun kafin su zauna shugaban ƙasa ya samu labari. Dariya abin ya bashi, bai kuma ji abin ya damesa ba. Shi ya gama nashi, ya barsu da nasu a yanzu kam. Tsabar ma yanda yake jin ransa fes kashe duk wayoyinsa yay ya miƙe ƙafa tsakkiyar yaransa cike da nishaɗin da ya ba First Lady Hajiya Zainab Tafida mamaki. Ya haɗa tarzoma da yaƙin baki yazo yana nishaɗi, rikita-rikitar mijinta na ɗaga mata hankali. Fatan ta dai a gama mulkin nan lafiya..

“Sam bazai yiwu ba, domin mutumin nan yama maidamu ƴan iska a zahirance.”

“Ai mun wuce ƴan iska a wajensa Honorable. Sai dai watsatstsu, wai taya zamu tura mota ta tashi sannan ta koma buɗemu da hayaƙin ta. Halan sojoji ne zasu koma mulkin ƙasar bamu sani ba”.

“Ga zahiri ka gani kuwa Professor. Shugaban ƙasa tsohon soja, Chief of staff soja, National security advisor soja, to a ministoci ma da suka rage sai mu jira wasu sojojin zasu shigo.”

Yanda suke ta surutai har wani baya tsayawa yaji na wani ya sake harzuƙa manyan jam'iyyar tasu. A fusace shugaban jam'iyya ya furta, “Wai cece kuce ɗin naku zamu ji ko abinda ya tara mu?!!”.

Tsitt meeting room ɗin yayi a karo na farko, sai dai kowa fuska a kumbure. Ji suke kamar da suna da iko yanzun nan su zartar da takardar sauke shugaban ƙasa a kujerar nan tashi, sai dai shugaban jam'iyya ya bari kowa ya sarara sannan ya cigaba da magana.

“Tabbas munyi kuskuren zaɓar mutumin nan sama da kowa. Sannan munyi kuskuren yarda da shi kai tsaye batare da mun zurfafa binciken gano ainahin abinda ke ransa ba. Kuskure na ƙarshe a jiya muka tafka shi, ya kamata kafin mu sallama masa musan wanene zai bama waɗan nan appointment ɗin ko kuwa Barrister?”.

Yay maganar ƙarshe yana kallon wani kamilallen mutum dake gefensa. Tunda ake cecekun baiyi ko tari ba, bama shi kaɗai ba akwai waɗanda da yawa basu ce ba dan su basuga abin tada jijiyar wuya ba anan. Hakan ta faru ne kuma sakamakon su zukatansu a tsarkake suke akan siyasar dama can.

Barrister yaja numfashi da sauke ajiyar zuciya sannan ya gyara zamansa da ƙyau. Idanunsa na bin kowa da kallo kafin ya furta, “Chairman ba lallai tunani na ya zama irin na kowa ba, amma a nawa ra'ayin ni banga abinda ba daidai ba anan. Na farko dai mune muka gindaya sharaɗin shugabanci 60-40. Duk da yaja kamar yanda aka saba yazo ya sakar mana. Ba kuma hakan na nufin bashi da ra'ayin kansa bane ba ko bashi da wasu buruka a cikin mulkinsa. Tunda har ya amshi namu buƙatun, ya kuma fara bada kujerun ga dukkan wanda muka zaɓa way note shima mu bashi tashi damar. Sannan mutanen nan biyu fa da ake magana a kansu mutanen kirki ne, mu cire batun ɓata su da akayi a baya, mu kalli gudunmawar da rawar da suka takama

ƙasar musamman akan rikicin shekarun baya da yaso kassara mana ƙasar. Shin bayan wannan akan aikinsu akwai wani kuskuren da zai sa mu ƙyamace su ne?”.

Shiru hall ɗin yayi kamar ruwa ya cinye su. Masu zuciyar gaskiya irin tasa nata jinjina kawunan gamsuwa. Ruɓaɓɓu masu manufa zukatansu na harzuƙa. Dan wasu a cikinsu sun so kujerar a bayan fage basu samu ba. Wasu kuma a bayyane, wasu ko yaran manyan shegun ne ƴan ƙunyar duhu. Wani matashin dattijo da bai wuce arba'in ba ya katse shirun da faɗin,

“Tabbas gaskiya Barrister ya faɗa, sannan ya farkar damu abinda idanunmu ke neman rufewa a kai. Haysam Abdul-rasheed Shehu da Imran Abbas basu da wani mummunan record na rayuwa idan ka cire abinda ya faru shekaru takwas da suka gabata da har yanzu babu mai bugar ƙirji yace gaskiya ne. Sannan suba ƴan siyasa ba balle muce. Ina ga maimakon ɓatama kammu suna da biye jam'iyyun adawa kawai mu goyama Mr President baya akan abinda ya dace. Mu fuskanci waɗancan dake sukarmu a waje yafi rikita kammu a cikin gida har azo a samu rarrabuwar kawuna. Ya mana abinda muke so, shima yayi wanda yake so zance ya ƙare ai?”.

A zahiri kowa ya amsa daga waɗan nan jawaban, sai dai a zukata wannan tamkar shine mabuɗin buɗe rarrabuwar kawunan ƴan jam'iyya. Dan meeting ɗin na watsewa wasu suka kafa nasu a bayan fage......

ººººººººººººººº
ºººººººººººººººº

Tunda ya shimfiɗe ta a gadon idanu kawai ya zuba mata tsawon lokaci. Kafin ya ɗan sauke numfashi da salon ɗan burzoshi ta hanci yana janye idanun nasa slowly. Ruwan dake a drawer ɗin gefen gadon ya ɗauka yasa kaɗan cikin tafin hannunsa sannan ya kai fuskarta ya shafa mata. Nannauyan numfashi ta kawo har jikinta na motsawa na yanayin farfaɗowa. Sai kuma ta koma laƙwas tana ƙara sauke ajiyar zuciya a jere. Fin sakan goma kafin ta shiga motsa idannunta da eyelashes ɗin ke a jiƙe. A kansa ta sauke su, yana zaune kusa da ita gab ya zuba mata nasa firgitattun idanun da a yanzu ta jisu da kaifi fiye da baya. So take ta risinar da nata kota maida ta rufe, amma hakan ya gareta. Sai ma wasu hawaye ne da gudu suka gangaro ta gefen idanun har suna shigewa a kunnenta.

Dada da gaba ɗaya yanda take kallonsa da wani irin yanayi kamar na mai roƙon ka tausaya min ɗin nan sai ya ji tana kassara illahirin jarumtarsa da ƙarfin garkuwar jikinsa. Kalaman mahaifiyarta suka shiga dawo masa cikin zuciya da ƙwaƙwalwa tamkar a yanzu ne take jera masa su. Dole shine ya lumshe nasa idanun a yau, tare da motsawa a hankali ya kai hannunsa saman fuskarta ya fara share mata hawayen.

Karo na farko ta maida fuskarta gefe alamar bata son share hawayen da yake matan. Dan haka shima ya tsaya kawai yana kallonta. Sai dai bai janye hannun nasa daga fuskarta ta ba. Kukan ta cigaba da yi, ta kuma ƙi juyowa ta sake kallonsa. Motsi lips ɗinsa sukayi kaɗan alamar murmurshi yake son yi, amma dai ya basar bai bari ya bayyana ba. Sai ma hannunta dake saman cikinta daya kamo da ɗayan hannunsa ya rumtse. A salon yanda yay ɗin ya tilasta Nimrah ɗan matse idanunta. Cikin suɓucewar harshe ta ce, “Dadaaaah!”.

“Na'am MATAR Dadah!”.

A bazata ya amsa kiran da waɗan nan kalmomin da suka sakata tashi zaune a zabure. Jikinta har rawa yake tsabar yanda ta tabbatar daga fa bakin nasa suke. Dan kuwa ya wani zuba mata idanu da kallon da zata rantse bata taɓa ganin yama wani ba a gidan balle ma ita ƴar ficikar nan. Rawa lips ɗinta suke alamar son sake yin magana, ga idanunsu cikin juna amma ta kasa iya furta komai..........✍

Received at 12:23 PM
[4/2, 10:28 PM] null: 22

........Bai hanata tashin da tai ɗin ba, sai dai a yanda ta tashin sai ya zama sun ƙara samun kusanci. Ƙafafunta ta matse tare da rungumesu da hannayenta. Sai zaman nata ya koma ta cure jikinta waje guda. Shi dai bai motsa ba, ya dai janye hannunsa dake riƙe da nata a lokacin da taje yunƙurin tashin.

Cikin sake fashe masa da sabon kuka ta ce, “Dada kana nufin Mammah ba tsokanar Uncle take ba kawai? Kaifa Dadanmu ne, taya za'ace haka. Inama laifin ace Mu'azz aka aura min”.

Har cikin rai kalmarta ta ƙarshe ta soke shi. Amma sai jarumtarsa ta danne hakan, ko'a zuciya bai raya komai ba. Ya dai zubama fuskarta da hawaye keta zarya idanunsa da suka sake kaɗewa, itama kallonsa take, so take ya amsa mata gaskiya ne Mammah tsokana take. Amma yaƙi furta komai, bashi da alamar zai ce wani abu. Ta ƙara langaɓe kanta lips ɗinta na rawa alamar son sake magana. Sai dai me, idanunsa da ke neman zubar da duk ƙwarin gwiwar ta ya wani kalar ja luuu kamar zai lumshe sai ya sake buɗesu a kanta.

“Shiii!!!” ya faɗa yana ɗaura yatsarsa ɗaya akan lips ɗinsa alamar kar tai magana. Kamar kuwa wadda akaima tsawa ta kasa maganar, dan ita kam al'amarin Dadan kamar ya fara hargitsa mata tunani. Dan da wani irin slow motion ya matso da tasa fuskar gab da tata har numfashinsu na gwamuwa cikin na juna. Da gudu ta rufe idannunta, duk da bata da tabbacin abinda zaiyi. Jin hucin numfashinsa a cikin kunnenta ya sata jin kamar zata shiɗe, musamman daya fara magana a cikinsu da muryar da bata taɓa sanin yana da ita ba, saboda tsabar yanda sautin ya fita da sanyi, da taushi, da kuma ainahin ɗabi'arsa ta nutsuwa da yin komai cikin kamun kai da gadara-gadara.

“Shi wannan DADAN zai iya zama MIJI. Dan haka Haysam Abdul-rasheed Shehu Kobi shi ne ainahin MIJI Kiddo, idan kin kalli DADA a matsayin Dada zaɓinki ne. Amma kowane YADI ana ɗinkashi da kalar ZARENSA ne NAJA'ATU NIMRAHH MUHAMMAD BANKAURA!”.

Ba tsigar jikinta kawai ba, hatta jininta sai da yay wata irin yamutsawar da har tana jin gangarawarsa cikin lungu da saƙo na brain ɗinta. Cikin yanayin ƙiƙƙifta idanunta dake mar-mar take kallon Dada daya janye fuskarsa daga kunnenta ya maido ta gab da tata tamkar hancinsu zai haɗe kan na juna..

Baki ta turaasa tare da taɓeshi cikin tantsar shagwaɓa hawayen da ita kanta laimarsu kawai taji na gangarowa da gudu akan fuskarta. A zuciyarta faɗi take (Na shiga uku ta tabbata hakan ne kenan. Dada fa ake magana! Wannan zakin da ganinsa ma firgici ne, taya za'ace ni matarka ce. Kai wlhy bazan iya ba kafi ƙarfinta. Yo ko su Uncle Ma'aruff sunfi ƙarfina ai balle kai Dada, kankat ɗin fa ake magana, haba dai wannan zance nauyinsa yayi min yawa, ayyanashi a zuciya kawai firgitani yake. Badan kasancewarsa a gabana ba da tuni ta ƙwala riƙaƙƙen ihun da sai gidan nan ya girgiza....)

Dada dake kallonta da karantar abinda take tattaunawa da zuciyarta akan fuskarta ya ɗan taɓe baki. Cikin sake kassarata ya furta, “Bazan hanaki kuka ba, kiyi har ki tabbatar da kin gamsu. Sai dai ki sani, abinda kika ji yana nan a yanda kika jishi, bazai taɓa canjawaba koda a labari ne, sai dai ma nace ki fara shiri Dan zaki shiga lavel 2 ajin sabuwar makarantar ki little Shadow.....” yana kai ƙarshen maganar da sai ka rantse ba daga bakinsa ta fito ba. Dan cike da basarwa da kame kai ya janye jikinsa gaba ɗaya daga nata ya miƙe abinsa yana ɓalle maɓallan rigar jikinsa.

Tsabar wani ƙullutu da Nimrah keji a zuciyarta sai ta fashe da kuka tare da fara turza ƙafa da sautin ya sashi tsayawa cak. Sai dai bai juyo ba, bai kuma yi magana ba har sai da ta fashe da kuka da faɗin, “Ni wlhy bana SON...”

Wani kalar bugawa zuciyarsa tayi tun kan ta ƙarasa, ya lumshe idanu yana matse yatsun hannunsa cikin juna. Sai dai dai-dai nan ta ƙarasa faɗin, “........KISHIYA ƴar daba”. Ai wani kalar kufcewa numfashin Dada da yay sama ya dawo cikin ƙirjinsa kamar mai farfaɗowa daga mutuwa saboda furicin farko da baiyi tunanin abinda zata faɗa ba kenan.

Received at 12:24 PM

reacted with ❤Dariya ma ce taso kamashi yanzu, wato tabbas Imran yayi gaskiya, yanzu dai tana nufin matarsa Nabeeha ce ƴar daba? Sunan data kirata a shekarun baya, hakan na nufin bata manta ba, anya kuwa bai kamata ya fara tsoron al'amarin yarinyar nan ba?. Ƴar firit da ita har tasan wani kishiya, a lallai ya shiga ukun sa.....”

“Ni dai Dada kayi maganaaaa!”.

Ta ƙara faɗa cike da neman fitina tana ƙara ƙarfin tirje-tirjen ta. Wani kalar juyowa yay a bazatar da ita kanta ganinsa kawai tai a gabanta. Kafin kuma ta tantance a yanda yazo kawai taji ƙananun lips ɗinta cikin nashi. Kaɗan ya rage ta saki fitsari dan firgita. Ta waro idanunta da ƙwayar tai kamar zata faɗo ƙasa. Shima kallon nata yake, sai kuma ya kai hannu a hankali ya rufe idanun nata kawai ya cigaba da kissing ɗinta.

Lallai wannan rana takai Nimrah ta kirata a mafi firgici da ruɗani. Abu ne da a duniya koda wasa babu wanda ya taɓa kwatanta mata shi sai Dada. Dada fa ba wani ba. Ya ilahi inama ta sake suma kawai ta huta...

(Nima ji nake kamar na suman Nimrah. Shike nan Dada girma Yayi tangal-tangal. Ba kunya ya matse lips ɗin Kiddo a nashi.)

Sai da Dada ya tabbatar ya huce takaicin lips ɗin nan dake damunsa da surutu da taɓara da rikici. Ya kuma lausasa jikin mamallakinsa sannan ya sake su, tare da janye tafin hannunsa daya rufe mata ido batare daya kalleta ba ya miƙe abinsa daga bakin gadon. Bai ko juya ya kalli sashen da take ba, dan da tasan fitinar tarnaƙin da take tayarwa da wannan lamarin nata da taja har ya kai ga abinda yake ta ƙoƙarin hana kansa da a bargo ta shige tun farko ta rufe kanta kawai zaifi sauƙi. Ƙofar Bathroom daya shiga ya maida ya rufe, tare da jingina a jikinta ya rufe idanunsa. Tabbas idan baiyi da gaske ba Yarinyar nan zata sakashi fara bin titi ne yana surutai....

<<••>><••••><<••>>

“Mammah! Gwaggo!! kuna ina? Shugaban ƙasa ya bama Dada da Yaya Imran appointment”.

Muryar Bilal da yaje ɗaukar Uncle Jamilu airport ta karaɗe falon a dai-dai lokacin da hankalinsu ke komawa kan Nabeeha dake layi zata faɗi ALLAH ya taimaka Ruky ta tareta. Sai dai ta mata nauyi, an kuma rasa wanda zai yunƙuro ya taimaka mata su riƙeta. Dan kowa kallon abin yake kamar iskanci ne kawai, ganin haka sai kawai itama Rukyn ta saketa ƙasa timmm😂 tana yarfe hannaye. A dai-dai lokacin Amima da Rayhana ke shigowa sashen. Yayinda a tare Daddy Imran da Uncle Tasi'u suka furta, “Appointment?!”.

“Wlhy kuwa, yanzun nan aka sanar. Yaya Imran NSA Dada COS”.

“Bilal bamu a buɗe, miye NSA da COS?”.

Cewar Gwaggo Khadijah tana yunƙurowa. Shi kam Daddy Imran kamar wanda yay sumar tsaye ma za'ace. Hakama Mammah abin ya daketa. Suko su Biebah tuni sun ɗauka wayoyi. Bilal ya bama Gwaggo Khadijah amsa da,

“National Security Advisor shine NSA. Chief Of Staff kuma shine COS Gwaggo. Kujeru ne masu girman gaske da daraja a gwamnatance fa. Hummm wannan gwamnatin tamu ce”.

“Tabbas tamu ce Bilalu”.

Cewar Yaya Ja'afar dake shigowa shi da Ma'aruff. Kai da ka gansu kasan cikin matsanancin farin ciki suke. Sai ga Ammar shima tare da Uncle Nasiru. Ai tuni an manta da wani batun video an koma farin ciki kamar falon zai fashe. Dan tsabar shaƙiyanci rawa harda su Ma'aruff. Wannan hanayinayar tasu ta saka Nimrah dake sume a ɗakin Dada ƙarfin jan ƙafafunta ta fito kamar mai jin juwa. Yayinda zuciyar Uncle Tasi'u ke faman bugawa a cikin ƙirjinsa. Rayawa yake a ransa (Shike nan A'isha ta sake mun nisa).

Oho shi kaɗai yasan yanayi, dan shi da ƴaƴansa ne kawai tsaye ƙiƙam suna kallon yanda falon ya harmutse. Dan suma su Lailah dake fama da jego musamman ita ga CS sai gasu kamar an jehosu dai-dai da sakkowar Nimrah daga upstairs. Tuni Ruky da ta fara ganin Nimrah taje ta tungumeta batare data lura da yanda take a hargitse ba. Dan murna biyu take yi, na samun appointment ɗin iyayensu da farin cikin Ninah ɗinta matar Dadansu.
Received at 12:24 Nimrah ta tura baki da faɗin, "Wai miya faru Buddy?".

"Dada da Daddy aka bama appointment Trouble Queen ɗina. Wayyo ALLAH daɗi kasheni my Ninah matar Dadana."

Idanu sosai Nimrah ta waro tana danne bakin Ruky da hannu, a haka taja hannunta suka shige ɗakinsu. Tana maida ƙofar ta rufe Ruky ta buge mata hannu da faɗin, "Ke ana celebration zaki jawoni nan lafiya?".

Maimakon amsa sai kawai Nimrah ta rungumeta tana fashewa da kuka. "Ruky na shiga uku Dada fa? Wlhy ji nake kamar zan haukace dan tashin hankali. Ruky guduwa zanyi, bazan iya kallon Dada a matsayin miji ba yamin girma, shi uba ne Ruky, duk da abinda ke raina a game da shi shi da Daddy martabarsu bata da misali a zuciyata. Ko su Uncle Ja'afar sun min girma ai balle Dada. Inama laifin su Mu'azz.."

Rawa jikin Ruky yake yi, ta kama Nimrah suka ƙarasa bakin gado. Zaunar da ita tai itama ta zauna. Sai ta sake rungumeta. Itama tata muryar na rawa ta ce,..........✍

ALLAH dai yasa kar Ninah ta tonama Dada asiri a wajen Ruky munga idi, Dan ALLAH ku taro ta ba'a bama aminai wannan labarin♀.
[4/2, 10:37 PM] null: 23

........."Wace irin magana ce wannan Nimrah? Ni banga abin tada hankali anan ba. Wlhy kunyi matuƙar dacewa da Dada. Wannan ai abin farin ciki ne. Mi zaki yi da wasu su Yaya Mu'azz ana zaune ƙalau. Kefa kike cewa baƙya son auren yaro zaki raina shi, ALLAH kuma ya baki wanda ya dace shine kike faɗar haka? Haba Ninah ki buɗe idon ki ki kalla Dada. Cikakken mutum ainahin nutsatstse, handsome. Ga kwarjini, ga ibada, ga iya wanka ko su Yaya Bilal dake samari bazasu nuna masa iya saka kaya da gayu ba. Ga ilimin addini dana zamani. Idan yana magana ma kawai abin ka tsaya kana kallo ne, to wlhy kallo da idanu ma kawai na Dada na musamman ne. Ke banda ma rashin wayo ai wannan dama ce da zamu dama akan waccan shegiyar matar tasa. Dan wlhy jiya sanda kina ɗakin Dada ke da ita Yaya Mu'azz ya bani labari sosai a kanta da iskancinta. Ashe ta jima tana abubuwa a gidan nan Mammah na hana a ɗauki mataki kanta saboda Uncle Nasiru. Sannan ashe tabar gidan nan ne saboda yankan nan na cinyarki, to sai ma yanzu da akace matarsa ce ke na gano wani abu da shima Yaya Mu'azz bai sani ba. Saboda auren ku ta yanka ki ɗin kenan..."

"Kam bu! Ki ce ALLAH?".

"Wlhy da gaske nake. Dan haka in ma zaki ajiye wannan shirmen ki ajiye, fili ne da muka samu aci uwar sabada."

"Uhmmm! Ruky na fahimceki, amma kema kin san abin nan da girma yake. Sannan kinfa san bana son kishiya daga ni har ke. A tsarin mu na auren masu shekaru babu mai mata. Tuzuru dai haka ko mijin matacciya kin manta ne".

"Ke dalla wannan ai tsarin mu ne. Yanzu kuma tsarin UBANGIJI ake magana. To banda ma abinki kin san dai Dada bazai sake ki ba. My love manta da wani burin mu aci uwar sabada a gidan nan. Duk abinda shegiyar can tama iyayenmu mu rama musu wlhy. Sannan mu ƙwace Dadan a hannunta sai ta bar gidan nan koda rarrafe, dan ƙafafun ma sai mun nakasa su tunda kema a ƙafa ta yanke ki. Banda ALLAH ya kiyaye da yanzu Bestyna gurguwa ce".

Ruky ta ƙare maganar da tsokana tana jan hancin Nimrah. Hannun ta buge mata tana dariya itama. Hakan zai tabbatar maka da zallar ƙuruciyarsu. Dan cikin ƙanƙanin

lokaci har Ruky ta canja tunanin Nimrah akan tashin hankalin wannan aure. Kawai ma sun koma tsare-tsaren su akan yanda zasu gogema Nabeeha hadda ne.....

Kai ALLAH ya shirya waɗan nan yara, kwana biyu aljanu sun lafa ashe watan dawowarsu ya kama♀.

••••••••••••••

Da mamaki Dada dake fitowa a bathroom yake kallon Imran dake zaune a ɗakin nasa. Gado ya kalla, dan ya tabbatar anan yabar Nimrah ai, sai kuma ya sake juyowa ya kalla Imran da shima ke kallonsa cike da alamar tambaya.

"Wai lafiya?".

"Tana ina?".

"Wace?".

"Ƴarka mana".

"Ai ban sameta a ɗakin nan ba ni kam".

Ɗan jimmm Dada yay na mamaki, sai kuma ya nufi wadrobe ya kama buɗe-buɗe. Imran dake danne dariya ya ce, "Mi kake nema kuma?".

"Ita mana, nasan kaɗan daga aikinta yin hakan ai."

Yanzu kam dole Imran ya dara. "Na gode ALLAH daka fara fahimtar hakan. To kwantar da hankalinka ta fita, dan sai da naga saukarta ƙasa na hauro. Wai kasan mike faruwa ne?".

Ɓoyayyar ajiyar zuciya Dada ya sauke. Sai kuma ya girgizama Imran kai batare da yace komai ba. Waya Imran ya miƙa masa kawai shima. Kamar Dada zai yi magana sai kuma ya fasa, ya amsa kawai yana kallon screen ɗin.

"What! Imran mike damun Janar ne?".

"Bala'i mana, da neman takife irin na tsohon soja. Ina ga so yake sai anyi bandar mu a titi hankalinsa zai kwanta. Ya mance siyasa ba gumurzun soja bane a jeji na ayi rai ko a mutu. Cikin awannin da basu gaza biyu ba ya hargitse ƙasar gaba ɗaya".

Karo na farko Dada daya rasa abin faɗa yay murmushin da har haƙoransa na bayyana.

"Oh dariya ma abin ya baka?".

"To idan banyi dariya ba kuka kake so nayi Imran. A zahirance Janar ya fimu zama ɗan ta'addan ƙunar baƙin wake. Gaba ɗaya mantawa yake da suwaye mutanen nan a ƙasar nan".

Received at 12:24 PM "Wlhy yana sane Haysam. Kawai dai ɗan ƙunar baƙin waken ne kamar yanda ka faɗa."

"Ai ko dole yau mu samesa, dan bazamu iya haɗa wannan aikin dana bayan fage ba".

"Ina bayanka nima kam. Ya za'ayi da yaron nan daya ɗauka videon nan?".

Maimakon amsawa miƙewa Dada yay yana nufar gaban mirror. Hakan yasa Daddy Imran binsa da kallo.

"Wannan su Ruƙayya ma ai sun ishe shi. Ka barsu da shi kawai. Uban dama akwai shirin da nake a kansa."

"Bincike kayi a kansa?".

"Dama zan barsa a jikin Mammah ne sakaka ban san waye shi ba a yanzu. Karka manta da abinda ya aikata a baya. Idan ita ta karɓesa mu sai mu karɓesa?".

"Ni a ganina karɓarsa ba wani abu bane. Koba komai ɗan uwanta ne. Tana cike da wannan ƙishin a cikin zuciyarta. Kasan shi ruwan kashe gobara kona gutter aka gani ɗiba ake a kashe".

"Ai ko zan shayar da wannan gobar mamaki, dan ni da fetur zan kashe ta ko gas.."

"Hhhh ai kai baka tsoron a mutu ko ai rai. Shiyyasa kai da Janar ɗin ban san wa yafi nemo mana aradu da ka ba".

"A ya fini. Janar fa ainahin fitinannen mutum ne".

Sosai Imran ke dariya yanzun kam. Dada ma murmurshi yake yi. Sai da suka tsagaita Imran yace, “Uncle Jamilu fa ya iso. Uncle Nasiru ma yazo, ya kamata muje ƙasan. Amma yaya kuka ƙare da Daughter?”.

Murmushi Dada yayi yana kaiwa zaune. Ya ce, “Hummm”.

“Kai malam bani nasha miye wani Hummm.”

Dada ya sake sakin murmurshi yana ɗan cizar lips ɗinsa kawai. “Yau kana sani surutu da yawa ALLAH. Bazaka gane bane, yarinyar nan daruntа yafi na Janar ɗin ma ai. Wai kasan kuka ta dasa min ita bazata son kishiya”.

Ba ƙarmin gwalalo idanu waje Daddy Imran yayi ba. Cikin matuƙar mamaki ya ce, “Nimrah ɗin?”..

“Wlhy karka ji wasa. Shiyyasa ma nai shigewata bayi na barta.”

“Tofa babbar magana, kenan dai ta amshi auren?”.

“Oho mata, dan tace wai ita dama Mu'azz ne dai ko miye na manta shirmen nata ma ni.”

Daddy Imran yay dariya. “Uhmm ai aiki ya sameka. Dan ba'a fara komai ba ma. Ai tunda a haka abin ya tsaya Alhamdullah. Su dai mata duk ƙanƙantarsu sun san kishi...”

“Humm ni kaina abin ya girmi kaina ai.”

“Dolene ai. Kasan kuwa kana haurowa itama Nabeeha ta yanke jiki ta faɗi, sai lokacin ma duk muka farga da ita. Zakina inaga kayi haƙuri haka nan ka janye fushinka ka fuskanceta itama. Gara ku dai-daita kafin Nimrah ta tare.”

“Amma wasa kake yi? Dan a cikin horon dana shirya mata bamma fara komai ba. Bani take ɗauka shashasha ba, saboda mamanta ta ɗaure mata ƙugu. Mu zuba nida ita...”

“Ban hanaka horata ba, amma kayi mata kai da ita kawai. Bana son mutanen da basu san mita aikata ba a gefe ko suka manta su kalleka matsayin wanda ke watsar da uwargidansa saboda amarya”.

“Matsalar su ce su masu wannan tunanin ɗin. Duk kuma namijin daka ganshi a wannan layin bai yarda da kansa bane ba. Ni ban taso gidanmu naga wani uwargida da amarya ba. Dan haka a gidana ma matana matana ne. Kowacce nada girma da darajar ta, ya rage naki ki riƙe na tayaki riƙewar. Ko ki zubar na tayaki takawa a ƙasa. Ƙyale ni na huta joooouh. Ka cikani da surutu barci ma ni nake ji?”.

“Aiko bazakayi shi ba wlhy, tashi ma zakai mu sauka ƙasa.”

Hararar da Dada yayi, Imran ya taɓe baki irin kai ka sani ɗin nan.....

===========

“Aunty kuka fa ba shi bane mafita. Tashi zaki ki ƙwaci ƴancinki a gidan nan. Sannan ki cirema zuciyarki tsoron Dada. Idan ba haka ba zai cigaba da takaki yanda ransa ke so.”

“Hummm amma Amima ki cire son zuciya. Itama fa da laifinta. Ai ya cancanci yabo ma da salon hukuncin nashi. Idan wani ne ko ƙofar gate ɗin nan bazai bari ta sake takowa ba balle ƴan uwansa. Bai kamata kullum kuna ɗora masa laifi ba ita ku gagara gaya mata gaskiyar nata kuskuren”. Rayhana ta ƙarasa faɗa tana taɓe baki.
Received at 12:24 PM “Wace irin magana ce wannan Rayhana?”.

“Gaskiya mana. Koda yake ku mutanen duniya itace bakwa son ji”.

“To ke ki fara gayawa kanki gaskiyar mana mtsoww”.

“Iyeee lallai Amimah wai ni kike ma tsaki?”.

“An miki ɗin. Kuma in baki da abin faɗa ga hanya nan ki kama gabanki”.

Duka Rayhana ta kai mata. Tasa hannu ta tare tana faɗin, “Wlhy kika dakan sai na rama.”

Ƙwafa kawai Rayhana tayi, fuuu ta fice a ɗakin tana jefama Nabeeha kallon banza. Itama Amimah rakata tai da harara. Kafin ta maida hankalinta kan Nabeeha dake kukanta har yanzu...

“Aunty kar shirmen Rayhana ya dame ki. Kamar yanda na faɗa miki yanzu lokacin yaƙin kwatar mijinki ne. Kuma in dai kina son cigaba da zama da shi dole kiyi hakan. Yanzu dai kinji da kunnenki, yarinyar nan bata san mijinta bane. Yanzu kuma ta sani, komai zaki iya gani a gareta. Zuwa yanzu dai kinga yanda take da rawar kai. Dan haka baki da wani isasshen lokaci ki nemi Aunty Jiddah na tabbatar zata ɗoraki akan duk shawarar data dace, in har kuma kikayi amfani da ita zaki ci riba”.

Tashi zaune Nabeeha tai tana share hawayenta. Murya a dakushe tace, “Amima Jiddah zata iya min dariya idan naje mata da damuwata a yanzu. Tunda a baya tayi iya yinta amma naƙi saurarenta”..........✍

Barkan mu da dawawa. Fatan kuna cikin ƙoshin lafiya.

Received at 12:24 PM

[4/2, 10:37 PM] null: 24

..........“Wlhy Aunty nasan Aunty Jiddah bazatai miki dariya ba. Sai dai ma taji daɗin kin fahimci abinda take son ki fahimta. Su Momy dai basu zauna damu ba balle gidajen nasu auren har da zasu fahimtar damu abinda zai fishshe mu. Damuwarsu kawai tara dukiya. Waɗan nan ƙawayen naki kuwa wlhy ba ƙaunarki suke ba. Hasalima wasu kamar suna hassada dake. Ki duba fa randa aka dawo dake yanda suketa ƙananun maganar wai ƴan uwan Dada sunyi kuɗi ba shi ba. Tunda ko gida yana prison suka gyara. Kuma in gaskiya za'a bi su gidan nan suna banbance dukiyarsu akan ta wane-da-wane ce? Komai nasu a haɗe yake, duk wata dai kowa za'a saka masa abinda ya sawwaƙa a account ɗinsa hidimar yau da kullum. Ko su Ammar dake ɗaukar albashi bana jin suna cinye kuɗin su kaɗai. To barshi ma gaskiya suka faɗa, yanzu ba gashi yau shugaban ƙasa ya bama Dadan appointment ba mai girman gaske. Chief Of Staff wasa ne. Duk fa wanda zaiga shugaban ƙasa a fadarsa sai yabi ta office ɗin Dada. Sannan shike da damar ganin shugaban ƙasa a koda yaushe fiye da kowa babu shamaki. Idan kika biye musu zako aci daular nan babu ke.”

“Na gode Amimah ƙarama da halin manya. Bari na kira Jiddah nace tazo. Ko kuma mu muje”.

“Muje ɗin dai Aunty. Dan bana jin tunda suka koma sabon gidansu kin taɓa ma zuwa. Amma dai ki fara gayama Dada idan ya yarda. Idan bai yarda ba sai mu nemo wata hanyar”.

Cikin gamsuwa ta jinjina mata kai tana miƙewa domin zuwa bayi wanke fuskarta...

Rayhana dake laɓe tana saurarensu tai ƙwafa da cije lips. Fuuu tabar jikin ƙofar yana ayyana mugayen ƙudirinta a zuciya game da Nabeeha. Dan ita fa ba gudu babu ja da baya. Aunty Jiddah ma kafin suje ita zata je......

(Wato a wannan rayuwar babu abun mamaki irin halayyar al'ummar wannan ƙarnin, dole ne ma muyita ganin masifu. Kowa dai yafi son ace shine sama da kowa. Wlhy mu dinga bincikar kammu da zukatanmu, da munga abu mara ƙyau na neman mana tasiri mu dage da addu'a sai ALLAH ya wanke mana zukatanmu. Wani abin fa da kaɗan ɗin nan yake farawa sai kaga ya zame maka ƙawa har baka ganin munin abinda kake yin).

★★★

“Kulu kefa nake jira. Dan na fahimci kina son laƙewa da wannan hayaniyar data sakamu fitowa a ɗaki babu shiri dan na manta”.

Murmushi Kulu tayi da dafa kafaɗar Hinde. "Hinde ki kwantar da hankalinki, ai ni na faɗa miki zan sanar miki ko. Yanzu kinga koba komai gidan da baƙi. Mammah bazata so mu kammala abinci a late ba."

"Hummm".

Kawai Hinde ta faɗa tana cigaba da aikinta. Itama sai Kulu tai dariya kawai ta cigaba da nata aikin. A ranta tana ayyana (Hinde kenan, lokaci da zai yi kisan wacece ni, kada ki damu)..

★___★

Mu'azz ne ya katse hirar Ruƙayya da Nimrah. Dan knocking ɗin da yay musu ya saka su yin shiru. A zatonsu Small Mom ce, dan basa son asan shirinsu balle ma Mammah ta hana su. Ganin Mu'azz daya ɗan turo ƙofar ya leƙo kansa ne suka sauke ajiyar zuciya. Doka ne baya shigo musu ɗaki sam sai da ƙwaƙwƙwaran dalili, shima ba shi kaɗai ba. Sai in da Mammah ko Small Mom haka.

"Dalla kuna nan ina can ina neman ku, ku fito akwai meeting".

In dai Yaya Mu'azz yace akwai meeting ai wata tsiyar za'a ƙulla. Dan haka duk suka miƙe kowa na neman dan ƙwali. Suna fitowa suka sameshi a ƙofa yana jiransu. Hannunsa ɗauke da plate dake rufe. Ruky takai hannu zata taɓa ya doketa.

"Kai Yaya Mu'azz dan ALLAH miye a ciki?".

"Koma miye ai zaki gani. Dalla kumuje abin taɓawa ne na samo mana, dan meeting ɗin yafi daɗi. Ku muje side ɗin su Uncle".

Tunda shugaban ƴan haɗa gwarama yayi kira ai dole mamu subi. Haka suka wuce su Mammah a falo kamar wani abin arziƙin zasuje ƙullowa. Babu wanda ya kulasu, dan iya manyan ne kawai ke magana. Dada da Daddy Imran ma basu kai ga sakkowa ba.

Can inda kujeru suke ƙasan bishiyar dake tsakiyar compound ɗin nasu Yaya Ma'aruff suka nufa. Bayan sun zauna Mu'azz ya gama waige-waigen tabbatar da babu kowa a kusa da su, har maigadi na can jikin gate yana gyangyaɗi, sai ya gyara zama. "Kun san wai minene?".

Received at 1:02 PM

reacted with ❤ "A'a sai ka faɗa."

Cewar Nimrah.

Mu'azz ya cigaba da faɗin. "Akan yaron nan ne Afeef. Bai kamata mu barshi ba. Dole yaji a jikinsa abinda yayi".

Nimrah ta kalli Ruky tai dariya. Kafin ta ce, "Haba Yaya Mu'azz dama kana tunanin zan barshi ne. Ashe ma shegiya aka haifeni ba uba. Yanzu ba dan akwai aure tsakani na da Dada ba shike nan sai ya min sharri ace mu ƴan iska ne".

A yanda tai maganar zaka tabbatar da zallar ƙuruciya a ciki. Dan shi kansa Mu'azz ɗin kasancewar ya girmesu sai da yay dariya da faɗin, "Eh lallai Ninah, abin ko kunya ma?".

"Yo kunyar mi zata ji, Yaya Mu'azz, kamar ma kana mana baƙin ciki banji ka tayamu murna ba". Cewar Ruƙayya tana tsare shi da idanu. Yay dariya yana girgiza kai.

"Nama fiki farin ciki ai. Kawai yanda abun yazo ne dai. Kinga bama gidan akayi labari Small Mom ta bamu. Amma idan banyi murnar auren Ninah da Dada ba nawa zan yi. Kema ALLAH ya kaimu naki".

"Sai da kai Yaya Mu'azz ɗin mu".

Suka faɗa a tare suna tafawa.

"Kai jama'a wlhy yaran nan kun lalace. Yanzu dai muje batun Afeef, miza'ai masa. Dan ina son aci ubansa ta yanda zai san mu gidanmu akwai girmama na gaba."

Ruky ta ce, "Tabbas zancenka dutsi. Amma fa naji kamar Mammah tace ya kwashe su subar gidan".

"Uncle Jamilu ya hana ai. Na kuma tabbatar idan yama Dada magana zai bari shima."

Nimrah ta ce, "Kai Alhmdllh ai mu haka muke so. Amma ina ga yanzu a barsa ya ɗan more weekend ɗin nan a gama suna sai a bajeta. Koya?".

Duk sun gamsu da zancen Nimrah dan haka sukace Yayi. Daga haka suka miƙe zuwa sashen Aunty Shariffa.....

§§§§§§§§§§§§§§

"Ni wlhy gaba ɗaya ka rikitani Oga. Dan ALLAH ka daina kai-kawon nan kazo mu nema mafita. Kazo ka ajiye mu a tsakiyar jeji ga dare na neman yi".

"Mole! Na rantse da ALLAH idan ka dameni zan alburushe kanka da bindigar nan. Kai wai kaine ƙarshen jakanta a ƙauyenku halan?. Dalla malam ka barni naji da damuwata".

Idanu Mole ya zuba masa. Har ya saka hannu a aljihu da nufin shi bari ya alburushe nasa kan kafin shi yayi hakan zuciyarsa ta gargaɗesa. (Karka aikata dan yana da amfani a rayuwarka. Karka damu akwai lokacin da zakai hakan. Bari ka gama sanin sirrinsa kaf musamman na dukiyarsa. Kaga idan ka kashe sa a wannan gaɓar riba biyu gareka. Maye gurbin kujerarsa, da mallake dukiyarsa). Kansa ya jinjina tamkar mai amsa zuciyarsa. Daga haka ya koma jikin motar Dagger ya jingina shiru kawai yana kallon sa.

Sun kwashe fin awa biyar a wajen, dan sai da duhun dare yayi sosai sannan Dagger ya nufi motar ya shiga. Da sauri shima Mole ya buɗe ya shiga gefen sa. Dagger ya kallesa a karo na farko. Cikin sassauta murya ya furta, "Lokaci yayi da zaka sanarma Nimrah kai ne mahaifinta. Kuma nan da wata biyu nake son ka ɗaura mana aure".

"Ta yaya Oga? Kuma saboda mi?".

"Saboda tabbas su Oga sunci amanarmu. Na gama karaɗe tunani na kaf na fahimci sune suka saka wasu sukai kidnapping Nimrah ranar. Dan a ranar da aka saketa an shigo da kayan aiki. Abin tambaya anan miyyasa suka saka wasu sukai musu aikin bamu ba? An fara munafuntata ne ta hanyar saka wasu aiki ko yaya?."

"Eh tabbas Oga kuma fa biri yayi kama da mutum. Kenan bayan mu akwai masu yi musu aiki a gidan. Kan uban can kai, wannan ai cin amana ce?".

"Aiko idan sukace zasuyi wasa da wuta zata ƙona su. Dan ni Dagger ba sha-sha-sha bane da zasuci moriyar ganga su yada kwaurenta. Komawarka gidan a yanzu akwai haɗari, dan haka zamu bi ta bayan fage tunda har yanzu bata gano mu su waye ba ka canja kamanni ka bayyana mata kai ne mahaifinta. Ni kuma ka barni da sauran aikin musamman akan su Oga. Zan gano mana koma mi suke shiryawa."

"Babu damuwa, sai dai gaskiya sai mun zauna mun tsara yanda zata kasance. Kasan Zak-Shadow ɗin nan shege ne wlhy. Kuskure ɗaya sai mu afka".

Received at 1:03 PM

2 people reacted with 😁 "Babu damuwa mu ƙarasa dai".

Ya faɗa yana tada motar suka ɗauki hanya. Ba ko ina bane kuma sai cikin jejin da suka sake danna kai dan Dagger nada haɗaɗɗen gida a wajen da komai na more rayuwa akwai a ciki. Ga mata ya zuba masu masa hidima sannan karuwansa. Banda wanda ake satowa a kawo masa yara ƙanana yana musu fyaɗe. Dan duk wadda ta shigo gidan ɗayan biyu ne. Kodai mutuwa ta fiddaki, ko ki zama baiwa mai hidima a garesa. Sai irin wanda suka zama yaransa da ake aika su yin ayyuka a cikin gari idan ta kama musamman akan manya.

Mole dai duk abin duniya ya damesa, musamman akan batun aure da Dagger yayi tsakaninsa da Nimrah. Eh tabbas ya yarda zai bayyana ma Nimrah kansa. Amma badan tazo hannun Dagger ba, sai dan ya nisantata da ƙasar nan gaba ɗaya. Daga yau kuma zai fara neman wanda zai taimaka masa samun muhalli a ƙasashen maƙwaftan nan nasu. Tunda a yanzu dai haka akwai kuɗaɗe masu nauyi a tare da shi da shi kansa bai san adadinsu ba. Ya kuma tabbatar zasu riƙe rayuwar Nimrah nan da

shekara fin goma ma, duk da yana da babban burin da target da yafi haka, babu tantama kuma sai ya cika, dukiyar Dagger sai ta zama mallakinsa shi da Nimransa. Hakama oganninsu lokacin da zai cigaba da tatsar kuɗi a jikinsu yayi, tunda har suka fara juyama Dagger baya hakan na nufin suma sun gaji Da shi..........✍

Hummmmmmm
[4/2, 10:38 PM] null: 25

.........Ran Uncle Nasiru yayi matuƙar ɓaci da jin abinda Uncle Tasi'u ya aikata. Hakama su Ja'afar da akai komai basa nan. Dan yanda Ja'afar ke huci sai ka rantse duka zai kai masa. Sai da Ma'aruff ya riƙesa ma. Shi kansa Uncle Jamilu duk da rashin yawan maganarsa sai da ya tanka. Sannan yay ma Uncle Tasi'un da kunya ya kama dalla-dalla akan auren. Sai dai baya fito ya sanar masa komai daya faru bane.

Uncle Nasiru ma faɗa sosai yayma Tasi'u irin wanda bai masa ko kwatankwacinsa ba a wancan karon. Sannan yaci uban Afeef dan saida yasha maruka biyu a wajensa. Hakan ya firgita Hanoon da Dayyan, suka kuma sake fahimtar Uncle Nasiru nada matsayi a wajen babbansu. Tunda ko tari bayyi ba sai ma haƙuri da yake ta bama Uncle Nasiru ɗin da Mammah.

Duk bidirin da ake sai ka rantse Dada baya wajen. Amma yana zaune abinsa ƙafa ɗaya kan ɗaya ya jingina da kujerar ya lumshe idanunsa. Gefensa Imran sai Bilal. Bayan Tasi'u yasha faɗa a gaban ƴaƴansa harda su Gwaggo Khadijah Uncle Nasiru ya koma nasiha da tabbatar musu muhimmancin zumunci. Ya kuma yabama ƙoƙarin Mammah da saka mata albarka akan yanda take kauda kanta. Koda ya kalla Dada ganin yanda yake zaune ma kamar mai barci sai ya kasa cemasa komai. Amma yasan dai duk yana jinsu. Sai dai shirun sa ba yana nufin babu komai a ransa ba. Bazai masa magana ba sai sun zauna su kaɗai. Dan haka maganar ta tsaya iya nan. Sai dai Mammah ta kafe kan washe gari Uncle Tasi'un zai ɗauki yaran su wuce gida. Dan ta tabbatar masa gaskiya sai ta huce koda zasu sake dawowa.

Hankalin Tasi'u ya tashi sosai, ya dinga roƙonta yana bada haƙuri. Haka ma hankalin Hanoon da Dayyan ya tashi, dan kuwa Hanoon a yanzu babu inda take son zama irin gidan nan, tunda aka fasa batun Nimrah matar Dada ce take jin ƙirjinta kamar zai buɗe dan tashin hankali. Ko kukan da take tun ɗazun akan Dada ne ba abinda akema uban su ba. Hakama Dayyan daya ƙwallafa ransa akan su Ruƙayya. A yau kuma jin Nimrah nada aure da kuma abinda ya faru sai ya tsarama kansa zai fara soyayya da Ruƙayya har akai ga aure. Sai kuma ga wannan batu ya ruguza musu dukkan shiri....

Hanoon na kuka ta rarrafa inda Mammah take. “Mammah dan ALLAH nidai zan zauna tare dake. Su Dayyan subi Dad ɗin, amma ni nafi jin daɗin zama anan. Kinga ni kaɗai ce mace a cikinsu, wlhy ina shiga kewar abokiyar hira, ga shi dangin Mom basa son muje inda suke ban san miyasa ba”.

Duk da Mammah taji tausayin yarinyar sai ta gagara cewa komai. A mamakin kowa kuma a bazata suka ji furucin Dada daya saka kowa kallonsa.

“Mammah ki barsu. Kar ki damu da makircin masu makirci, a ƙarshe kece da nasara. Dan kuwa sune ke ƙona kansu da kansu. Bibiyar wani da sharri ba shike nufin ka samu power ba, talala ce kake ma kanka, sannan alkairi kake kawoma wanda kake ganin bai kai ɗin ba. Wawancin wawaye kesa su kasa gane hakan. Idan kuma babu irinsu ai bama gane mun cigaba. Nasarace rayuwa da azzalumi. Kayita sama a gaban idonsa zuciyarsa na ƙara ƙonewa da zama a ƙunci da damuwar yaya zai yi da kai, shi baida tunanin yaya zai cigaba a tashi rayuwar. Kai kuma bama kasan da shi ba. A gama gwagwarmayar duniya aje lahira kaga mizaninka taf da ayyukan alkairi batare da kasan sanda ka tarasu ba. Ko kaga babu zunubanka ko ɗaya ka rasa yaya akayi. To ai ɗayan biyu ne. Kodai a ɗiba daga ladansu a ƙara maka, ko kuma a ɗiba daga

zunubinka a ƙara musu idan basu da ayyukan ladar. Dan ni dai Haysam Abdul-rasheed da ƴan uwana, babu yafiya tsakaninmu da masheranta".

Yana kaiwa ƙarshen nan yabar falon gaba ɗaya. Falon yay tsitt, zuciyar Tasi'u nata faman kai kawo, harga ALLAH kalaman Haysam ɗin sun shigesa, bama akan su kawai ba, haƙƙokin ɗunbin al'umma dake kansa da matarsa da a yau tana cikin ƙasa.......

□★□★□★□★□

A falo ana wannan cakwakiyar Biebah, Mu'azz, Nimrah na sashen su Lailah ne suna hirarsu. Hirar kuwa duk akan batun auren Nimrah da Dada ne. Abinda ya ke basu dariya yanda bakin Nimrah ya mutu rumus. Ko faɗan da Mu'azz ke takalar ta sai Ruky ke rama mata. Suko su Shariffa na dariya. Ana cikin hakan kira ya shigo wayar Biebah.

Received at 1:03 PM

Viewed 26 timesDan haka ta miƙe ta shige bedroom ɗin Lailah. Aiko Shariffa da Lailah suka fara tsokanarta suma. Dan soyayyar Faro da Biebah abin mamaki ce. Komai zakaga suna yinsa ne a ƙunshe. Ko su su Aunty Lailah ɗin sun jima kafin su san Yaya Haydar ke son Biebah. Hakama su Ja'afar. Balle su Nimrah da basu taɓa gane komai ba. Idan ma Faro zai zo hira wajenta mafi yawan lokaci Lahadi ne bayan Asr. Su kuma sun wuce islamiyya. Idan yay jinkirin tafiya suka dawo suka samesa a gidan sai ta nuna kamar yazo gaida Mammah ne. Sai da a dawowar nan ta Dada suka fahimta. (Haydar Galadima da ake kira da Faro dai kowa yasan amini ne a wajen Dada da Daddy Imran. Yanada mata har da yarinya ɗaya. Sai dai ALLAH yay ma matarsa rasuwa a wajen haihuwa a lokacin Dada na prison, shi kuma Daddy Imran ya fito babu jimawa. Ya jigatu da wannan jarabawa, dama yana tsaka da rashin aminai biyu kuma, duk da dai shi Imran ya fito lokacin. Daga baya dai ya haƙura ya barma ALLAH komai. Yanzu haka yarinyar na wajen mahaifiyar matar tasa. Shekaru uku kenan kuma da fara neman Biebah, duk da dai da farko ta nuna tsoron hakan saboda kasancewar sa abokin yayunta. Sai da Ammie ta saka baki da Imran cikin hikima sannan ta bada kai bori ya hau. Amma har yanzu ba gaba ɗaya ta iya sakin jikinta da shi ba dan tana masa kallon girmamawa kamar yanda take ma Imran da Dada)..

Anan sukaci abinci, sai wajen goma na dare suka miƙe dan komawa sashen Mammah saboda ganin su Uncle Ma'aruff sun shigo. Dama Nimrah kwance take shiru kamar mai barci, babu abinda ya tsaya mata a rai sai abinda Dada yay mata, kaɗan-kaɗan ta shafa lips tana jin abin kamar a mafarki ya faru, sai dai bata iya bama kowa labari ba, dan bazama ta iya hakan ba. Sai Baby Nasir dake saman cikinta shima yana barci. Ita kuma Babyn Lailah na bayan Aunty Shariffa ne ta goyata dan taji ɗumin baya ana kuma son cibiyarta ya ida faɗuwa da wuri.

Kamar Nimrah bazata bada Naseer ba dai ta haƙura ta bada shin suka fito. Sun iske har su Mammah sun shige, sai su Hinde suma sun kammala duk abinda ya dace zasu shige ne. Mu'azz ya haura sama su kuma suka shige nasu ɗakunan....

□□□□□□□

"Ke dai ƴar wahala ce. Wai bazaki daina ma mutane wannan kukan ba Hanoon. Dama mi zakiyi da shi. Mutum a murɗe. Ita wannan ɗin dake rawar kai ƙila rana ɗaya zai halakata har lahira. Banda ma rashin sanin hakkin ɗan Adam, taya za'a ɗauki wannan ƴar yarinyar da bata cika ko 18 ba a bama mutum irin wannan daya haifi wanda ya ma fita. 16 da wasu watanni fa naji ance. Koma 17 ɗin basu cika cif ba sai watan gobe. Ga uban ƙarfi. Ni wlhy ji nake kamar na kai su human right".

"Tunda baka da hankali ba. Wai Dayyan ina ruwanka. Kodai son yarinyar nan kake yi?".

"To Dad laifi ne idan naso ta. Ai ni ne ma dai-dai ita. Tana 17 ina 28 ya kaga haɗin?".

Sosai Uncle Tasi'u ya saki baki yana kallon sa. Shi bai san irin rainin da yaransa sukai masa ba. Har sha'awar yaga ƴaƴa na respecting ɗin iyaye yake. Jiba dai yau Adda A'isha da nata yaran, sun girma sun zama magidanta amma sai abinda tace sukeyi. Nashi ko gasu nan dai. Dayyan ɗin ne babba amma rashin hankali kamar kiwon tunkiyar wawa. Wani lokacin ma gwara Hanoon ɗin dake mace. Cikin sauke ajiyar zuciya ya ce, "Ya kamata ace kun canja ko yaya zuwa yanzu. Kodan zaman gidan nan da rayuwar da kuke gani masu gidan nayi. Yanzu kuna dai gani badan Haysam ɗin yasa baki ba wlhy sai kun bar gidan daga ni har ku. Kuma kunfi kowa sanin zamanku anan shine rufin asirinmu mu duka. Dan mutumin can ya tabbatar min idan ban biyashi kuɗaɗensa ba bazai bani gidan can ba. Kai a yanzu haka ya saka shi a kasuwa. Shiyyasa ma na biyema Afeef da tunanin ko videon zai taimake ni na samu wani abu wajen Adda na bashi. Ashe shi shashashan babu wani bincike yay abun. Na rasa ina zan saka kaina......"

"Hummm Dad duk fa abin nan kai ka jawoshi. Itafa harkar nan yanzu ba wani tafiya take ba. Mutane sun riga sun gane. Na fara koyon yahoo ɗin nan kayi kutun-kutun ka hana. Yanzu ma badan ɗan live ɗin nan na TikTok da Hanoon keyi ba da kayan da zamu saka ma sai sun gagare mu.Ga karatun Afeef ya tsaya".

"To ya kuke so nayi Dayyan. Duk ba kune da uwarku kuka sakani a bala'in nan ba....."

"A'a Dad, mu ka daina saka mana uwa a maganarka. Ta mutu ka barta ta huta kaji da kanka. Kuma mu ɗin ba ƴaƴanka bane. Kasan bazaka iya ɗawainiyarmu ba miyasa ka haife mu?".

"Ni wlhy kuna damuna da surutu. Dad dan ALLAH ƙyalesu. Ni yanzu ka taimake ni kama Mammah maganar Haysam. ALLAH na yarda zanje a matarsa ta uku".

Gaba ɗayansu zubama Hanoon mai maganar ido sukayi, sai dai kowa ya gagara cewa komai. Tausayi take basu ko haushi ma su basu sani ba..........✍

Hummm Uncle Tasi'u mi kake ɓoye wa ne? Da alama fa wuta ce ta kori ɓera daga rami ashe□. To muna biye maji ma gani matar ɗan hau ta zama malamar wa'azi□.
Received at 1:03 PM
[4/2, 10:38 PM] null: 26

..........Washe gari asabar. A gidan Mammah kowa ya tashi busy domin shirya tarbar baƙi. Dan yanda tsarin yake ƙarfe sha biyu zasu iso, anan zasuyi sallar azhar. Cikin amincin ALLAH kafin goma sun kammala komai. Babu abinda kake ji sai daddaɗan ƙamshin turaren SHUWA INCENSE AND MORE +234 704 229 3387. Ke tashi har compound. An gyara falon baƙi tsaff, duk abincin nan da aka haɗa an kaishi can an shirya.

Babu wanda yaga Dada a gidan har sai da Daddy Imran ya iso. Lokacin da suke sakkowa daga sama Nimrah najin ƙarar takunsu ta gudu kitchen. Rabonta da Dada tun jiya a ɗakinsa. Wasan ɓuya take da shi. Yanda ta tashi da sauri ta nufi kitchen ɗin yasa Mammah da Gwaggo Khadijah ankara da ita. Sai dai babu wanda yace komai.

Dada ma sarai ya ganta, dan sun riga sun kawo jiki sanda take saurin shigewa kitchen ɗin. Kauda kansa kawai yayi da maida hankalinsa ga Imran kamar bai ganta ɗin ba shima...

Alhamdullahi baƙi sun iso su biyar. Sai Baffa mahaifin Daddy Imran da Uncle Nasiru da Uncle Jamilu da Uncle Tasi'u daya maƙale ta ɓangaren masu karɓa kenan, sai su Dada da Imran, Ma'aruff su duka huɗun. Ja'afar, Bilal, Ammar. Anyi gaisuwa cikin mutunta juna, kafin iyayen Haydar su gabatar da abinda suka zo da shi. Sun nema a tsaida rana Dada yace in dai ba damuwa a ɗaura auren a yanzu kawai.

Babu wanda bai kallesa ba a falon, idan ka cire Imran, Baffa, Uncle Nasiru da Uncle Jamilu da suka san da shirin. Kawun Haydar dake murmurshi ya ce, “Aiko mun gode da wannan karamci Alhaji Haysam. ALLAH ya bar zuminci mukam mun amince”.

Jin haka suma sauran suka bada goyon baya, dama ƙanen mamansa ne sai yayunsa biyu da yayan waccan matar tasa data rasu, sai shi ƙanin mahaifinsa. A take suka ajiye sadaki aka ɗaura auren Haydar Galadima Faro da Habibah Nura a cikin falon nan da mutanen da basu gaza goma sha biyar ba. An kammala ana barka-barka aka koma kan batun Ruƙayya da Ammar da akama suprice, dan sam bai san da wannan shiri ba sai da Ma'aruff da Ja'afar suka matso gaban Dada matsayin masu nemawa ƙaninsu auren ƴarsa Ruƙayya. Kai tsaye Dada ya fuskance su, suma sun ajiye komai na aure dan ya tabbatar musu bazai raga musu ba dama su zo da shirinsu. Ya kuma yanka musu sadaki a wajen tare da faɗin, “Idan kun shirya ku kawo sadaki yanzu a ɗaura kuma, dan na shirya aurar da yarinyata. Amma biki sai sun kammala jarabawa ita da ƴar uwarta nan da wata ɗaya da kwanaki.”

Rawa sosai jikin Ammar ya kama yi, sai da Bilal dake ƙunshe dariya ya riƙesa. Suko su Dada da basu san yana yi ba atake Ma'aruff yace sun shirya, idan babu damuwa a musu lamuni a ɗaura nan da awa guda zasu kawo sadaki cash. Amma sai Dada yace ga account number su saka. Shi bai bada ɗiyarsa sai yaji dumus. Ba ƙaramar dariya aka sanya a falon ba gaba ɗaya. Yayinda al'amarin ya sake rikita Uncle Tasi'u dan shikam ya gagara gane alaƙarsu da waɗan nan yara guda biyu.

Ja'afar ya sanya kuɗin sadaki a account ɗin Dada. Daga haka aka ɗaura auren Abdul-rasheed Abdul-rasheed Shehu Kobi da amarya Ruƙayya Imran Abbas akan sadaki mai tsoka. Sosai Baffa da Daddy Imran suka ji hawaye ya cika musu ido. Haysam ya wuce ɗan uwa ko amini, shi gudan jini ne. Baffa najin tamkar shine ya haifi Imran da Haysam matsayin tagwaye. Kamar yanda su Bilal kejin Imran an haifeshi a gidansu ne tamkar Dada. Dan basa kallon wannan alaƙar matsayin abota a yanzu sai ta gudan jini. Abinda yaba kowa dariya yanda Ammar ya rarrafo ya rungume Dada yana hawaye. Aiko su Bilal suka fashe masa da dariyar da har su Mammah na joyowa daga falo. Hakan yasa suka fahimci lallai zaman na bada nishaɗi.

Baffa ne ya katse yanayin nasu da faɗin, “Indai haka ne inaga maimakon wahalar da kai a gobe a sake wani zaman shima Bilal kawai ayita ta ƙare shi da Ma'u. Sai suci albarkacin juna. Ba ƙaramin daɗi Dada yaji da hakan ba, dan a ransa yaso kawo hakan ya ga dai kar suyi karan tsaye shiyyasa ya daure. Bilal aka mintsini Ammar irin yaro nima fa lokaci yayi ɗin nan. Aiko sai da Ammar yay dariya ga nashi hawayen yana karasa sharewa. Su su Ja'afar farin ciki fal ransu.

Received at 6:40 PM

Viewed 24 timesƳan ƙannensu duk sun zama manya. A take yanzu kam Dada ya ajiye komai na ɓangaren Bilal shi kuma. Uncle Nasiru da Uncle Jamilu suka basu auren Asma'u, nan ma aka sake ɗaurawa a karo na uku. Hakan kuma yay dai-dai da kiran sallar Azhar dan haka suka miƙe idan sun dawo aci abincin da aka shirya kuma..

( Rige-Rigi yanzu dai auren falo ake yayi, na massalacin ma zakaga iya dangi ne ￼￼. Amare ALLAH ya sanya albarka ya bada zaman lafiya. Su Ruky da Small Mom da Ma'u za'a shiga daga cikin￼￼￼).

Aurarraki kam sun ɗauru Alhamdullah, sai dai Dada yace su duka ba yanzu za su sani ba. Dan haka koda su Ma'aruff suka shigo an amshi kuɗi an kuma tsaida rana nan da wata ɗaya kawai aka sanar ma kowa. Sai dai Uncle Nasiru da Uncle Jamilu sun ja su Mammah gefe a ɓoye ita da Gwaggo Khadijah da Gwaggo Alawiyya sun sanar musu duk yanda akayi. ALLAH sarki Mammah harda hawayen farin ciki ta share. Jinta take sakayau kamar an sauke mata kaya. Alƙawarin UBANGIJI ya cika ta kammala aurar da ƴaƴan Abdul-rasheed ƴaƴan amana. Yau da Abdul-rasheed da Yakura na raye yaya zasu ji?. Kuka take sosai har sai da su Gwaggo Alawiyya suka koma lallashinta. Duk da suma sunyi irin tunaninta kuma sunyi hawayen tuna ɗan uwa mai

zuminci da son kowa irin Yaya Abdul-rasheed. Basu kaɗai ba shi kansa yau Uncle Nasiru sai da yay hawaye. Rayuwarsa da ɗan uwansa, aboki, aminin arziƙi irin Abdul-rasheed da har yanzu bai maye madadinsa ba a wannan duniyar ta dinga dawo masa. Daren jiya sai da yay mafarki da shi sunata hira, ashe wannan alkairin ne na yau.

Tuni su Ruky da Nimrah sun rikice da farin cikin zasu sha bikin Small Mom da Aunty Asmy. Harda zagaye Biebah su da Mu'azz suka fara raira waƙoƙi suna rawa abinsu. Daga ƙarshe ma suka kunna waƙar sani martaba ta MINE NE SO MINENE ƘAUNA a wayar Mu'azz suna mata. Dariya su Mammah suke musu, yayinda Ammar ya kafe Ruky da ido yana jin abin tamkar almara ko mafarki. Tsawon shekaru yake danne abun nan a ransa, badan komai ba sai dan yana burin har sai ta kai girma. Hatta Haneef shine ya samesa da uban gargaɗi akan Ruƙayya, har suka nema yin faɗa sai da Aunty Mimi ta shiga tsakani dan a gidanta akai abin. Ita a lokacin ne ma tasan Ammar ɗin na son Rukayya. Sai dai ya roƙeta tai shiru ba yanzu ba sai Ruky ta shiga University. Sai gashi yau cikin bazata su Dada sun masa abinda bai taɓa kawowa anan kusa ba.

Caraf kuwa Ruky ta kama Ammar na kallonta, da yake babu man kai bata fahimci a yau salon kallon ya canja ba. Hasali ma zuwa tai gabansa ta zauna tana faɗin, “ALLAH sarki Uncle har ka bani tausayi. Ya naga kayi shiru? ko kana kishi ne Small Mom ta rigaka aure?. Karka damu zamu lallaɓa Dada ni da Ninah kaima a aura maka ko ƴar budur-bazar ce. ALLAH da gaske nake tausayi ka ya kamani. Yanzu fa duk iyayenmu na gidan nan sunyi aure sai kai kaɗai aka bari. Mammah ALLAH shima Uncle Ammar aure yake so a tausaya masa jibi idonsa ma kamar yayi kuka”. Tana maganar ne tana zabga tagumi da kallonsa irin da gaske ya bata tausayi ɗin.

Bilal da su Ja'afar suka ƙunshe dariya. Sauran kuwa sun gaza hakan. Gaba ɗaya falon aka fashe da dariya. Ita ko ko'a jikinta. Sai ma ƴar uwar ɗayar ce ta matso suka saka shi gaba su duka. Ganin zasu addabesa ya ɗauki filo alamar zai dake su. Da gudu suka tashi suna dariya suma suka koma inda Biebah tasa hijjab ta ƙudundune kanta saboda waƙar da suke mata kawai sai taji kuka nazo mata. Haka kawai take jin kanta wani iri, harga ALLAH wata ɗayan nan da yayunta sukace an saka jitai ya mata kaɗan, dan ta zata kamar shekara za'a saka ma. Ba kuma taji kukan yazo mata ba sai yanzu da taga massage ɗin Yaya Haydar ya shigo wayarta. Dan wasu tsumammun kalamai ne masu zaƙi da saka zuciya nutsuwa tare da tabbatar mata ta kusa zama Halal ɗinsa ya turo mata.

Sun sha bidirinsu har sai da Gwaggo Alawiyya ta korasu ɗaki suka bar Biebah da Uncle Bilal suka huta. Lokacin da baƙi suka wuce su Dada suka shigo basu samesu a falon ba ma......

==============

Received Bayan wucewar baƙi Dada da Daddy Imran sun kai Baffah gida ne. Daga can suka zauna hira da Hajjo. Basu baro gidan ba sai gab da magriba. Sai da sukai sallar magriba da isha'i suka nufi UNIT ZERO. Ba sufi awa ɗaya ba suka samu saƙon shugaban ƙasa da tun jiya suka tura masa na izinin ganinsa. Shine bai basu amsa ba sai yanzu. Suna ganin saƙon basu ɓata lokaci ba suka bar UNIT ZERO zuwa address ɗin daya tura musu, dan a ƙage suke dama da hakan.

Tun a ƙofar ƙaramin gidan da sun jima da sanin nasa ne suka samu dogarinsa na jiransu. Bayan an buɗe musu gate suka shiga ciki. Dogarin shugaban ƙasa yazo ya isar da gaisuwa a garesu sannan yay musu iso ciki.........✍

[4/2, 10:38 PM] null: 27

.........Janar Yusuf Shu’aibu Tafida yana tsaye kusa da window ɗin falon duk yana kallonsu har suka shigo. Bai juyo ya kallesu ba har suka zauna. Shayi mai daɗin gaske da aka tanada dogarinsa ya zuba yakai gaban su, sannan ya ajiye na Janar a gefen kujerar da yasan yana zaune kafin shigowarsu. Sai a lokacin Janar ya baro jikin

window ɗin shima, idanunsa a kansu yakai zaune a kujerar da yake tun farko dake facing ɗin su. Yanda yake ta gyara fuska zaka san dariya yake gimtsewa.

“Da alama taron dangi aka zo yimin dai yau ɗin nan?”.

Ya faɗa yana sake kafe su da ido. Karo na farko sukai murmushi da fara gaisheshi. Ya amsa da kulawa yana cigaba da faɗin, “Ina fatan tattauna yanda za'a tafiyar da Offices ya kawo ku, ba tambaya ba?.”

Kallonsa duk sukayi, ganin tun a farko ya musu takunkumi akan abinda suka zo da shi. Imran ya kalli Dada na ɗan sakanni, sai kuma ya sake maida kallonsa ga Janar. Ganin yanda har yanzu shima yake kallonsu yasa ya janye, cikin nutsuwa ya furta, “Sir… waɗan nan offices ɗin fa sunyi girma da yawa. Za’a dinga kallon mu kamar......”

Cikin son katse shi Janar ya yi murmushi kaɗan, murmushi irin na wanda ya riga ya san hakan zata kasance.

“Saboda suga kamar haka ɗin, shi yasa na yi hakan ai Imran”.

Dada bai ce komai ba yana sauraren su dai, sai dai ya zuba idanunsa akan Janar kai tsaye, ba raini, ba ƙalubale.

A karo na biyu Imran ya sake faɗin, “Sir, muƙamin nan na zahiri zai iya ɗauke hankalinmu. Kasan muna da aikin bayan fage fa”.

Janar ya jinjina kansa yana gyara zamansa bayan ya ajiye kofin shayinsa. Murya a ƙasa, amma da nauyi a cikinta ya ce.

“Imran ko bayan wannan aka ƙara wasu offices ɗin nasan zaku iya. Dan haka babu abinda zai canja daga ƙwazonku na zahiri, sannan riƙe wannan offices ɗin da shine zai rufe wancan aikin namu na bayan fage hankalinsu duk ya dawo nan mu jefa tsuntsu biyu da dutsi ɗaya. Dan haka babu abinda zai canja nake gani. Idan ma akwai wanda zai iya canjawar shi ne… yanzu su zasu dinga kallon hannunku, ba zuciyarku ba.”

Imran ya lumshe ido na ɗan lokaci. Ya gane. Dada shima ya gane. Dan haka a karo na farko ya furta, “Amma ranka ya daɗe kasan Jam’iyya zata yi hayaniya”.

Janar yay ƙaramar dariya. “A tun a jiya take a motse, sai dai ko zata harmutse babu canji. Dama nayi ne saboda munafukai zasu motsa. Ƙungiyar duhu zata ɗauka dama ce a hannunta. Mu kuma sai muyi amfani da hakan mu damesu tamkar ana dama fura a ƙwarya”. Janar ya ɗan dakata yana sauke numfashi, sai kuma ya cigaba da faɗin, “Na bar musu hakan. Ku kuma ku biyun… ku zama abin da ba su zata ba.” Shiru ya sake biyo bayan a maganar tasa. Sai kuma ya sake cigaba da faɗin, “Ba umarni ba ne kawai nake bayarwa a gareku ba a wannan daren, alkawari ne na ɗora akan ku biyu matsayin  inuwa ɗaya, ba duhu ɗaya ba”.

Kawuna suka shiga jinjina masa cike da nuna gamsuwa. Janar ya ɗauki kofin shayinsa dake a kan teburi. “Litinin zaku shiga office dan bamu da lokacin ɓatawa. Amma daga wannan daren… aiki ya fara.”

Yanzun ma kawuna suka jinjina masa irin na sojojin da suka san sun shiga yaƙin da ba a rubuta sunansa ba. Daga haka shiru ya biyo baya, Janar na murmushi da shan shayinsa, a ransa yana raya (ba sabon COS kawai aka haifa ba, ba kuma sabon NSA kaɗai ba. Ku makamin ƙare dangi ne waɗan nan sojojin guda biyu. Ina sha ALLAHU sai The two Shadow sun zama makamin tarwatsa munafukai a ƙasar nan....)

××××××××××××××

Washe gari lahadi da yamma su Nimrah na compound suna ƴar ɓurun-ɓurun kasancewar aminansu biyu suma a gidan suka yini yau. Bintu da Feedo. Su Mammah na daga falo suna tasu hirar. Mazan gidan kam zamu iya cewa babu kowa sai Dada. Shima yana ɗakinsa salla kawai ke sakko da shi, dan yau yace yana son ya huta a gida sosai.

Su Ruƙayya sun shagala da wasan su sosai cikin matuƙar nishaɗi. Dan sunata guje-guje ne an ɗaure ma Feedo idanu tana faman bulayin neman samun wani ta

taɓa amma ta kasa. Sai ma wannan ya taɓata ta nan ya gudu, wannan yaja mata riga. Wannan ya mintsineta suke. Ita ko ta kasa samun sa'ar kama kowa.
ReceivedZuwa can tsautsayi ya kawo Nimrah ta ja mata riga, mai makon ta gudu sai ta kai hannu zata sake mintsininta. Aiko caraf Feedo ta cafketa.

Miko zasuyi idan ba dariya ba. Nimrah na tuttura baki aka ɗaura mata, duk suka gudu domin ɓuya, lokaci-lokaci suna mata irin na Feedo amma ta gagara kama kowa. Sai faman lalube-lalube take kamar sabuwar makauniya. Duk wannan abu da suke yi Rayhana da Amima na barandar sashensu zaune. Sai dai sai faman taɓe baki suke suna zaginsu batare da sanin takamaimai laifin da sukai musu ba. Ga shi kuma babu damar zuwa su taresu faɗa dan sun san yaran tsagerancinsu yafi nasu, tas zasu goge musu hadda sai dai ƴar bayan fage ɗin wai faɗan mai tsoro. Ba Ruƙayya da Nimrah kawai ba, hatta Feedo ɗin da Bintu babu kanwar lasa a ciki.

A wannan lokacin Dada ke fitowa a sashen Mammah, sanye yake cikin simple kaya duk baƙaƙe daga wandon har rigar. Sai slippers ɗin ƙafarsa daya kasance ash. Hannunsa ɗaya da files guda biyu da laptop, sai ɗayan riƙe da wayarsa daya manna a kunne alamar magana yake da wani. Tun fitowarsa yaga su Nimrah, amma sai ya basar ya cigaba da tafiyarsa, dan yana son zuwa rumfar bunun dake a compound ɗin can gefe ya sha iska tare da jiran Imran da ya kira shi a waya yanzun akan wani batu mai muhimmanci.

Yazo gab da su Nimrah da sam basu san da fitowarsa ba. Ruƙayya ta mintsini Nimrah ta gudu, dan haka take laluben inda zata cafkota tana tafiya. A karo na farko Dada ya kalleta a kaikaice, ya kalla mota da take nufa, kuma ta saitin mirror ɗin gaban motar daya tabbatar idan ta ƙarasa mirror ɗin zata buga da cikinta.

Dai-dai Nimrah takai jikin motar, ƙiris ta buga cikinta da mirror ɗin Dada ya shiga tsakkiya, cikin rashin sani ita kuma jin hucin mutum kawai ta tafi gaba ɗaya da nufin riƙe ko wanene sai gaba ɗaya ta faɗa jikinsa. Yanda kanta ya bugi ƙirjinsa da yanda ta faɗo masan yasa bayansa ɗan buguwa da mirror ɗin da ya bata kariya a kansa. Sosai yaji zafi, dan har sai da ya runtse idanunsa tare da yamutsa fuskarsa. Ita kuma a dai-dai lokacin ƙamshin turarensa ya gama gauraye hancinta zuwa brain. Da sauri ta kai hannu ta janye abinda aka ɗaure mata ido da shi. Aiko idanunta caraf a cikin nasa dake kallonta.

Da gudun tsiya tai maza ta rufe nata idanun ƙirjinta na bugawa. Rabonta da shi tun ranar juma'a a ɗakinsa. Dan wasan ɓuya take da shi yau kuma ga shi an haɗu a bazata. Jikinta dake tsuma tai ƙoƙarin janyewa, sai dai bisa tsautsayi ta tuzguɗe ƴar ƙafar dole ta sake dawowa jikinsan dai tare da rirriƙesa. Shima kuma da yaji tana neman zubar da su babu arziƙi yasa hannunsa dake riƙe da waya ya tallafo ƙugunta da ƙyau yana manneta da jikin nasa sosai idanunsa akan fuskarta..

Wata ashariya Rayhana ta buga daga inda suke suna kallon komai. Hakama Amima cike da kishin ƴar uwarta ta tayata. Yayida su Feedo suka waro ido waje dan sun san yau Nimrah za taci ƙaniyarta maybe ma harda su. Ruƙayya kuwa idanu ta rufe tana dariya cike da farin ciki. A cikin ranta har da faɗin (Awwwwhh shoshalewa Dada da My Trouble Queen) sai kuma ta ɗan sake leƙo idanunta ta tsakkiyar yatsunta. A dai-dai lokacin Nimrah ke kiciniyar janye jikinta. shi kuma Dada yaƙi sakinta sai ma kallon nata dai da yake yi ƙasa-ƙasa.

“Kiddo marayan ALLAH kike son zubarwa a ƙasa?”.

Furucin ya suɓuto a bakinsa batare daya shirya ba. Shigarsa kunnen Nimrah kuma ya sata dakatawa daga mutsu-mutsun nata ta kallesa. Lips ɗinta ke motsi alamar son yin magana amma ta kasa. Gashi ya sarƙe idanunsu waje guda ya hanata janye nata da har sun fara tara ruwan hawayen jin matuƙar kunya daya sashi ganin sun ƙara ƙyau. Nasa ya lumshe a hankali tare da sake buɗe su a kan natan dai. Sai kawai Nimrah ta samu kanta da tura masa baki.

Bugun da yaji zuciyarsa tayi ya saka shi kauda kansa gefe yana sakinta. Sai kuma ya yinƙura zai bar wajen da faɗin, “Jeki kawo min coffee”. Daga haka yay wucewarsa ya barta da bugun zuciya da tsumar jiki. Dan gaba ɗaya jin kanta take kamar a dokar

jeji babu gida gaba babu baya ga ƙaton zaki tsaye a gabanta yana kallonta da lasar baki.
Received at 6:40 PMSai da Ruky tazo ta taɓata ta sauke ajiyar zuciya mai ƙarfi, suna haɗa idanu Ruky ta ɗaga mata gira da kashe mata ido ɗaya tana murmurshi.

Harararta Nimrah tayi, Ruky ta ƙyalƙyale da dariya tana kai bakinta saitin kunnenta ta furta, “Madam bar wani borin kunya kin gama more min jikin Babana. Inyeee My Trouble Queen a jikin Dada shoshalewa”. Sai kuma ta fara rairai mata waƙa tana rawa da zagayata.

“Sunanki ne a zuciyata”.

“Ni naki ne Sahibata”.

“Aurenki ne manufata”.

“Hakkin ki ne na baki gata”.

“Wataran watara na, za'a kai ki gidana, matsayin matata. Kece madarata”.

“Wataran watara na, za'a kai ki gidana, matsayin matata. Kece madarata”.

“Na matsu, na matsu, na matsu naga wanan rana!!”.

“Na matsu, na matsu, na matsuuuuu. Nace! na matsu. Na matsu, Na matsu naga wannan rana. Na matsu- na matsuu na matsuuuu.....”

Dukan da Nimrah takai mata ya sata barin wajen da gudu tana dariya. Sukam su Feedo dake isowa yanzu cikin damuwa suke tambayarta Dada bai mata faɗa ba ko?.

Kai ta girgiza musu, yayinda cikin shaƙiyanci Ruky tace, “Wane faɗa kuma ana harkar lada”. Sam basu mahimci abinda take nufi ba. Sai ma duka da Bintu takai mata. Nimrah kuma tabar wajen zuwa kawo coffee..........✍
[4/2, 10:39 PM] null: 29

.........Gaba ɗaya kallonsu ya dawo kan Nabeeha da jikinta ke tsuma. Ga butar shayi da shayi tarwatse a ƙasa. Ganin inda take kallo ya saka su sake maida kallonsu wajen. Sai dai banda Dada da tunda yay mata kallo ɗaya ya ɗauke idanunsa kamar bai san abinda ake ba. Cirko-cirko kowa ya sake yi ganin Adeel da Nabeeha ke kallo, yayinda shi kuma Adeel ke kallon Nimrah a yanzu. Wata banzar harara Nimrah ta zabga masa ganin ita yake kallo, ranta a ɓace ta kauda kai ta maida hankalinta ga Dada tana faɗin, “Dada a saka suga?”.

Kai ya girgiza mata, sai kuma ya sake kallon Adeel da yake kallonta ta gefen ido. Ganin idanunsa akan Nimrah ne yanzu ya sake tsuke fuska. Cikin farga Ammar ya taɓa Adeel, ya ɗanyi firgigit alamar dawowa hayyaci yana sauke ajiyar zuciya. Imran dake nazartar kallon da Nabeeha kema Adeel shima yay gyaran murya. Kamar wadda ta dawo a suma taja numfashi ta fesar, sai kuma ta fara kame-kamen kaiwa duƙe tana tattara butar shayin data fashe hannunta na rawa.

A zahiri zaka rantse Dada bai ga abinda ke faruwa tsakanin Nabeeha da Adeel ba, amma yafi kowa fahimta da nazartar komai a wajen. Dan Nabeeha na haɗa kwalaben waje guda tana ɗagowa ta saci kallon Adeel ta saci kallon Dadan, wani kallo da ya watsa mata sai da taji kamar zata saki fitsari a wajen, sai rawar jikinta ta nema ƙaruwa.

Daddy Imran yakai zaune Nimrah na gaishe sa fuskarta da murmushin murnar ganinsa. Shi kuma Ammar ya jawo hannun Adeel suma suka shigo cikin rumfar sosai yana faɗin, “Dada. Yaya Imran ga abokina Adeel zai gaishe ku”.

Murmushi Imran yayi yana nuna musu sauran kujerun biyu da suka rage. Ammar ya zauna a kusa data Dada, shi kuma Adeel kusa da Imran. Sai ya zama Adeel na facing Dada, Ammar na facing Imran. Kasancewar kofuna biyu ne kawai Nimrah ta zubama Daddy Imran shayi shima. Ta kalla Ammar cikin ƴar shagwaɓa ta ce, "Uncle kaima fa yanzu sai kace sai kunsha ko?".

Ammar ya ɗan harareta da faɗin, "Ninah bana son harkar rowa. Miye na kandagarkin to?".

Baki ta tura da faɗin, "To Uncle da wahala ne zuwa kitchen na dawo."

Ammar yay dariya, zata sake magana Dada da yakai ƙarshen ƙulewa da shagwaɓar da take ma Ammar ga Adeel daya tsaya masa a wuya cikin kaushin murya ya furta, "Kiddo bar wajen nan".

A yanda yay maganar bama ita kaɗai ba harta Ammar nutsuwa yayi. Imran yay guntun murmushi. Adeel kam jiyay zuciyarsa na girgiza. Dan har tsakiyar rai yaji fitar sautin golden voice ɗin Dada dake fita da ainahin gizagon mazan da basu san kalmar wasa ba. Ya haɗiye yawu da ƙyar yana kallon Nabeeha dake kallonsa cikin roƙo da magiya. Dan ita tashin hankalin da take ciki ma yafi na kowa. Dada daya ƙara ƙuluwa duk da ita Nimrah harta tafi ya watsama Nabeeha kallon gargaɗi itama. Ita kam ko kallo yay tana gane abinda yake nufi ba Nimrah da sai ya furta ba. Da sauri ta bar wajen jikinta na rawa zuciyarta na tsitstsinkewa. Tambayar kanta take, "Ya akai Adeel yasan gidan nan? A ina suka san juna da Ammar? Mi yazo yi gidan?". Bata da mai bata wannan amsar, babban burinta kawai takai kanta sashensa ta kira Momy a waya......

>>>>>%<<<<<

A ɓangaren ƙungiyar duhu basu samu zama ba sai a yau a wannan yammaci na Lahadi. An samu tsaikon zaman ne sakamakon Oga Jush baya ƙasar da wasu jigajigan tafiyar. Sai a yau suka gama hallaruwa gaba ɗaya. Dan haka ko zaman hutawa basuyi ba akai zaman meeting na gaggawa.

Kamar yanda suka saba. A meeting room ɗinsu suke mai zurfi da duhu duk da rana ce kuwa, amma fitila guda ɗaya ce ke haskawa an rufe windows an saki labule. Baka jin komai sai sautin bugawar zukatansu dake tabbatar da ɓacin ransu a bayyane. Wasun su sai zufa suke dan yau ko ac basu kunna ba tabbacin tashin hankalin da suke ciki.

Oga Jush, da fuskarsa tafi ta kullum zama kalar firgici cikin umarni ya furta, "Ina buƙatar son jin sanarwar da kunnena".

Received at 3:05 Raven ya ɗauka wayarsa, kai tsaye ya shiga intanet ya samo videon dake ta yawo har zuwa yau tamkar wutar jeji saboda yanda bakunan ƴan siyasa yaƙi rufuwa daga cecekucen.

"…Mr. Haysam Abdul-Rasheed Shehu Kobi is appointed as Chief of Staff to the President. & Mr. Imran Abbas is appointed as National Security Advisor…"

Ɗakin yay shiru. Kowa yana jiran cewar Oga, amma yaƙi ya tanka sai da ya mula dan kansa sannan ya furta. "Ministoci nawa ne damu a ciki?".

Kai tsaye Mr Specter dake a tsorace tunda yasan shine ya kawo Janar ɗin ya furta, "Biyar a cikinsu duk namu ne. A wanda za'a sake badawa ma mune mafi rinjaye".

Batare da Oga Jush ya kallesa ba ya bashi amsa da, "Suma sauran duk su zama namu. A shirya vice president zai koma president nan da ƙarshen wannan shekarar".

Babu wanda bai girgiza ba, duk da su dukansu basu san kalmar tausayi ba. Amma furicin Oga na nufin ɗayan biyu ne. Kodai za'a kwantar da Janar yana raye komai sai an masa kamar na baya, ko za'a binne shi cikin ƙasa matsayin gawa. Sai dai babu damar yin koda musu. Amma a wannan gaɓar akwai masu alaƙa da Janar tun kafin wannan ƙungiya, akwai kuma irin su Garba da suka afka kansu ciki duk da suna gidan soja a zahiri.

Cikin ɗacin murya Viper ya furta, “Su kuma waɗan ƘAYAR KIFIN fa? Ya haɗa su biyu fa a mafi girman muƙamai.”
Cikin fushi Mr Scythe ya amshe zancen kafin Oga ya amsa ma Viper ɗin. “Viper wannan ba siyasa bane ai. Yaƙi ne tsakanin masarautu guda biyu. Dole kuma sarki ɗaya ne zai rayu. Kuma mune”.
Black Spider ya ce, “Tabbas maganarka gaskiya ce Mr Scythe. Zak-Shadow bai fito fili ba sai da izini. Kuma idan ya fito... yana nufin an riga an shirya wani abu. Hakan na nufin a yanzu bama buƙatar hargowa ko fito-na-fito da shi. Yaƙin sunƙuru za'a fara. Ta hakane za'a banbance SARKIN da zai karɓi wannan KUKERAR IKON a tsakanin mu da shi”.
Karo na farko Mr Specter ya furta, “Ai ni ban taɓa ji da ganin abinda ya girgizani ba irin wannan. A lokacin da naji ji na dinga yi kamar sunan aljanu aka ambata. NSA da COS... inuwa biyu a kusa da shugaban ƙasa. Ni Yusuf Tafida zai ma haka?”.
Kafaɗarsa Iron Fang ya dafa, cike da son kwantar da hankali ya furta, “Karka wani damu kanka, ya kawo kansa ramin Damisa ne ai bai sani ba. Mu ma kuma a yanzu dole ne mu sake lura. Saboda idan mun kusanci Tafida, zasu ji. Idan mun matsi Zak-Shadow, zamu ji.”
Ƙaramin tsaki Oga Jush yaja. Cike da takaici da zafin furuci ya furta, “Ku daina kallon mukami. Ku kalli abin da yake ɓoye a bayansa.” Ya ɗan tsaya yana jan numfashi, kafin ya cigaba da murya mai zafi, “Wannan naɗin ya tabbatar mana da abu guda... Tafida ya san muna nan.”
A take meeting room ɗin ya sake zama tsitt. Wasu suka gyara zama. Raven yay ƙarfin halin faɗin, “Tabbas Oga maganarka nakan hanya, dan wannan abun da yayi tamkar yana son nuna shi KIDA A RUWA ne MAI SON TADA HANKALIN DODO. TO menene mataki na gaba?”.
Kai tsaye Oga Jush ya amsa da, “Mu bar su su ji daɗin watan farko na sabon office. Litinin ɗin sabon wata... zamu fara gwada ƙarfin inuwa.”
Jikake raf! Raf! Tafi ya karaɗe ɗakin. Wasu na murmusawa a duhu. Cike da shaƙiyanci Black Spider ya fusta, “The two shadows?”.
Viper ya amsa masa da, “A’a... Yanzu sun zama targets.”
A tare suka fashe da dariya irin ta mugunta da mugun ƙudiri......

<<••••••>><<••••••>>

Kai da kaga yanda Adeel ke mutsu-mutsu a wajen zaka san a takure yake. Ga Dada ya haɗe gabas da yamma ko gaisuwa a daƙile ya amsata. Daga nan ya cigaba da aikin gabansa kai kace yama manta da su a wajen. Sai Daddy Imran ne ke hira da Ammar.
Tabbas a wannan gaɓar Adeel jinsa yake ba komai ba. Babu sarauta babu gadara babu fariyya irin ta jininsa. Yo ashe ma idan kaga shege na gwada shegantaka ga wani jinsin mutane irinsa sai a inda yake da ƙarfi da faɗa aji. Dan akwai a inda idan ya aikata ubansa zaici koda kuwa ace a zahiri ya mallaki duniya da dama data wanda yake ganin kaskantattu sai shine mafifici.
Received at 3:05A cikin mintuna ƙalilan ya fahimci dalilin da ya saka bazai taɓa iya burge mace irin Nabeeha dake fifita soyayya sama da kuɗi ba. Wanda keda wannan tsayayyen jarumin namijin a shi idan ka cire dukiya, kyan fuska da gidan mulki mike gareshi? Sufa irin waɗan nan mazan badan ƙyawu, dukiya ko wani matsayin duniya ake son su ba. UBANGIJI ya gama mallaka musu abinda ba waɗancan abubuwan ba, ko su maza irinsu da suka mallaka sai sun risina musu da jinjinar ban girma. Ya sallama baida abokin faɗa anan, amma zai wajiga rayuwar Nabeeha da Uwarta, dan dole ne suyi aman abinda suka ci nasa. Abu na gaba kwantar da kai, tabbas zai yi biyayya kuma anan ɗin dai domin samun ɗaya tilon sa Nimrah. Dan ya fahimci Nimrah ɗiyar mijin Nabeeha ce kenan. Maybe ma UBANGIJI ya jarabcesa da Nabeeha ɗin ne dan ya kawosa ga Nimrah, ba kuma zai yi sakaci da wannan damar ba. Ko zuri'arsa naso ko basa so, ko zasu sallamashi ma duniya sai ya mallaki Nimrah. Dan

zai iya faɗa da kowa akanta, duk tsanani kuma bazai iya sallamawa ba koda a numfashinsa na ƙarshe ne. A yanzu haka yana shirin saye estate ɗin su Yohan ne gaba ɗaya, dan kasuwanci ma yake shirin kafawa a ƙasar saboda yanda yake jin daɗin zama cikinta, wasa ɗan gaske ya shirya yi akan Abu biyu. Nimrah da Hajiya Hasiba da ƴarta Nabeeha koda yaƙin zai ci ƙasar.........✍

Hhhhhh anayi muna shan shayi, to Adeel bari muga ko wasan naka zai zama abin kallo a gare mu. Ƙasar dai idan bata tashi dan kai ba, to zata tashi da kai a ciki kuwa🤷🏻‍♀.

Received at 3:05 PMKullum daga shinkafa, sai taliya da tuwo a gidanki. A'a Hajiya Balki ai an wuce wannan ƙarnin tuni. Mata sun gane yanzu. Idan kuma kin tsaya kallon ruwa lallai kwaɗo zai miki ƙafa, dan kina ji kina gani mijinki zai koma bin gidajen abinci. Daga haka a barbaɗesa kuma😝, to ni dai ba ruwana🤣, na nuna muku hanyar da zata fishe ku. Wato Ramadan class na Chef Yakudima, bama sai Ramadan ba, ko yaushe ajinta na koyon girki abuɗe yake. Nima dai Bilyn Abdull banga ta zama ba. Dole naje domin sake damƙe Bawan ALLAHn nan Malam Audu a hannuna🤣. Chef Yakudima zo mu saka labule🤣.

×××××××××××

“Ruky dan ALLAH ga abincin nan ki miƙama Uncle Ammar. Yace a bama Mu'azz ya kai masa kuma ban ganshi ba”.

Kallon Mammah Ruƙayya tayi, dan tasan in har Uncle's ɗin nasu na ɗaki bata aiken su ciki. Dama shara ce ta safe ke kaisu. Idan har ka gansu da yamma ko da rana to su suna falo ne suka aike su ɗakko abu ko basa gidan Mammah ta aikesu, mafi yawancin lokaci ma sunfi saka Mu'azz. Jin batace komai ba, kuma bata miƙe ba Mammah ta kallesu, dai-dai itama Kulu ta buɗe baki zata sake magana sai tai shiru.

“Amsa ki kai masa”.

Cewar Mammah tana kallon Ruƙayya. Mamaki sosai ya kama Ruky, amma babu musu tsakaninsu da Mammah dan haka ta miƙe ta amsa ɗin...........✍

Jama'a, karfa ku bari ayi bikin shagalin girke-girken online class na Chef Yakudima babu ku😘🏃.

Ga Ruky kuma za'a fara aikin lada🤣. Bari muga ya za'a kwashe🤣. A barku haka ko a ƙara biyun♀?.

Received at 3:05

[4/2, 10:39 PM] null: 30

...........“Malam duk kabi ka rikita yaro da wannan kallon naka sai tsuma yake kamar mai tsutsar basir. ALLAH kai mugu ne”.

Hararar Daddy Imran Dada yayi, tare da faɗin, “Kai ai duk duniya ba wanda ka raina sama dani. Ni ubansa ne da zai yi tsumar jiki a kaina? Tunda ni mugu ne kai ne na'ibina ai”.

Dariya Imran ya shiga tuntsurawa. “ALLAH Serious a rikice yake. Ko Ammar ya sha jinin jikinsa ne shiyyasa yace suje.”

“Su suka sani, amma tun wuri ka dakatar da shi zuwa gidan nan inba haka ba kuma huumm.....”

“A'a yi haƙuri mu gara ka barshi yazo mu samu abinda muke so. Amma fa yanda Nabeeha ta razana yafi komai ɗaure mun kai, shima yanda yake kallonta kamar sun san juna.”

Dada dake kallonsa ya ɗan ciza lips. Ga hannunsa ya dunƙule alamar fushi. Imran daya fahimci halin da yake ciki ya sauke numfashi da faɗin, “Relax! Zak... Mubi

komai a sannu, in sha ALLAHU zan sabunta bincike akansa. Dan tabbas ina ji a jikina ba business ya kawo shi ƙasar nan ba kawai.”

Idanu Dada ya lumshe tare da buɗesu a lokaci guda. Cikin ture zancen ya ce, “Ya ake ciki da yaran nan?”.

Shima Daddy Imran sakin zancen yay kawai. Sai kuma ya miƙa masa takardu da ya ajiye gefensa. “Komai ya kammala. ALLAH ma yaso naje yau ɗin da an samu matsala. Dan gobe zasu rufe registration ɗin.”

“Dama Auta ta faɗa ai. Yanzu dai tunda anyi Alhamdullah. Yaushe zasu fara exams ɗin?.”

“Babu wani nisa nan da sati biyu ne”.

“ALLAH yasa muna da rabon kaiwa. Haydar ya kira ka ne?”.

“Humm kaga zan manta ba. Ya kirani yana sanar min kamar sun gano inda drivers ɗin nan suke fa, kuma suna zargin wanda muka sani ne Ogan su, bai wuce kuma Ojo ba. Sai dai basu tabbatar ba, gadai jami'an farin kaya zasu fita operation tare da Dabo”.

“Ni bana jin wani shakkun shine.”

“Kayi aiki a ɓoye kenan?”.

Murmurshi mai faɗi Dada ya saki amma bai ce komai ba. Imran dake murmurshin shima da jinjina kai ya ce, “Aljanancin ka na bani tsoro Haysam.”

Dada bai ce komai ba nan ma. Dan haka Imran ya sake faɗin, “Malam Buba ya dawo ne?”.

Kai Dada ya girgiza masa alamar a'a.

“Kenan ta tabbata mutumin nan munafuki ne? Yanzu ta ina zamu fara?”.

“Karka damu, zasu zo hannu cikin sauƙi. Yanzu haka akwai jami'an da nake son ya kasance kan aikin.”

“Hakan yayi, sai office. Kasan dai ba fashi dole gobe idan ALLAH ya kaimu mu fara shiga”.

“Humm wato Janar ko....?”.

Dariya Imran ya sanya. “To ya muka iya, ya riga ya ɗaure mu, kuma tsarin yayi. ALLAH ya ɗora nasararmu akan tasu kawai....”

“Amin ya rabbi to”....

□□□□□□

“Momy wlhy na shiga uku.....”

“Kamar ya kin shiga uku Nabeeha? Ba sallama ba gaisuwa sai zance shiga uku. Nifa matsalata dake rashin hankali”.

“Momy dole nake faɗar haka, Adeel ne fa a gidana.....”

Wani kalar rikitowa Hajiya Hasiba tai daga samon gadonta. Sai kuma ta kalla First Lady dake kallonta dan suna tare ne a saman gadon. Ɗauke kai First Lady ɗin tayi, itama Hajiya Hasiba sai ta haɗiye busashen yawin dake neman yanka mata maƙoshi. Cikin tsargawar zuciya ta furta, “Adeel! Nabeeha ya akai Adeel yasan gidanki? Miya kawo shi kuma?”.

Nabeeha ta share hawayen dake mata gudu. “Momy ban sani ba. Tare da wannan ƙanin Haysam ɗin suke Ammar. Kuma Haysam na nan dan yanzu haka a wajensa na baro shi. Wlhy Mammah ina son mijina, ina son rayuwar aurena. Idan na rabu da Haysam mutuwa zanyi. Ki taimakeni Momy, ki taimakeni kada Adeel ya lalata min aure na”.

“Ki kwantar da hankalinki. Zuwa anjima zan kiraki. Shima kuma zan samesa a masaukinsa kinji.”

“Mammah hankalina bazai taɓa kwanciya ba sai naga Adeel ya bar ƙasar nan na har abada”.

“Kar ki damu zai barta. Ki saurare ni”.

Ƙitt ta yanke kiran, Nabeeha ta zube ƙasa hawaye na cigaba da zuba mata. Wani makirin murmurshi Rayhana dake laɓe ta saki. Dan tabbas wannan shine babban makaminta a yanzu. Dan haka yanzu wasan zai fara......

□□□□□□
Received at 3:05 PM
[4/2, 10:40 PM] null: KIƊA A RUWA

........Dai-dai lokacin Nimrah ke shigowa falon goye da Naseer dake barci. Afrah biye da ita da ƙatuwar robar ice-cream a hannu. Itama Nimrah ɗin da ledoji a hannunta.

Da sauri Ruky ta nufi saman tana faɗin, “Kai bari nai sauri na dawo. Irin wannan kayan daɗi haka waya kawo mana?”.

“Kwaɗayayayyya ki kalla gabanki dai kar ki faɗi”. Cewar Nimrah tana harararta. Ruky bata kulata ba ta cigaba da haura staircase ɗin. Hankalinta kwance tai knocking ƙofar bedroom ɗin nasa. Ammar dake kwance daga shi sai shot da vest yana kallon Film a laptop a tunaninsa Mu'azz ne kai tsaye yace, “Come in”.

Kai tsaye Ruky ta tura ƙofar ta shiga abinta, dan hankalinta ma nakan ta koma wajen su Nimrah ne. Sallamarta ta saka Ammar ɗagowa da sauri. Yay bala'in waro idanu waje, gashi ya kasa tashi kamar wanda yay sumar zaune. Sumar ma irin ta tsuntsu daga sama gasashshe ɗin nan. Itama Ruky cak ta tsaya lokacin da take juyowa idannunta suka sauka a kansa. Kanta ta duƙar da sauri tana kif-kif da idanu. Dan Uncle's ɗinsu ko 3quarter na wando da wahalar gaske ka gansu da shi a falo balle shot da vest. Ganin hannunta na neman kifar masa da abinci baima san ya diro a gadon ya iso gabanta ba. Sai jin hucinsa tai a kusa da ita. Yana kama tray ɗin ta sakar masa zata gudu. Hannunta ya cafko kuwa da ɗayan hannunsa, ɗayan yana rungume da tray ɗin.

Da sauri ta furta, “Uncle Mammah na jirana”.

“Idan kin amsa min tambayoyina kenan”.

Ya bata amsa yana jan hannun nata. A haka suka isa gaban gadon nashi ya ajiye tray ɗin. Sosai Ruky ta rikice da mamakinsa da tsoro. Ai tana ganin ya saki hannun nata yana gyara tray ɗin tai hanyar ƙofa da sauri. Taku biyu ya iskota. Ƙafa ya saka mata. Dan haka ta tafi zata faɗi ya sake riƙota da hannunsa. Ruky tai tsirmai-tsirmai da idanu. Gaba ɗaya lamarin Ammar ya gama firgitata.

“Uncle kana lafiya kuwa?”.

“Da sauƙi dai kam Babie”.

“Babie”.

Ruky ta maimaita sunan tana waro idanu, sai dai ta kasa kallonsa, ga jikinta jini na gudu saboda yanda yake tsaye a kusa da ita sosai. Har kamar ma yana neman haɗe jikinsu sai da ta matsa baya. A mamakinta shima sai ya matso. Ta sake matsawa. Ya sake matsota har suka dangane da bango. Yanda ta maƙure lips ɗinta na rawa yaso bashi dariya. Ya dogara hannunsa da bango yana gyara tsaiwarsa...

“Uncle dan ALLAH kayi haƙuri idan laifi na maka”.

Yanda tai maganar murya na rawa ya sashi kai hannu kamar zai taɓa lips ɗin nata sai kuma ya tuna gargaɗin Dada. (Kar kaga na saka an ɗaura auren nan ka zata dami a kala ka samu Ammar. Kaje ka nema soyayyar yarinyata kafin tarewarku. Domin Bilal ma soyayyar Asma'u ya nema harta amince masa. Kaima na baka wannan damar dan in har baka samo zuciyarta ba sai wata shekarar zata tare ita kam......)

Fasawa yayi, ya ɗan haɗiyi yawu yana cije nashi lips ɗin. Cikin wayancewa ya furta, “Yaushe na zama abin wasan ki a gidan nan? Jiya kece mai faɗin aji tausayina a aura min budur-bazar ne ko miye ma kika ce maimaita?”.

Ɓoyayyar ajiyar zuciya ta sauke. Sai kuma tai ƴar dariya da tura baki. “Uncle to miye laifina anan. Bama godiya ya kamata kamun ba na damu da kai. Naga ne yanzu kowa yayi aure kai ko budurwa baka da ita....”

“Ke waya faɗa miki banda budurwa? Ina da ita mana”..

“Lah! Da gaske dan ALLAH Uncle?”.

Kai ya jinjina mata.
Ta ce, “Wooow dan ALLAH wacece?”.
“Gata nan a gaba na”.
Ya bata amsa kai tsaye. Tsabar rashin man kai sai ta fara waige-waige a zuciyarta tana tunanin to wacece? Sai kuma ta zubama laptop ɗinsa dake saman gado idanu. “Dan ALLAH ka nuna min hotonta ALLAH bazan faɗama kowa ba har Ninah.”

“Hummm haba Ruky ni zaki yaudara, ai ko rantsuwa kikai akan Ninah bazata ji ba nasan sai kin faɗa. Faɗa min miye budur-bazar?”.

Dariya ta ƙyalƙyale da ita, sai kuma ta ɗan tura lips da faɗin, “Shike nan tunda baka yarda ba. Uncle kai kamar ba bahaushe ba. Budur-bazar ne baka sani ba?”
Received at 4:41 PM
[4/1, 9:43 PM] Maman Nahnah□□□: “Naji ba bahaushe bane ni. Faɗa min?”.

“Sakin wawa fa ake nufi?”.

“ALLAH ya shiryeki miye sakin wawa kuma?”.

Tai dariyar da ke saka tsigar jikinsa tashi. Kanta tsaye ta ce, “Irin wadda ba'a daɗe da aure ɗin nan ba mana a sake su, sai kagansu kamar ƴan mata amma sun yaɓa aure”.

“Gaskiya kin raina ni. Ni sabuwa dal a leda garan. Sweet sixteen”.

Bakin ta ɗan tura masa da faɗin, “Uhmmm”.

“Dan ALLAH ki tausaya min ki bar tura min lips ɗin nan. Na rantse a matse nake”.

Da mamaki da ƴar rikicewa ta ce, “Na shiga uku Uncle kamar ya?”.

Maimakon bata amsa sai ya bar wajen. Kai tsaye inda jallabiyarsa take yaje ya ɗauka ya sanya dan kar taga gobarar data haɗa. Ita ko duk yanda take son basar da kalamansa sun fara sakata a ruɗani. Dan gaba ɗaya a yanda yake mata maganar ma yau salon na daban ne. Sum-sum ta nufi ƙofa, sai jin rufewarta Ammar yayi, ya zaburo zai yi magana ina harta gudu. Cikin dafe kai ya furta, “Ya ALLAH ka taimaki marayan ALLAH kar yay aika-aika a gaban Dada da Mammah”....

Ashe Ruky tana ruwa□□□.

«««««««»»»»»»»

“Ruky lafiyarki kuwa?”.

Nimrah ta faɗa cikin raɗa tana ƙara tsatstsare Ruƙayya da ido. Sashen da Mammah take Ruky ta ɗan saci kallo. Ganin hankalinta akan bama su Afrah abinci a baki yake ta kama hannun Nimrah kamar zasu yi wani abu a kitchen. Suna shiga ta leƙa ƙofar baya dan tabbatar da su Kulu basa kusa sannan ta dawo kusa da Nimrah.

“Ninah wlhy Uncle Ammar ne ya firgitani. Wai kinga yanda yake min magana kuwa.”

Sosai Nimrah ta waro idanunta da faɗin, “Ke kodai dan kina ruɗe ne”.

“Ba wani ruɗe wlhy. Sai kace wata ƴar ƙwaya..........”

Tsaf ta kwashe labari ta sanar mata. Nimrah akai zugum tana tuno Dada. Yayinda zuciyarta ke ayyana mata (To mike damun iyayen nasu? Ko itama Rukyn an ɗaura mata aure da Ammar ɗin......)

Zungurinta da Ruky tai ya sata kawo numfashi. “Wai tunanin mi kike yi?”.

“Uhmm Ruky anya kuwa kema ba'a ɗaura miki aure da Uncle Ammar ba? Ya kamata hankalinmu ya dawo jikinmu. A baya bamu gane abinda yasa Mammah ke saka mana dokokin rufe jiki da nasiha akan maza ba. Amma tunda abin nan ya faru na batun video ɗin nan nake ta nazari abubuwan da suka shuɗe a baya.....”

“Na shiga uku Nimrah aure kuma? Kada ki haukatani dan ALLAH. Wlhy kin fini ƙarfin zuciyar ɗaukar abu”.

Karo na farko Nimrah tai ƴar dariya da faɗin, “Kema ɗauka zakiyi yarinya. Ni wlhy yanzu ma na ƙara yarda bamu da hankali. Kammu baya gane komai. Inyeee kaga ta Uncle Auta. Har naji sanyi a raina tunda yanzu bani kaɗai bace”.

Harararta Ruky tayi idanunta na tara hawaye. Ta ce, “Dan ALLAH Ninah yi shiru. Wlhy zuciyata bugawa take. Kinga mu koma falo”.

“Miye na wani bugawar zuciya. Mammah tace sai ɗan gata akema irin wannan auren fa. Dan haka dalla malama manta da wani bugun zuciya mu ALLAH ya tabbatar haka ɗin ne ma. Muna kusa da Mammah ɗinmu, kuma muna tare na har abada. Dama ALLAH ya bamu na cigaba da jin daɗinmu da masoyiya Mammah har mutuwa.”

Murmurshi Ruky tayi itama. Dan harga ALLAH zukatansu na ƙaunar Mammah kamar yanda Nimrah ta faɗa....

Mammah najin motsin zasu fito tabar wajen tana murmurshi. Dan tunda suka taho ta biyosu, dan a yanda suka bar falon sai tai tunanin wani rashin jin zasu aikata. Dan tun jiya ta tsargu da yanda suke kallon su Afeef suna dariya. Tasan halin yaran nata ƴan ƙunar baƙin wake ne. Dama kuma ta tabbatar bazasu bar Afeef akan laifinsa ba. Haka kawai hirar tasu ta dinga bata dariya a zuciya. Dan ta fahimci autocinta sun fara hankali......

[×××][××××][×××]

WASHE GARI Litinin tushen aiki. Ƙarfe shida da rabi na safiya Bilal da Ammar masu fita aiki nata saurin zaman shan shayi da Mammah kan tsaresu shansa dole kafin su fita sautin takun da suke jiyowa daga stairscase ya saka su juyawa suna kallon wajen. Ba su kaɗai ba harda Mammah da su Kulu dake tsaftace falon. Isowar sirrintaccen ƙamshin turarensa ya tabbatar musu da mai gayya da aiki ne. Kafin ya bayyana a cikin idanunsu. Babu wanda bai ambaci Masha ALLAH ba a zuciya.
Received at 4:41 PM
reacted with ❤
[4/1, 9:43 PM] Maman Nahnah: Saboda yanda Dadan ya fito a jarumin jarumansa. Baya buƙatar kurantawa ko wasawa, ko maƙiyinsa ya gansa dole yaji eh lallai wankan ya wanku. Sosai Suit ɗin sun zauna masa a jiki tamkar kayan gadonsa.

“Anya yau ba Dadanmu za'a kalla matsayin shugaban ƙasa a fadar shugaban ƙasar ba”. Bilal ya faɗa da iya gaskiyarsa. Amshe masa Ammar yay da shima. “Yaya kamar ka shiga zuciyata ka karanto abinda ke cikinta.”

Dada daya ƙaraso kamar yasan gulmarsa suke ya zuba musu harara. Zamansu suka gyara kuwa kowa na haɗiye sauran gulmar a zuciyarsa. Mammah tai murmurshi, cikin kafesa da ido ta ce, “Kun haƙura dai kenan?”.

“To Mammah ya zamuyi kema kina bayan Janar”.

Nan ma murmurshin ta ƙara yi, dan jiya da dare ya shiga mata hira yake mata ƙorafin wannan aiki. Shine tai zama na musamman ta masa nasiha yanda ya kamata. Bai dai ce komai ba a jiyan, amma tasan dama bazai bijirema lallashinta ba. Ya sake gaisheta, suma su Bilal suka gaishe shi duk da sunyi a ɗazun da suka dawo salla. Mammah tasan bazai ci abinci ba a yanzu. Dan haka ta saka Kulu kawo masa zallar ruwan zafin da babu komai a cikinsa. Shi kuwa yasha, yana cikin sha ɗin ne Mu'azz ya fito dan shima zai wuce makaranta. Sai ga Biebah dake son shiga kitchen.

Duk gaishe sa sukayi. Ya amsa musu da kulawa. Dai-dai ya miƙe Bilal ke tambayar su Nimrah. Mu'azz ya ce, “Tab Uncle kaima kasan suna can suna barci. Tunda suka daina zuwa makaranta ai suka samu wannan lasisin. Yanzu haka sai su kai sha ɗaya a gado”.

“Mu'azz kaji tsoron ALLAH banda sharri. Suna kai dai tara amma ba sha ɗaya ba ”.

Biebah ta faɗa tana hararar sa. Mu'azz ya tura baki da faɗin, “To Small Mom miye marabar 9 da 11 ɗin?”.

“Awa biyu”.

Ta sake bashi amsa tana hararar tasa dai. Shi dai Dada baima nuna yana jinsu ba. Hasalima sallama yayma Mammah dake jera masa addu'oi sannan ya fice. Su Ammar na take masa baya..........✍

Received at 4:41 PM
[4/2, 10:40 PM] null: KIƊA A RUWA

.......Sun fito compound da Sanda ya gama sharewa tsaf, dan yana tsaka da banruwan fulawa ne ma ya hangosu ya ɓuya. Sai maigadi ne ya zo da sauri yana gaishe da Dada. Sannan suka gaisa dasu Ammar.

"Alhaji dama tun ɗazu baƙi suke jiranka."

Da mamaki Dada daya ɗan zuba masa ido ya furta, "Baƙi?".

"Eh wlhy suna wajen gate. Sai dai daga gani jami'an tsaro ne. Amma fa da wasu zuƙa-zuƙan motoci suke baƙaƙe wulik kamar na shigar shugaban ƙasa".

Dada baiyi magana ba, sai ma juyawa yay ya kalla Bilal. Bilal ya fahimci abinda yake nufi, dan haka ya miƙama Ammar briefcase ɗinsa ya nufi gate, sai kuma akai sa'a ma jami'an dake a gidan tun dawowarsa sai ga shugabansu ya shigo. Tare suka dawo inda Dadan yake da Bilal, yay gaisuwa. Kai kawai Dada ya jinjina masa.

Cikin ƙara gyara nutsuwarsa ya cigaba da faɗin, "Sir! Masu rakkiyarka ne daga fadar shubagaban ƙasa. Idan ka amince zan shigo da shugaban su".

Kallon juna Bilal da Ammar sukayi suka kashe ido da jinjina. Sai kuma suka gimtse murmushin fuskokinsu dan dai-dai nan Dada ya jinjinama jami'in kai. Da alama yau babu ƴan maganar a kusa. Da sauri kuwa Jam'in ya juya, dan ya gane yaren Boss ɗin. Babu jimawa suka dawo da wani mutumin dake sanye cikin baƙaƙen suit shima. Bazai wuce sa'an su Ja'afar ba. Sai da suka iso wajen yay gaisuwa irin ta girmamawa sannan yay bayanin dake tafe da shi.

"Ranka ya daɗe, bisa umarnin Shugaban Ƙasa, mun zo ɗaukar nauyin tsaronka da rakkiyarka zuwa Office."

Birkitattun idanunsa ya zubama jami'in, aiko bawan ALLAH babu shiri yay ƙasa da kansa. Zuciyarsa kuwa sai bugawa take da sauri-sauri. A ransa ya furta, (Tab wlhy bazan iya ba. Dama haka mutumin nan yake da cika waje. Ina wannan filin ba nawa bane dan zan iya tona kaina). A zahiri kuwa ya kasa ɗago kai ya kalla Dada a karo na biyu, shima kuma baiyi magana ba ya nufi gate abinsa. Da sauri su Ammar suka bisa kuwa, dole suma suka take musu baya.

Tabbas maigadi baiyi ƙarya ba. Zuƙa-zuƙan motoci ne da ko wanda bai san mota ba yasan an saye su da kuɗaɗe masu nauyin gaske. Ga wasu baradan jaruman tsaye masu jiran kota kwana. Suna fitowa duk suka sake nutsuwa, sai kuma sukai caaa suna miƙa gaisuwa. Hannu kawai ya ɗaga musu..

Wanda ya masa bayani a cikin gidan nan ne dai ya buɗe masa motar tsakkiya da saurinsa. Dada yay ɗan jimm yana karanta addu'ar hawa abin hawa kamar yanda ya saba koda tashi ce sannan ya shiga ya zauna. Jami'in ya maida ya rufe. Sannan ya zagaya gaba ya zauna ta gefen mai zaman banza, cikin waɗancan kuma wani ya buɗe mazaunin driver ya shiga. Matsowa su Bilal sukai suka masa bye, ya jinjina musu kai yana lumshe idanunsa.

Suma sauran jami'an duk sun shiga sauran motoci biyun. Daga haka suka harba kan titi. Kasa haƙuri su Ammar sukai sai da suka koma cikin gidan kaima su Mammah rahoto. Dan Ammar ma harda video ya ɗauka dama. Kuma ya ƙudiri aniyar ɗorashi a media dan zukatan maƙiya su buga.....

^^^^^^^^^^^^^

A ɓangaren Daddy Imran ma hakan ce ta faru. Yayi shirinsa tsaf cikin Suit masu duhu Ammie tai masa rakkiya compound da shirin shiga motarsa, Asma'u dake riƙe da briefcase ɗinsa na roƙonsa bin Ammie kasuwa dan za'ai sunan Aunty Lailah gobe, shi kuma yace a'a tanata shagwaɓa. Gefe Khalifa na mata dariya, Lolo kuwa na ɗakinsa yana shirin makaranta. Isowar mai wankinsu ya katse faɗan Khalifa da Asma'u. Ya gaishesu sannan yake sanar muku baƙin dake gate.

Mamaki ya kama Daddy Imran sosai, amma sai yace maiwanki ya shigo da Ogansu yaji lafiya. Saɓanin na Dada shi nashi sojoji ne, duk da dai a wanda ke waje

akwai wasu jami'an harda ɓoyayyu ma. Yanda akaima Dada bayani anan shima haka akai masa. Yasan hakan normal ne dama, amma yayi tunanin sai sun fara zuwa office a yau sannan za'a basu waɗan nan damammakin. Dole yay sallama da iyalinsa yana sake jaddadama Asma'u karta fita ko'ina. Daga haka aka buɗe masa mota suka wuce fadar shugaban ƙasa.

)))))))★(((((((

Received at 4:41 PM

[4/1, 9:43 PM] Maman Nahnah: Tsakanin isowar motocin Dada dana Daddy Imran babu nisa. Sai dai da yake a faɗar shugaban ƙasar ma kowa da fanninsa sai basu haɗu ba. Kai tsaye motocin ɗaukar Dada sun nufi sashen ofishin shugaban ƙasa ne. Wani babban jami’i Chief of Protocol ya tarbe shi. Dan motocin na kammala tsayawa jam'in nan yay wuff ya fita a gaban mota kamar sauran suma yazo ya buɗe sashen da Dadan yake. Sai da yaja fin mintuna biyu, dan sai da ya karanta addu'oi sosai tare da ƙarema wajen kallo sannan ya sauke ƙafarsa ta dama dake sanye cikin haɗaɗɗen takalminsa. A take ƙamshin turarensa ya isa hancinansu, duk da suma ƙamshin nasu turarrukan sun shiga nashi hancin.

Cike da girmamawa Chief of Protocol ya miƙa gaisuwa. Tare da faɗin, “Ranka ya daɗe Sir. Shugaban Ƙasa ya bayar da umarnin a raka ka kai tsaye ofishin ka.”

Kai kawai ya jinjina masa kamar na baya, dan tun maganarsa da Mammah a gida bai sake magana da kowa ba. Wannan kuma salon takun manya ne. Jami'an da suka ɗakkosa har yanzu basu ji muryarsa ba, dan haka suka fara tunanin wai kodai bebe ne mutumin nan?. Babu mai basu amsa dan haka sukai gum, saboda kwarjininsa kawai da cikar kamala da kamewarsa ga nutsuwa da gizago ya sakasu jin shakkarsa, tare da yarda da batutuwan mutane a kansa. Dan a weekend ɗin nan babu sunan daya kai sunan sa dana Imran yawo sai na shugaban ƙasa.

Yanda Chief of Protocol ke gaba, sai jam'in nan dake nuna shine shugaban wannan tawagar a tare da shi, Dada na bayansu, bayansa kuma sauran jami'an nan ne ke take masa baya dole abin ya birgeka. Dan kamar an tsara su ne, suna sauke ƙafa da ajiyeta a tare kaida ka gani kasan rakkiyar ta babban kai ce. Gashi suna tafiya ne ta cikin dogon corridor mai sanyi, shirun da babu hayaniya. Tun fitowarsa motar ƴan median fadar ta shugaban ƙasa suka dasa musu camara kuma. Dan dole ne a saki labaran shigowar Chief Of Staff na farko office ga ƴan ƙasa.

Ko'a jikin gogan naku. Takunsa yake cike da ƙasaita da mazantaka. Fuskar nan ciɗin-ciɗin yau ta asalin sojan sa a fagen yaƙi. Ga hotunan tsoffin shugabanni da suka cika bangon dogon corridor ɗin suna kallonsa kamar suna tantance shi da masa barhaban. A ƙarshe aka tsaya a gaban wata ƙofa dake ɗauke da baƙin allon rubutu da kalar gold.

CHIEF OF STAFF TO THE PRESIDENT.

Shine a rubuce ɓaro-ɓaro ga mai kallo. Chief of Protocol ya danna wani maɓalli dake a bango a take ƙofar ta raba kanta biyu. Makeken Ofishin mai girman gaske ya bayyana a idanunsu. A tsaftace yake, ga ƙamshi na tashi mai ainahin saka nutsuwa. Matuƙar tsaruwa wannan office ya tsaru. Dan kuwa komai na cikinsa yana tabbatar da ƙarfin ikon mamallakinsa .

Dada ya tsaya na ɗan lokaci yana karanta addu'oi. Kafin ya saka ƙafarsa ta dama batare da ya daina ambaton ALLAH ba. Dan shine cikakken sarki gagara misalin masu misali. Mai cikakken iko da rahama ga jinƙai ga bayinsa. Shike bada dama ga wanda yaso a sanda yaso. Shike daka girma da cikar kamalar bawa a idanun ƴan uwansa bayi badan ya kasance mafifici a garesu ba. Ba'a farautar ɗaukaka ko girma da kuɗi ko ƙarfin ƙwanji. UBANGIJI ne kawai ke badawa kamar yanda ya bama wannan bawan nasa Haysam Abdul-rasheed Shehu Kobi.

A hankali ya kai zaune cikin kujerar da aka gyara masa idanunsa a lumshe bakinsa na cigaba da ambaton UBANGIJI da neman agajinsa. Dan tabbas yanzu ne wasan zai fara. Farawa irin ta KARE JINI. BIRI JINI. A yanzu yaƙine na kwatar ƴanci da neman tsira. Kuma duk zasu fara ne ta silar wannan kujera....

★A can ma Daddy Imran ya shiga nasa babban ofishin dake da ƙarfin faɗa aji akan tsaron ƙasa. Shima dai an shirya shi da girma da aji tamkar na Dadan. Dan tsarin da akaima offices ɗin duk mai hankali ya tabbatar da gayya shugaban ƙasa yasa akayi su. Ga tsaro mai tsaurin gaske dake tabbatar ma maƙiya koda zasu iya keta wannan alfarmar sai da ƙarfin ikon ALLAH. Sannan The two shadows sun iso FILIN YAƘIN. Yanzu ne za'a banbance MAZAJE DA MAZARE......

============
Received at 4:41 PM
[4/2, 10:41 PM] null: 28

........Sosai zuciyar Nabeeha ke tafasa da bayanin Amima. Sai dai batace komai ba har Amima ɗin ta kai ƙarshe. Sai kuma ta ɗora da faɗin, “Aunty wannan dama ce a gareki da zaki je ki tambayesa zuwa gidan Aunty Jiddah. Kinga sai mu tafi yanzu ko anjima ko? Dan gara muyi abinda ya dace da wuri. Na kira Aunty Ismat ma tace anjima kaɗan zata zo”.

Ajiyar zuciya Nabeeha ta sauke tana shanye damuwarta ta ce, “Kuma fa haka ne Amima. Bari kiga na ɗan gyara fuskata to. Ita kuma ALLAH ya kawo ta”.

“Aunty ai ba gyara fuska ma kawai ba, bari na saka Nana ta dafa shayi ki tafi masa da shi, irin kamar abinda kika kawo masa dama kenan. Ko lemo za'a haɗa da ruwa?”.

“A'a a dafa shayin, dan nasan shi da son shayin zai fi son sa. Haysam baya shan kayan zaƙin nan kin manta”.

“Af haka ne fa. Yauwa to shirya, bari naje itama na sakata dafa shayin, sai kin fito. Amma dan ALLAH kiyi ƙyau sosai”.

Dariyar yaƙe tai mata. Itama ta fice tana murmushi. Rayhana dake ƙofar tsaye yabar wajen tana dariya. Dan harta gama kitsama kanta abinda zatayi yanzun nan. Ai tayi ma kanta alƙawarin bazata taɓa bari Nabeeha ta shirya da Haysam ba.......

÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷÷

Su Mammah na falo Nimrah ta wuce ta shiga kitchen. Babu wanda yay magana sai Aunty Mimi data miƙe tabi bayanta. Ta sameta tana wanke tukunya, dan haka ta jefa mata tambaya.

“Ninah mi zakiyi?”.

Cikin ɗan tura baki ta ce, “Momy Dada yace na dafa masa Coffee”.

(Anzo wajen) Cewar Mimi a zuciya. A zahiri kam sai tai murmushi da matsowa inda take tana faɗin, “Okay zubo ruwan kizo kiga wani wani abu to”.

Babu musu Nimrah ta amsa mata. Kafin ta ƙarasa inda take. Da taimakon Aunty Mimi aka dafa Coffee ɗin aka kuma dafa shayi mai shegen daɗi, kowanne aka zuba shi a inda ya dace sannan ta sakata ta shirya a kwando mai ƙyau kai kace wajen gidan za'a fita da shi, harda ɗan abin taɓawa na snacks da aka gasa, dan Dada baya cin soyayyen abu ko miye. Hatta doya ko dankali in har zai ci sai dai a gasa. Kuma ba koda yaushe ma yake cin ba, dan abincinsa nada tsari da ƙa'idar gina jikin ƙarfi da lafiya..

Abinda yasa Nimrah ta riga Nabeeha fitowa duk da kayanta sunfi yawa acan mai aiki sukari ta zabga a shayin. Nabeeha na ɗan ɗanawa dan taji ko yayi daɗi taji sukarin zau. Ai ko sai da Nana tasha mari a hannunta tana masifa. Dan Dada baya shan sugar kwata-kwata ma shi. Ko zuma sai lokaci-lokaci ba kullum bane. Ko maggi duk yawan abincinsa zakaga baya wuce ɗaya jal a ciki, balle su gishiri ƴan ƙarshen layi.

Nana na kuka tana bata haƙuri da faɗin, “Aunty wlhy ban sani bane da bazan saka ba. Dan ALLAH kiyi haƙuri, kuma wlhy kaɗan ma na saka ban san yaya akai ya haura haka sama sosai ba”.

Harara Nabeeha ta zabga mata da faɗin, “Dalla naji wanke tukunyar ki sake haɗa wani bana son surutun banza wawuya kawai baƙauya. Banda ƙauyanci uwarki tace kisa sugan baki tambaya ba”.

Jiki na rawa Nana ta fara yin yanda tace, sai dai a zuciyarta duk zagin da Nabeeha tai mata sai da ta rama. Tama ƙara mata da wasu da sukafi nata. amma a zahiri tana mamakin yanda akai sugan yayi yawa ɗin dai. Dan tasan kaɗan ta zuba, kuma babu wanda ya shigo kitchen ɗin sai Rayhana. Hakan na nufin ita ta ƙara sugan kenan?. Bata da mai bata amsa, dan haka ta cigaba da aikin dan Nabeeha ta fice falo. Maimakon ita ta amsa ta dafa ɗin dan rashin dabara..

Duk da Rayhana taji haushin haƙarta bata cimma ruwa ba sai ta share, acewarta ai yanzu aka fara wasan...

Dada na zaune a rumfar yana aikinsa hankali kwance lokaci-lokaci ana kiran wayarsa ko shi ya kira ya hango Nimrah na nufo shi cikin tafiya salaf-salaf kamar kazar da ƙwai ya fashe ma a ciki. Su Ruƙayya sun bar compound ɗin tun ɗazun suka shige sashen su Lailah. Daga su maigadi a gate koma muce maigadi kawai, dan tunda Dada ya fito Sanda yay wuff ya shige ɗaki bai sake fitowa ba. Malam Buba kuma kwana biyu baya nan, yace musu tafiya ce ta kamashi matarsa babu lafiya, dan su ya sakama su isar da saƙon gasu Mammah a shekaran jiya da safe.

Received at 3:05 PMReactions:Dan haka babu wanda ya sake bi ta kansa duk da Mammah ta ba maigadi kuɗi ya tura masa ya ƙara ya kula da matarsa. Nimrah na zaune akai hakan, sai ta dinga sauke ajiyar zuciya dan ta fahimci dai Baba Driver maybe ya gudu ne, har komai ya lafa sannan ya dawo. Shi kuma sai yanzu ma yake ji a bakin Mammah daya fito ɗin nan.....

“Assalamu alaikum”.

Sallamar Nimrah ta saka Dada ɗan ɗagowa tunaninsa na katsewa, kallo ɗaya ya mata ya maida kansa ga wayarsa, sai kuma ya kaita kunnensa yana faɗin, “Dabo kana jina?”.

Bata san mi akace daga can ba, ya dai cigaba da faɗin, “Ku tabbatar dukansu sunzo hannunku da rai, koda ta kama zakuyi harbi kar ya wuce ƙafa, hannu ko cinya ba inda za'a mutu ba”.

Yanda gaban Nimrah ya faɗi sai da ta ɗago ta kallesa. Suna haɗa ido tai saurin maida nata ta risinar. Shima daga haka ya ajiye wayar, sai kuma ya kalla basket ɗin data buɗe. Ganin kaya sosai daya wuce abinda ya buƙata ya furta, “Ni da nace Coffee, miye da miye haka duk kika haɗo?”.

Yanayin da take ciki ta haɗiye, fuskarta da ɗan murmurshi ta masa bayani tana nuna masa komai. Sai ya murmusa da faɗin, “Okay to bani shayin, anjima nasha coffee ɗin”.

Jitai ranta ya mata sanyi bai kusheta ba, dama abinda take ta tsoro kenan. Ga shi yama bar abinda yake so yace ta bashi wanda ta kawo batare da yasan da shi ba. Sai taji hakan girmamawa ce yayi a gareta. Dai-dai ta gama zuba shayin ta ɗago zata ajiye masa Nabeeha ta iso wajen. Sallamarta ta saka shi da Nimrah ɗin ɗagowa suna kallonta. Ƙaramar harara ta zuba ma Nimrah.

Babu ragi itama Nimrah sai ta taɓe baki tana yamutsa fuska ta ɗauke kanta kamar taga wata bola. Nabeeha da abin ya mata zafi wai ƙaramar yarinya ƴar cikinta na mata wannan iskancin ta haɗiye yawun takaicin ta saboda tuna shawarar Amima. Kanta ta maida ga Dada tana sakin murmushin danne abinda ke taso mata kamar yanda Amima ta bata shawara.

“D. Barka da yamma”.

Ta faɗa a hankali.

“Uhmmm”.

Ya amsa mata a taƙaice. Duk da bataji daɗi ba sai ta danne, dan ta fahimci ita mai laifice a garesa, ta buɗe baki zata sake magana motar Imran ta shigo gidan. A kuma dai-dai lokacin Ammar da Adeel suma suke shigowa da ƙafa. Dan tun ɗazun Ammar na tare da su Adeel ɗin kasancewar yanzu sun gama janye ra'ayinsa har estate ɗin su yana shiga musamman weekend, sannan suna fita yawo jefi-jefi. Nan gidan ne dai Adeel bai taɓa zuwa ba sai yau Ammar ya matsa masa da ƙyar akan sai fa ya shigo ya gaida Mammah. Shine fa ya biyoshi suka shigo. Hango Dada kuma ya sashi jan hannun Adeel ɗin. "Ga Dada ma na gida. Muje ka gaida shi, shima Yaya Imran gashi yazo".

Haka kawai Adeel da yayma sashen Dada kallo guda yaji shakkar kamilallen mutumin da kwarjininsa ke cika ido tun daga nesa. Ya ɗan shafa gashin fuskarsa da faɗin, "Abiy ɗinku ne?".

"Eh matsayinsa kenan a garemu. Amma shine babban yayanmu gaba ɗaya. ALLAH yayima Abiy rasuwa tun ina watanni baifi huɗu ba".

Sosai Adeel ya zaro idanun. Sai kuma tausayin Ammar ya bayyana a fuskarsa sosai. Ammar yay murmurshi da faɗin, "Manta kawai. Muje kaji".

Addu'a Adeel yay ya neman gafara ga Abiy. Sannan yay ya ta'azziya ga Ammar. Ammar ya amsa masa da Amin yana godiya. Sannan suka nufi inda Dadan yake da matansa biyu da suka saka shi tsakkiya. Wanda Adeel baiga fuskokinsu ba kasancewar sun juyama ta inda suke baya ne.

Isowarsu dai-dai da juyowar Nabeeha da Nimrah dake amsa sallamar Daddy Imran da shima ya iso wajen. Sai ko idon Nabeeha akan Adeel, da shima kamar ance ya kalletan nashi suka sauka a cikin natan. Wata irin girgizawa ƙirjinta yayi, zuciyarta ta buga tamkar zata tarwatse. Duhu ya mamaye ganinta, kunnenta yay irin dummmm ɗin nan kamar an daki ƙarfe a cikinsu. Ai bata ma san ta saki butar shayin hannunta ƙasa ba tsabar yanda illahirin hankalinta yay mugun nisa da gangar jikinta da numfashinta gaba ɗaya..........✍

Ga Dada, ga Adeel, ga Nimrah, ga Nabeeha. Wai wai daɗi kan daɗi, wai majina akan tuwon mashara□□😂□.

Received at 3:05 PMReactions:Wannan fa shi ake kira ƙaƙa ƙara ƙaƙa. Ga akuya ga kura. Boni ya cimu, Dada ya haɗu da ɗan larabawa mai masa farautar mata. Wa yaga kaddara ko ganganci?😂.

Received at 3:05 PM

reacted with □

[4/1, 12:35 PM] null: KIƊA A RUWA 3

29

.........Gaba ɗaya kallonsu ya dawo kan Nabeeha da jikinta ke tsuma. Ga butar shayi da shayi tarwatse a ƙasa. Ganin inda take kallo ya saka su sake maida kallonsu wajen. Sai dai banda Dada da tunda yay mata kallo ɗaya ya ɗauke idanunsa kamar bai san abinda ake ba. Cirko-cirko kowa ya sake yi ganin Adeel da Nabeeha ke kallo, yayinda shi kuma Adeel ke kallon Nimrah a yanzu. Wata banzar harara Nimrah ta zabga masa ganin ita yake kallo, ranta a ɓace ta kauda kai ta maida hankalinta ga Dada tana faɗin, "Dada a saka suga?".

Kai ya girgiza mata, sai kuma ya sake kallon Adeel da yake kallonta ta gefen ido. Ganin idanunsa akan Nimrah ne yanzu ya sake tsuke fuska. Cikin farga Ammar ya taɓa Adeel, ya ɗanyi firgigit alamar dawowa hayyaci yana sauke ajiyar zuciya. Imran dake nazartar kallon da Nabeeha kema Adeel shima yay gyaran murya. Kamar wadda ta dawo a suma taja numfashi ta fesar, sai kuma ta fara kame-kamen kaiwa duƙe tana tattara butar shayin data fashe hannunta na rawa.

A zahiri zaka rantse Dada bai ga abinda ke faruwa tsakanin Nabeeha da Adeel ba, amma yafi kowa fahimta da nazartar komai a wajen. Dan Nabeeha na haɗa kwalaben

waje guda tana ɗagowa ta saci kallon Adeel ta saci kallon Dadan, wani kallo da ya watsa mata sai da taji kamar zata saki fitsari a wajen, sai rawar jikinta ta nema ƙaruwa.

Daddy Imran yakai zaune Nimrah na gaishe sa fuskarta da murmushin murnar ganinsa. Shi kuma Ammar ya jawo hannun Adeel suma suka shigo cikin rumfar sosai yana faɗin, “Dada. Yaya Imran ga abokina Adeel zai gaishe ku”.

Murmushi Imran yayi yana nuna musu sauran kujerun biyu da suka rage. Ammar ya zauna a kusa data Dada, shi kuma Adeel kusa da Imran. Sai ya zama Adeel na facing Dada, Ammar na facing Imran. Kasancewar kofuna biyu ne kawai Nimrah ta zubama Daddy Imran shayi shima. Ta kalla Ammar cikin ƴar shagwaɓa ta ce, “Uncle kaima fa yanzu sai kace sai kunsha ko?”.

Ammar ya ɗan harareta da faɗin, “Ninah bana son harkar rowa. Miye na kandagarkin to?”.

Baki ta tura da faɗin, “To Uncle da wahala ne zuwa kitchen na dawo.”

Ammar yay dariya, zata sake magana Dada da yakai ƙarshen ƙulewa da shagwaɓar da take ma Ammar ga Adeel daya tsaya masa a wuya cikin kaushin murya ya furta, “Kiddo bar wajen nan”.

A yanda yay maganar bama ita kaɗai ba harta Ammar nutsuwa yayi. Imran yay guntun murmushi. Adeel kam jiyay zuciyarsa na girgiza. Dan har tsakiyar rai yaji fitar sautin golden voice ɗin Dada dake fita da ainahin gizagon mazan da basu san kalmar wasa ba. Ya haɗiye yawu da ƙyar yana kallon Nabeeha dake kallonsa cikin roƙo da magiya. Dan ita tashin hankalin da take ciki ma yafi na kowa. Dada daya ƙara ƙuluwa duk da ita Nimrah harta tafi ya watsama Nabeeha kallon gargaɗi itama. Ita kam ko kallo yay tana gane abinda yake nufi ba Nimrah da sai ya furta ba. Da sauri ta bar wajen jikinta na rawa zuciyarta na tsitstsinkewa. Tambayar kanta take, “Ya akai Adeel yasan gidan nan? A ina suka san juna da Ammar? Mi yazo yi gidan?”. Bata da mai bata wannan amsar, babban burinta kawai takai kanta sashensa ta kira Momy a waya......

>>>>>%<<<<<

A ɓangaren ƙungiyar duhu basu samu zama ba sai a yau a wannan yammaci na Lahadi. An samu tsaikon zaman ne sakamakon Oga Jush baya ƙasar da wasu jigajigan tafiyar. Sai a yau suka gama hallaruwa gaba ɗaya. Dan haka ko zaman hutawa basuyi ba akai zaman meeting na gaggawa.

Kamar yanda suka saba. A meeting room ɗinsu suke mai zurfi da duhu duk da rana ce kuwa, amma fitila guda ɗaya ce ke haskawa an rufe windows an saki labule. Baka jin komai sai sautin bugawar zukatansu dake tabbatar da ɓacin ransu a bayyane. Wasun su sai zufa suke dan yau ko ac basu kunna ba tabbacin tashin hankalin da suke ciki.

Oga Jush, da fuskarsa tafi ta kullum zama kalar firgici cikin umarni ya furta, “Ina buƙatar son jin sanarwar da kunnena”.

Received at 3:05 Raven ya ɗauka wayarsa, kai tsaye ya shiga intanet ya samo videon dake ta yawo har zuwa yau tamkar wutar jeji saboda yanda bakunan ƴan siyasa yaƙi rufuwa daga cecekucen.

“…Mr. Haysam Abdul-Rasheed Shehu Kobi is appointed as Chief of Staff to the President. & Mr. Imran Abbas is appointed as National Security Advisor…”

Ɗakin yay shiru. Kowa yana jiran cewar Oga, amma yaƙi ya tanka sai da ya mula dan kansa sannan ya furta. “Ministoci nawa ne damu a ciki?”.

Kai tsaye Mr Specter dake a tsorace tunda yasan shine ya kawo Janar ɗin ya furta, “Biyar a cikinsu duk namu ne. A wanda za'a sake badawa ma mune mafi rinjaye”.

Batare da Oga Jush ya kallesa ba ya bashi amsa da, “Suma sauran duk su zama namu. A shirya vice president zai koma president nan da ƙarshen wannan shekarar”.

Babu wanda bai girgiza ba, duk da su dukansu basu san kalmar tausayi ba. Amma furicin Oga na nufin ɗayan biyu ne. Kodai za'a kwantar da Janar yana raye komai sai an masa kamar na baya, ko za'a binne shi cikin ƙasa matsayin gawa. Sai dai babu damar yin koda musu. Amma a wannan gaɓar akwai masu alaƙa da Janar tun kafin wannan ƙungiya, akwai kuma irin su Garba da suka afka kansu ciki duk da suna gidan soja a zahiri.

Cikin ɗacin murya Viper ya furta, “Su kuma waɗan ƘAYAR KIFIN fa? Ya haɗa su biyu fa a mafi girman muƙamai.”

Cikin fushi Mr Scythe ya amshe zancen kafin Oga ya amsa ma Viper ɗin. “Viper wannan ba siyasa bane ai. Yaƙi ne tsakanin masarautu guda biyu. Dole kuma sarki ɗaya ne zai rayu. Kuma mune”.

Black Spider ya ce, “Tabbas maganarka gaskiya ce Mr Scythe. Zak-Shadow bai fito fili ba sai da izini. Kuma idan ya fito... yana nufin an riga an shirya wani abu. Hakan na nufin a yanzu bama buƙatar hargowa ko fito-na-fito da shi. Yaƙin sunƙuru za'a fara. Ta hakane za'a banbance SARKIN da zai karɓi wannan KUKERAR IKON a tsakanin mu da shi”.

Karo na farko Mr Specter ya furta, “Ai ni ban taɓa ji da ganin abinda ya girgizani ba irin wannan. A lokacin da naji ji na dinga yi kamar sunan aljanu aka ambata. NSA da COS... inuwa biyu a kusa da shugaban ƙasa. Ni Yusuf Tafida zai ma haka?”.

Kafaɗarsa Iron Fang ya dafa, cike da son kwantar da hankali ya furta, “Karka wani damu kanka, ya kawo kansa ramin Damisa ne ai bai sani ba. Mu ma kuma a yanzu dole ne mu sake lura. Saboda idan mun kusanci Tafida, zasu ji. Idan mun matsi Zak-Shadow, zamu ji.”

Ƙaramin tsaki Oga Jush yaja. Cike da takaici da zafin furuci ya furta, “Ku daina kallon mukami. Ku kalli abin da yake ɓoye a bayansa.” Ya ɗan tsaya yana jan numfashi, kafin ya cigaba da murya mai zafi, “Wannan naɗin ya tabbatar mana da abu guda... Tafida ya san muna nan.”

A take meeting room ɗin ya sake zama tsitt. Wasu suka gyara zama. Raven yay ƙarfin halin faɗin, “Tabbas Oga maganarka nakan hanya, dan wannan abun da yayi tamkar yana son nuna shi KIDA A RUWA ne MAI SON TADA HANKALIN DODO. TO menene mataki na gaba?”.

Kai tsaye Oga Jush ya amsa da, “Mu bar su su ji daɗin watan farko na sabon office. Litinin ɗin sabon wata... zamu fara gwada ƙarfin inuwa.”

Jikake raf! Raf! Tafi ya karaɗe ɗakin. Wasu na murmusawa a duhu. Cike da shaƙiyanci Black Spider ya fusta, “The two shadows?”.

Viper ya amsa masa da, “A’a... Yanzu sun zama targets.”

A tare suka fashe da dariya irin ta mugunta da mugun ƙudiri......

<<••••••>><<••••••>>

Kai da kaga yanda Adeel ke mutsu-mutsu a wajen zaka san a takure yake. Ga Dada ya haɗe gabas da yamma ko gaisuwa a daƙile ya amsata. Daga nan ya cigaba da aikin gabansa kai kace yama manta da su a wajen. Sai Daddy Imran ne ke hira da Ammar.

Tabbas a wannan gaɓar Adeel jinsa yake ba komai ba. Babu sarauta babu gadara babu fariyya irin ta jininsa. Yo ashe ma idan kaga shege na gwada shegantaka ga wani jinsin mutane irinsa sai a inda yake da ƙarfi da faɗa aji. Dan akwai a inda idan ya aikata ubansa zaici koda kuwa ace a zahiri ya mallaki duniya da dama data wanda yake ganin kaskantattu sai shine mafifici.
Received at 3:05A cikin mintuna ƙalilan ya fahimci dalilin da ya saka bazai taɓa iya burge mace irin Nabeeha dake fifita soyayya sama da kuɗi ba. Wanda keda wannan tsayayyen jarumin namijin a shi idan ka cire dukiya, kyan fuska da gidan mulki mike gareshi? Sufa irin waɗan nan mazan badan ƙyawu, dukiya ko wani matsayin duniya ake son su ba. UBANGIJI ya gama mallaka musu abinda ba waɗancan abubuwan ba, ko su maza irinsu da suka mallaka sai sun risina musu da jinjinar ban girma. Ya

sallama baida abokin faɗa anan, amma zai wajiga rayuwar Nabeeha da Uwarta, dan dole ne suyi aman abinda suka ci nasa. Abu na gaba kwantar da kai, tabbas zai yi biyayya kuma anan ɗin dai domin samun ɗaya tilon sa Nimrah. Dan ya fahimci Nimrah ɗiyar mijin Nabeeha ce kenan. Maybe ma UBANGIJI ya jarabcesa da Nabeeha ɗin ne dan ya kawosa ga Nimrah, ba kuma zai yi sakaci da wannan damar ba. Ko zuri'arsa naso ko basa so, ko zasu sallamashi ma duniya sai ya mallaki Nimrah. Dan zai iya faɗa da kowa akanta, duk tsanani kuma bazai iya sallamawa ba koda a numfashinsa na ƙarshe ne. A yanzu haka yana shirin saye estate ɗin su Yohan ne gaba ɗaya, dan kasuwanci ma yake shirin kafawa a ƙasar saboda yanda yake jin daɗin zama cikinta, wasa ɗan gaske ya shirya yi akan Abu biyu. Nimrah da Hajiya Hasiba da ƴarta Nabeeha koda yaƙin zai ci ƙasar.........✍

Hhhhhh anayi muna shan shayi, to Adeel bari muga ko wasan naka zai zama abin kallo a gare mu. Ƙasar dai idan bata tashi dan kai ba, to zata tashi da kai a ciki kuwa🤦🏻‍♀.
Received at 3:05 PM
[4/1, 12:35 PM] null: KIƊA A RUWA 3

30

...........“Malam duk kabi ka rikita yaro da wannan kallon naka sai tsuma yake kamar mai tsutsar basir. ALLAH kai mugu ne”.

Hararar Daddy Imran Dada yayi, tare da faɗin, “Kai ai duk duniya ba wanda ka raina sama dani. Ni ubansa ne da zai yi tsumar jiki a kaina? Tunda ni mugu ne kai ne na'ibina ai”.

Dariya Imran ya shiga tuntsurawa. “ALLAH Serious a rikice yake. Ko Ammar ya sha jinin jikinsa ne shiyyasa yace suje.”

“Su suka sani, amma tun wuri ka dakatar da shi zuwa gidan nan inba haka ba kuma huumm.....”

“A'a yi haƙuri mu gara ka barshi yazo mu samu abinda muke so. Amma fa yanda Nabeeha ta razana yafi komai ɗaure mun kai, shima yanda yake kallonta kamar sun san juna.”

Dada dake kallonsa ya ɗan ciza lips. Ga hannunsa ya dunƙule alamar fushi. Imran daya fahimci halin da yake ciki ya sauke numfashi da faɗin, “Relax! Zak... Mubi komai a sannu, in sha ALLAHU zan sabunta bincike akansa. Dan tabbas ina ji a jikina ba business ya kawo shi ƙasar nan ba kawai.”

Idanu Dada ya lumshe tare da buɗesu a lokaci guda. Cikin ture zancen ya ce, “Ya ake ciki da yaran nan?”.

Shima Daddy Imran sakin zancen yay kawai. Sai kuma ya miƙa masa takardu da ya ajiye gefensa. “Komai ya kammala. ALLAH ma yaso naje yau ɗin da an samu matsala. Dan gobe zasu rufe registration ɗin.”

“Dama Auta ta faɗa ai. Yanzu dai tunda anyi Alhamdullah. Yaushe zasu fara exams ɗin?.”

“Babu wani nisa nan da sati biyu ne”.

“ALLAH yasa muna da rabon kaiwa. Haydar ya kira ka ne?”.

“Humm kaga zan manta ba. Ya kirani yana sanar min kamar sun gano inda drivers ɗin nan suke fa, kuma suna zargin wanda muka sani ne Ogan su, bai wuce kuma Ojo ba. Sai dai basu tabbatar ba, gadai jami'an farin kaya zasu fita operation tare da Dabo”.

“Ni bana jin wani shakkun shine.”

“Kayi aiki a ɓoye kenan?”.

Murmurshi mai faɗi Dada ya saki amma bai ce komai ba. Imran dake murmurshin shima da jinjina kai ya ce, “Aljanancin ka na bani tsoro Haysam.”

Dada bai ce komai ba nan ma. Dan haka Imran ya sake faɗin, “Malam Buba ya dawo ne?”.

Kai Dada ya girgiza masa alamar a'a.

"Kenan ta tabbata mutumin nan munafuki ne? Yanzu ta ina zamu fara?".

"Karka damu, zasu zo hannu cikin sauƙi. Yanzu haka akwai jami'an da nake son ya kasance kan aikin."

"Hakan yayi, sai office. Kasan dai ba fashi dole gobe idan ALLAH ya kaimu mu fara shiga".

"Humm wato Janar ko....?".

Dariya Imran ya sanya. "To ya muka iya, ya riga ya ɗaure mu, kuma tsarin yayi. ALLAH ya ɗora nasararmu akan tasu kawai...."

"Amin ya rabbi to"....

□□□□□□

"Momy wlhy na shiga uku....."

"Kamar ya kin shiga uku Nabeeha? Ba sallama ba gaisuwa sai zance shiga uku. Nifa matsalata dake rashin hankali".

"Momy dole nake faɗar haka, Adeel ne fa a gidana....."

Wani kalar rikitowa Hajiya Hasiba tai daga samon gadonta. Sai kuma ta kalla First Lady dake kallonta dan suna tare ne a saman gadon. Ɗauke kai First Lady ɗin tayi, itama Hajiya Hasiba sai ta haɗiye busashen yawin dake neman yanka mata maƙoshi. Cikin tsargawar zuciya ta furta, "Adeel! Nabeeha ya akai Adeel yasan gidanki? Miya kawo shi kuma?".

Nabeeha ta share hawayen dake mata gudu. "Momy ban sani ba. Tare da wannan ƙanin Haysam ɗin suke Ammar. Kuma Haysam na nan dan yanzu haka a wajensa na baro shi. Wlhy Mammah ina son mijina, ina son rayuwar aurena. Idan na rabu da Haysam mutuwa zanyi. Ki taimakeni Momy, ki taimakeni kada Adeel ya lalata min aure na".

"Ki kwantar da hankalinki. Zuwa anjima zan kiraki. Shima kuma zan samesa a masaukinsa kinji."

"Mammah hankalina bazai taɓa kwanciya ba sai naga Adeel ya bar ƙasar nan na har abada".

"Kar ki damu zai barta. Ki saurare ni".

Ƙitt ta yanke kiran, Nabeeha ta zube ƙasa hawaye na cigaba da zuba mata. Wani makirin murmurshi Rayhana dake laɓe ta saki. Dan tabbas wannan shine babban makaminta a yanzu. Dan haka yanzu wasan zai fara......

□□□□□□

Received at 3:05 PMKullum daga shinkafa, sai taliya da tuwo a gidanki. A'a Hajiya Balki ai an wuce wannan ƙarnin tuni. Mata sun gane yanzu. Idan kuma kin tsaya kallon ruwa lallai kwaɗo zai miki ƙafa, dan kina ji kina gani mijinki zai koma bin gidajen abinci. Daga haka a barbaɗesa kuma😝, to ni dai ba ruwana□, na nuna muku hanyar da zata fishe ku. Wato Ramadan class na Chef Yakudima, bama sai Ramadan ba, ko yaushe ajinta na koyon girki abuɗe yake. Nima dai Bilyn Abdull banga ta zama ba. Dole naje domin sake damƙe Bawan ALLAHn nan Malam Audu a hannuna□. Chef Yakudima zo mu saka labule□.

××××××××××××

"Ruky dan ALLAH ga abincin nan ki miƙama Uncle Ammar. Yace a bama Mu'azz ya kai masa kuma ban ganshi ba".

Kallon Mammah Ruƙayya tayi, dan tasan in har Uncle's ɗin nasu na ɗaki bata aiken su ciki. Dama shara ce ta safe ke kaisu. Idan har ka gansu da yamma ko da rana to su suna falo ne suka aike su ɗakko abu ko basa gidan Mammah ta aikesu, mafi yawancin lokaci ma sunfi saka Mu'azz. Jin batace komai ba, kuma bata miƙe ba Mammah ta kallesu, dai-dai itama Kulu ta buɗe baki zata sake magana sai tai shiru.

“Amsa ki kai masa”.

Cewar Mammah tana kallon Ruƙayya. Mamaki sosai ya kama Ruky, amma babu musu tsakaninsu da Mammah dan haka ta miƙe ta amsa ɗin...........✍

Jama'a, karfa ku bari ayi bikin shagalin girke-girken online class na Chef Yakudima babu ku😘🏃.

Ga Ruky kuma za'a fara aikin lada🏃. Bari muga ya za'a kwashe🏃. A barku haka ko a ƙara biyun♀?.
Received at 3:05
[4/2, 2:42 PM] null: KIƊA A RUWA

........Dai-dai lokacin Nimrah ke shigowa falon goye da Naseer dake barci. Afrah biye da ita da ƙatuwar robar ice-cream a hannu. Itama Nimrah ɗin da ledoji a hannunta.

Da sauri Ruky ta nufi saman tana faɗin, “Kai bari nai sauri na dawo. Irin wannan kayan daɗi haka waya kawo mana?”.

“Kwaɗayayayyya ki kalla gabanki dai kar ki faɗi”. Cewar Nimrah tana harararta. Ruky bata kulata ba ta cigaba da haura staircase ɗin. Hankalinta kwance tai knocking ƙofar bedroom ɗin nasa. Ammar dake kwance daga shi sai shot da vest yana kallon Film a laptop a tunaninsa Mu'azz ne kai tsaye yace, “Come in”.

Kai tsaye Ruky ta tura ƙofar ta shiga abinta, dan hankalinta ma nakan ta koma wajen su Nimrah ne. Sallamarta ta saka Ammar ɗagowa da sauri. Yay bala'in waro idanu waje, gashi ya kasa tashi kamar wanda yay sumar zaune. Sumar ma irin ta tsuntsu daga sama gasashshe ɗin nan. Itama Ruky cak ta tsaya lokacin da take juyowa idannunta suka sauka a kansa. Kanta ta duƙar da sauri tana kif-kif da idanu. Dan Uncle's ɗinsu ko 3quarter na wando da wahalar gaske ka gansu da shi a falo balle shot da vest. Ganin hannunta na neman kifar masa da abinci baima san ya diro a gadon ya iso gabanta ba. Sai jin hucinsa tai a kusa da ita. Yana kama tray ɗin ta sakar masa zata gudu. Hannunta ya cafko kuwa da ɗayan hannunsa, ɗayan yana rungume da tray ɗin.

Da sauri ta furta, “Uncle Mammah na jirana”.

“Idan kin amsa min tambayoyina kenan”.

Ya bata amsa yana jan hannun nata. A haka suka isa gaban gadon nashi ya ajiye tray ɗin. Sosai Ruky ta rikice da mamakinsa da tsoro. Ai tana ganin ya saki hannun nata yana gyara tray ɗin tai hanyar ƙofa da sauri. Taku biyu ya iskota. Ƙafa ya saka mata. Dan haka ta tafi zata faɗi ya sake riƙota da hannunsa. Ruky tai tsirmai-tsirmai da idanu. Gaba ɗaya lamarin Ammar ya gama firgitata.

“Uncle kana lafiya kuwa?”.

“Da sauƙi dai kam Babie”.

“Babie”.

Ruky ta maimaita sunan tana waro idanu, sai dai ta kasa kallonsa, ga jikinta jini na gudu saboda yanda yake tsaye a kusa da ita sosai. Har kamar ma yana neman haɗe jikinsu sai da ta matsa baya. A mamakinta shima sai ya matso. Ta sake matsawa. Ya sake matsota har suka dangane da bango. Yanda ta maƙure lips ɗinta na rawa yaso bashi dariya. Ya dogara hannunsa da bango yana gyara tsaiwarsa...

“Uncle dan ALLAH kayi haƙuri idan laifi na maka”.

Yanda tai maganar murya na rawa ya sashi kai hannu kamar zai taɓa lips ɗin nata sai kuma ya tuna gargaɗin Dada. (Kar kaga na saka an ɗaura auren nan ka zata dami a kala ka samu Ammar. Kaje ka nema soyayyar yarinyata kafin tarewarku. Domin Bilal ma soyayyar Asma'u ya nema harta amince masa. Kaima na baka wannan damar dan in har baka samo zuciyarta ba sai wata shekarar zata tare ita kam......)

Fasawa yayi, ya ɗan haɗiyi yawu yana cije nashi lips ɗin. Cikin wayancewa ya furta, “Yaushe na zama abin wasan ki a gidan nan? Jiya kece mai faɗin aji tausayina a aura min budur-bazar ne ko miye ma kika ce maimaita?”.

Ɓoyayyar ajiyar zuciya ta sauke. Sai kuma tai ƴar dariya da tura baki. “Uncle to miye laifina anan. Bama godiya ya kamata kamun ba na damu da kai. Naga ne yanzu kowa yayi aure kai ko budurwa baka da ita....”

“Ke waya faɗa miki banda budurwa? Ina da ita mana”..

“Lah! Da gaske dan ALLAH Uncle?”.

Kai ya jinjina mata.

Ta ce, “Wooow dan ALLAH wacece?”.

“Gata nan a gaba na”.

Ya bata amsa kai tsaye. Tsabar rashin man kai sai ta fara waige-waige a zuciyarta tana tunanin to wacece? Sai kuma ta zubama laptop ɗinsa dake saman gado idanu. “Dan ALLAH ka nuna min hotonta ALLAH bazan faɗama kowa ba har Ninah.”

“Hummm haba Ruky ni zaki yaudara, ai ko rantsuwa kikai akan Ninah bazata ji ba nasan sai kin faɗa. Faɗa min miye budur-bazar?”.

Dariya ta ƙyalƙyale da ita, sai kuma ta ɗan tura lips da faɗin, “Shike nan tunda baka yarda ba. Uncle kai kamar ba bahaushe ba. Budur-bazar ne baka sani ba?”

Received at 4:41 PM

[4/1, 9:43 PM] Maman Nahnah□□□: “Naji ba bahaushe bane ni. Faɗa min?”.

“Sakin wawa fa ake nufi?”.

“ALLAH ya shiryeki miye sakin wawa kuma?”.

Tai dariyar da ke saka tsigar jikinsa tashi. Kanta tsaye ta ce, “Irin wadda ba'a daɗe da aure ɗin nan ba mana a sake su, sai kagansu kamar ƴan mata amma sun yaɓa aure”.

“Gaskiya kin raina ni. Ni sabuwa dal a leda garan. Sweet sixteen”.

Bakin ta ɗan tura masa da faɗin, “Uhmmm”.

“Dan ALLAH ki tausaya min ki bar tura min lips ɗin nan. Na rantse a matse nake”.

Da mamaki da ƴar rikicewa ta ce, “Na shiga uku Uncle kamar ya?”.

Maimakon bata amsa sai ya bar wajen. Kai tsaye inda jallabiyarsa take yaje ya ɗauka ya sanya dan kar taga gobarar data haɗa. Ita ko duk yanda take son basar da kalamansa sun fara sakata a ruɗani. Dan gaba ɗaya a yanda yake mata maganar ma yau salon na daban ne. Sum-sum ta nufi ƙofa, sai jin rufewarta Ammar yayi, ya zaburo zai yi magana ina harta gudu. Cikin dafe kai ya furta, “Ya ALLAH ka taimaki marayan ALLAH kar yay aika-aika a gaban Dada da Mammah”....

Ashe Ruky tana ruwa□□□.

«««««««»»»»»»»

“Ruky lafiyarki kuwa?”.

Nimrah ta faɗa cikin raɗa tana ƙara tsatstsare Ruƙayya da ido. Sashen da Mammah take Ruky ta ɗan saci kallo. Ganin hankalinta akan bama su Afrah abinci a baki yake ta kama hannun Nimrah kamar zasu yi wani abu a kitchen. Suna shiga ta leƙa ƙofar baya dan tabbatar da su Kulu basa kusa sannan ta dawo kusa da Nimrah.

“Ninah wlhy Uncle Ammar ne ya firgitani. Wai kinga yanda yake min magana kuwa.”

Sosai Nimrah ta waro idanunta da faɗin, “Ke kodai dan kina ruɗe ne”.

“Ba wani ruɗe wlhy. Sai kace wata ƴar ƙwaya..........”

Tsaf ta kwashe labari ta sanar mata. Nimrah akai zugum tana tuno Dada. Yayinda zuciyarta ke ayyana mata (To mike damun iyayen nasu? Ko itama Rukyn an ɗaura mata aure da Ammar ɗin......)

Zungurinta da Ruky tai ya sata kawo numfashi. “Wai tunanin mi kike yi?”.

“Uhmm Ruky anya kuwa kema ba'a ɗaura miki aure da Uncle Ammar ba? Ya kamata hankalinmu ya dawo jikinmu. A baya bamu gane abinda yasa Mammah ke saka mana dokokin rufe jiki da nasiha akan maza ba. Amma tunda abin nan ya faru na batun video ɗin nan nake ta nazari abubuwan da suka shuɗe a baya.....”

“Na shiga uku Nimrah aure kuma? Kada ki haukatani dan ALLAH. Wlhy kin fini ƙarfin zuciyar ɗaukar abu”.

Karo na farko Nimrah tai ƴar dariya da faɗin, “Kema ɗauka zakiyi yarinya. Ni wlhy yanzu ma na ƙara yarda bamu da hankali. Kammu baya gane komai. Inyeee kaga ta Uncle Auta. Har naji sanyi a raina tunda yanzu bani kaɗai bace”.

Harararta Ruky tayi idanunta na tara hawaye. Ta ce, “Dan ALLAH Ninah yi shiru. Wlhy zuciyata bugawa take. Kinga mu koma falo”.

“Miye na wani bugawar zuciya. Mammah tace sai ɗan gata akema irin wannan auren fa. Dan haka dalla malama manta da wani bugun zuciya mu ALLAH ya tabbatar haka ɗin ne ma. Muna kusa da Mammah ɗinmu, kuma muna tare na har abada. Dama ALLAH ya bamu na cigaba da jin daɗinmu da masoyiya Mammah har mutuwa.”

Murmurshi Ruky tayi itama. Dan harga ALLAH zukatansu na ƙaunar Mammah kamar yanda Nimrah ta faɗa....

Mammah najin motsin zasu fito tabar wajen tana murmurshi. Dan tunda suka taho ta biyosu, dan a yanda suka bar falon sai tai tunanin wani rashin jin zasu aikata. Dan tun jiya ta tsargu da yanda suke kallon su Afeef suna dariya. Tasan halin yaran nata ƴan ƙunar baƙin wake ne. Dama kuma ta tabbatar bazasu bar Afeef akan laifinsa ba. Haka kawai hirar tasu ta dinga bata dariya a zuciya. Dan ta fahimci autocinta sun fara hankali......

[×××][××××][×××]

WASHE GARI Litinin tushen aiki. Ƙarfe shida da rabi na safiya Bilal da Ammar masu fita aiki nata saurin zaman shan shayi da Mammah kan tsaresu shansa dole kafin su fita sautin takun da suke jiyowa daga stairscase ya saka su juyawa suna kallon wajen. Ba su kaɗai ba harda Mammah da su Kulu dake tsaftace falon. Isowar sirrintaccen ƙamshin turarensa ya tabbatar musu da mai gayya da aiki ne. Kafin ya bayyana a cikin idanunsu. Babu wanda bai ambaci Masha ALLAH ba a zuciya.
Received at 4:41 PM
reacted with ❤
[4/1, 9:43 PM] Maman Nahnah: Saboda yanda Dadan ya fito a jarumin jarumansa. Baya buƙatar kurantawa ko wasawa, ko maƙiyinsa ya gansa dole yaji eh lallai wankan ya wanku. Sosai Suit ɗin sun zauna masa a jiki tamkar kayan gadonsa.

“Anya yau ba Dadanmu za'a kalla matsayin shugaban ƙasa a fadar shugaban ƙasar ba”. Bilal ya faɗa da iya gaskiyarsa. Amshe masa Ammar yay da shima. “Yaya kamar ka shiga zuciyata ka karanto abinda ke cikinta.”

Dada daya ƙaraso kamar yasan gulmarsa suke ya zuba musu harara. Zamansu suka gyara kuwa kowa na haɗiye sauran gulmar a zuciyarsa. Mammah tai murmurshi, cikin kafesa da ido ta ce, “Kun haƙura dai kenan?”.

“To Mammah ya zamuyi kema kina bayan Janar”.

Nan ma murmurshin ta ƙara yi, dan jiya da dare ya shiga mata hira yake mata ƙorafin wannan aiki. Shine tai zama na musamman ta masa nasiha yanda ya kamata. Bai dai ce komai ba a jiyan, amma tasan dama bazai bijirema lallashinta ba. Ya sake gaisheta, suma su Bilal suka gaishe shi duk da sunyi a ɗazun da suka dawo salla. Mammah tasan bazai ci abinci ba a yanzu. Dan haka ta saka Kulu kawo masa zallar ruwan zafin da babu komai a cikinsa. Shi kuwa yasha, yana cikin sha ɗin ne Mu'azz ya fito dan shima zai wuce makaranta. Sai ga Biebah dake son shiga kitchen.

Duk gaishe sa sukayi. Ya amsa musu da kulawa. Dai-dai ya miƙe Bilal ke tambayar su Nimrah. Mu'azz ya ce, “Tab Uncle kaima kasan suna can suna barci. Tunda suka daina zuwa makaranta ai suka samu wannan lasisin. Yanzu haka sai su kai sha ɗaya a gado”.

“Mu'azz kaji tsoron ALLAH banda sharri. Suna kai dai tara amma ba sha ɗaya ba ”.

Biebah ta faɗa tana hararar sa. Mu'azz ya tura baki da faɗin, “To Small Mom miye marabar 9 da 11 ɗin?”.

“Awa biyu”.

Ta sake bashi amsa tana hararar tasa dai. Shi dai Dada baima nuna yana jinsu ba. Hasalima sallama yayma Mammah dake jera masa addu'oi sannan ya fice. Su Ammar na take masa baya..........✍

Received at 4:41 PM

[4/2, 2:47 PM] null: KIƊA A RUWA

.......Sun fito compound da Sanda ya gama sharewa tsaf, dan yana tsaka da banruwan fulawa ne ma ya hangosu ya ɓuya. Sai maigadi ne ya zo da sauri yana gaishe da Dada. Sannan suka gaisa dasu Ammar.

“Alhaji dama tun ɗazu baƙi suke jiranka.”

Da mamaki Dada daya ɗan zuba masa ido ya furta, “Baƙi?”.

“Eh wlhy suna wajen gate. Sai dai daga gani jami'an tsaro ne. Amma fa da wasu zuƙa-zuƙan motoci suke baƙaƙe wulik kamar na shigar shugaban ƙasa”.

Dada baiyi magana ba, sai ma juyawa yay ya kalla Bilal. Bilal ya fahimci abinda yake nufi, dan haka ya miƙama Ammar briefcase ɗinsa ya nufi gate, sai kuma akai sa'a ma jami'an dake a gidan tun dawowarsa sai ga shugabansu ya shigo. Tare suka dawo inda Dadan yake da Bilal, yay gaisuwa. Kai kawai Dada ya jinjina masa.

Cikin ƙara gyara nutsuwarsa ya cigaba da faɗin, “Sir! Masu rakkiyarka ne daga fadar shubagaban ƙasa. Idan ka amince zan shigo da shugaban su”.

Kallon juna Bilal da Ammar sukayi suka kashe ido da jinjina. Sai kuma suka gimtse murmushin fuskokinsu dan dai-dai nan Dada ya jinjinama jami'in kai. Da alama yau babu ƴan maganar a kusa. Da sauri kuwa Jam'in ya juya, dan ya gane yaren Boss ɗin. Babu jimawa suka dawo da wani mutumin dake sanye cikin baƙaƙen suit shima. Bazai wuce sa'an su Ja'afar ba. Sai da suka iso wajen yay gaisuwa irin ta girmamawa sannan yay bayanin dake tafe da shi.

“Ranka ya daɗe, bisa umarnin Shugaban Ƙasa, mun zo ɗaukar nauyin tsaronka da rakkiyarka zuwa Office.”

Birkitattun idanunsa ya zubama jami'in, aiko bawan ALLAH babu shiri yay ƙasa da kansa. Zuciyarsa kuwa sai bugawa take da sauri-sauri. A ransa ya furta, (Tab wlhy bazan iya ba. Dama haka mutumin nan yake da cika waje. Ina wannan filin ba nawa bane dan zan iya tona kaina). A zahiri kuwa ya kasa ɗago kai ya kalla Dada a karo na biyu, shima kuma baiyi magana ba ya nufi gate abinsa. Da sauri su Ammar suka bisa kuwa, dole suma suka take musu baya.

Tabbas maigadi baiyi ƙarya ba. Zuƙa-zuƙan motoci ne da ko wanda bai san mota ba yasan an saye su da kuɗaɗe masu nauyin gaske. Ga wasu baradan jaruman tsaye masu jiran kota kwana. Suna fitowa duk suka sake nutsuwa, sai kuma sukai caaa suna miƙa gaisuwa. Hannu kawai ya ɗaga musu..

Wanda ya masa bayani a cikin gidan nan ne dai ya buɗe masa motar tsakkiya da saurinsa. Dada yay ɗan jimm yana karanta addu'ar hawa abin hawa kamar yanda ya saba koda tashi ce sannan ya shiga ya zauna. Jami'in ya maida ya rufe. Sannan ya zagaya gaba ya zauna ta gefen mai zaman banza, cikin waɗancan kuma wani ya buɗe mazaunin driver ya shiga. Matsowa su Bilal sukai suka masa bye, ya jinjina musu kai yana lumshe idanunsa.

Suma sauran jami'an duk sun shiga sauran motoci biyun. Daga haka suka harba kan titi. Kasa haƙuri su Ammar sukai sai da suka koma cikin gidan kaima su Mammah rahoto. Dan Ammar ma harda video ya ɗauka dama. Kuma ya ƙudiri aniyar ɗorashi a media dan zukatan maƙiya su buga.....

^^^^^^^^^^^^^^

A ɓangaren Daddy Imran ma hakan ce ta faru. Yayi shirinsa tsaf cikin Suit masu duhu Ammie tai masa rakkiya compound da shirin shiga motarsa, Asma'u dake riƙe

da briefcase ɗinsa na roƙonsa bin Ammie kasuwa dan za'ai sunan Aunty Lailah gobe, shi kuma yace a'a tanata shagwaɓa. Gefe Khalifa na mata dariya, Lolo kuwa na ɗakinsa yana shirin makaranta. Isowar mai wankinsu ya katse faɗan Khalifa da Asma'u. Ya gaishesu sannan yake sanar muku baƙin dake gate.

Mamaki ya kama Daddy Imran sosai, amma sai yace maiwanki ya shigo da Ogansu yaji lafiya. Saɓanin na Dada shi nashi sojoji ne, duk da dai a wanda ke waje akwai wasu jami'an harda ɓoyayyu ma. Yanda akaima Dada bayani anan shima haka akai masa. Yasan hakan normal ne dama, amma yayi tunanin sai sun fara zuwa office a yau sannan za'a basu waɗan nan damammakin. Dole yay sallama da iyalinsa yana sake jaddadama Asma'u karta fita ko'ina. Daga haka aka buɗe masa mota suka wuce fadar shugaban ƙasa.

)))))))★(((((((
Received at 4:41 PM
[4/1, 9:43 PM] Maman Nahnah🌹🌹🌹: Tsakanin isowar motocin Dada dana Daddy Imran babu nisa. Sai dai da yake a faɗar shugaban ƙasar ma kowa da fanninsa sai basu haɗu ba. Kai tsaye motocin ɗaukar Dada sun nufi sashen ofishin shugaban ƙasa ne. Wani babban jami'i Chief of Protocol ya tarbe shi. Dan motocin na kammala tsayawa jam'in nan yay wuff ya fita a gaban mota kamar sauran suma yazo ya buɗe sashen da Dadan yake. Sai da yaja fin mintuna biyu, dan sai da ya karanta addu'oi sosai tare da ƙarema wajen kallo sannan ya sauke ƙafarsa ta dama dake sanye cikin haɗaɗɗen takalminsa. A take ƙamshin turarensa ya isa hancinansu, duk da suma ƙamshin nasu turarrukan sun shiga nashi hancin.

Cike da girmamawa Chief of Protocol ya miƙa gaisuwa. Tare da faɗin, "Ranka ya daɗe Sir. Shugaban Ƙasa ya bayar da umarnin a raka ka kai tsaye ofishin ka."

Kai kawai ya jinjina masa kamar na baya, dan tun maganarsa da Mammah a gida bai sake magana da kowa ba. Wannan kuma salon takun manya ne. Jami'an da suka ɗakkosa har yanzu basu ji muryarsa ba, dan haka suka fara tunanin wai kodai bebe ne mutumin nan?. Babu mai basu amsa dan haka sukai gum, saboda kwarjininsa kawai da cikar kamala da kamewarsa ga nutsuwa da gizago ya sakasu jin shakkarsa, tare da yarda da batutuwan mutane a kansa. Dan a weekend ɗin nan babu sunan daya kai sunan sa dana Imran yawo sai na shugaban ƙasa.

Yanda Chief of Protocol ke gaba, sai jam'in nan dake nuna shine shugaban wannan tawagar a tare da shi, Dada na bayansu, bayansa kuma sauran jami'an nan ne ke take masa baya dole abin ya birgeka. Dan kamar an tsara su ne, suna sauke ƙafa da ajiyeta a tare kaida ka gani kasan rakkiyar ta babban kai ce. Gashi suna tafiya ne ta cikin dogon corridor mai sanyi, shirun da babu hayaniya. Tun fitowarsa motar ƴan median fadar ta shugaban ƙasa suka dasa musu camara kuma. Dan dole ne a saki labaran shigowar Chief Of Staff na farko office ga ƴan ƙasa.

Ko'a jikin gogan naku. Takunsa yake cike da ƙasaita da mazantaka. Fuskar nan ciɗin-ciɗin yau ta asalin sojan sa a fagen yaƙi. Ga hotunan tsoffin shugabanni da suka cika bangon dogon corridor ɗin suna kallonsa kamar suna tantance shi da masa barhaban. A ƙarshe aka tsaya a gaban wata ƙofa dake ɗauke da baƙin allon rubutu da kalar gold.

CHIEF OF STAFF TO THE PRESIDENT.

Shine a rubuce ɓaro-ɓaro ga mai kallo. Chief of Protocol ya danna wani maɓalli dake a bango a take ƙofar ta raba kanta biyu. Makeken Ofishin mai girman gaske ya bayyana a idanunsu. A tsaftace yake, ga ƙamshi na tashi mai ainahin saka nutsuwa. Matuƙar tsaruwa wannan office ya tsaru. Dan kuwa komai na cikinsa yana tabbatar da ƙarfin ikon mamallakinsa .

Dada ya tsaya na ɗan lokaci yana karanta addu'oi. Kafin ya saka ƙafarsa ta dama batare da ya daina ambaton ALLAH ba. Dan shine cikakken sarki gagara misalin masu misali. Mai cikakken iko da rahama ga jinƙai ga bayinsa. Shike bada dama ga wanda yaso a sanda yaso. Shike daka girma da cikar kamalar bawa a idanun ƴan uwansa bayi badan ya kasance mafifici a garesu ba. Ba'a farautar ɗaukaka ko girma

da kuɗi ko ƙarfin ƙwanji. UBANGIJI ne kawai ke badawa kamar yanda ya bama wannan bawan nasa Haysam Abdul-rasheed Shehu Kobi.

A hankali ya kai zaune cikin kujerar da aka gyara masa idanunsa a lumshe bakinsa na cigaba da ambaton UBANGIJI da neman agajinsa. Dan tabbas yanzu ne wasan zai fara. Farawa irin ta KARE JINI. BIRI JINI. A yanzu yaƙine na kwatar ƴanci da neman tsira. Kuma duk zasu fara ne ta silar wannan kujera....

★A can ma Daddy Imran ya shiga nasa babban ofishin dake da ƙarfin faɗa aji akan tsaron ƙasa. Shima dai an shirya shi da girma da aji tamkar na Dadan. Dan tsarin da akaima offices ɗin duk mai hankali ya tabbatar da gayya shugaban ƙasa yasa akayi su. Ga tsaro mai tsaurin gaske dake tabbatar ma maƙiya koda zasu iya keta wannan alfarmar sai da ƙarfin ikon ALLAH. Sannan The two shadows sun iso FILIN YAƘIN. Yanzu ne za'a banbance MAZAJE DA MAZARE......

============
Received at 4:41 PM
[4/3, 10:58 AM] null: KIƊA A RUWA 3

34

.......Isowar sa gaban su ya saka cikin jami'an nan biyu saurin jawo kujera ya ajiyema Dada. Koda ya kai zaune wani kalar zaman ƙasaita yayi tare da harɗe hannayensa a ƙirji ya zuba musu idanu. Ɗakin yay tsitt, sai nishinsu na wahala kawai kake ji. Mintuna goma cif Dada ya cika yana nazartarsu a haka kafin ya warware hannayensa ya ciro abu a aljihunsa. Wata ƴar mitsilar kwalba ce sai syringe guda uku a ledar su. Baiyi magana ba ya shiga buɗe ɗaya a ciki tare ta ɓalle kan kwalbar dake tabbatar da ruwan allura ne a ciki ya zuƙa a syringe ɗin ya miƙama ɗaya a cikin jami'an. Amsa yay da sauri, batare da ya tambaya ba kawai ya dannama ɗaya allurar. Aiko sai da ya saki wani ihun azaba. Saboda ruwan allurar wani mugun raɗaɗi ne da shi, kuma yana fara shiga jikinka kake jin hakan. Mintina biyar basu cika ba jikinsa ya fara rawa. Ga zufa ta bala'i ta jiƙesa sharkaf. Sai ga shi ya fara rattafo zance sala-sala.

Cikin razananniyar murya Dada ya jefa masa tambaya, “Kayan miye kuka wuce da shi?”.

“Mun ɗakko waɗan nan motocin daga gaɓar ruwa. Kuma a haka aka shigo dasu ta kwantaina. Makamai ne a ciki da bama-bamai. Mun kaisu inda aka umarcemu ne kawai”.

“Waye Ogan ku?”.

“Oga Jo kawai muke kiransa. Ban san ainahin sunansa na gaskiya ba”.

“Tun yaushe kuke masa aiki?”.

“Shekara uku ke nan”

“A ina yake zaune?”.

“Bamu san taka maimai wajen zamansa ba. Kawai idan zai sakamu aiki ne yake gaya mana inda zamu sameshi.”

“Ku nawa kukai aikin?”.

“Mu goma ne”.

Shiru Dada bai sake tambayarsa komai ba. Sai ma wani ruwan allurar ya sake ɗiba ya miƙa musu. Na kusa da shi shima aka danna masa. Kamar dai na farko shima tuni jikinsa ya rikice. Koda Dada ya tambayesa. “Ina sauran wanda kukai aikin?”.

Baima bari ya rufe baki ba ya fara bayani. “Akwai aikin da zasuyi ma Oga. Shine suka je ganawa da shi. Amma na tabbatar zasu dawo gida sun kwana a yau ɗin”.

“Ku miya hanaku zuwa?”.

“Kowa da aikinsa.”

“Dan ALLAH Oga karku kasheni, wlhy azaba nake ji a jikina kamar ana dafa ni”.

Dada bai tanka masa ba. Ya bada shima ɗayan akai masa allurar. Shima yana fara nashi vibration ɗin ya jeho masa tambaya.
"Ina kuka kai kayan?".
Tsaff ya bada address ɗin wajen.
"Mi za'ayi da su?".
"Bamu sani ba muma. Amma mun ji Oga Jo kamar na magana da wani a waya cewar za'a fara kai su jihohi daban-daban, amma bamu san akan aikin minene ba. Dan yanzu haka yan uwan mu akan haka sukaje ganawa da shi".
Ba ƙaramin zafi zuciyar Dada keyi ba. Komai bai sake cewa ba ya miƙe ya fice. Bayansa su Faro suka bi suma zukatansu na zafin. Tsumin sojojin na ƙoƙarin tashi. Dan wlhy badan suna da target ba yaran nan bazasu kwana da rai ba yau......

★★★

Tubda suka shigo ɗakin sirrin babu wanda yace da ɗan uwansa komai. Sai Dada dake faman kai-kawo. Kusan mintuna ashirin Dada ya kallesu.
"Idan lissafina yayi dai-dai Ojo ne Jo".
"Ojo fa Sir!?".
Cewar Dabo a kiɗime.
Batare da Dada ya kallesa ba ya ƙarasa gaban computers ɗin ɗakin. Sai da ya zauna kai tsaye ya cigaba da faɗin. "Bazai taɓa bari su san inda yake ba. Saboda su waɗan nan amfani kawai ake da su. Kuma suna cikin yaran da aka ɗiba a ƙauyen can aka horar. Dole yau za'a fita wani operation ɗin kafin su farga da waɗan nan basa nan. Banda harbi. Dan kaf yaran nan ina son su a raye. In sha ALLAHU zamu maida su barazana ga mutanen nan. Yusuf ka nutsu ka tantance a cikin hotunan yaran tun suna ƙananu waɗanne ne a cik?i. Ka kawo doctor ya binciki lafiyarsu dan alamu ya nuna suna shaye-shaye. Ayi treating ɗinsu da ƙyau, a kuma fara basu abinci mai ƙyau. Zan tanadi malamin da zai fara dawo da hankalinsu jikinsu, duk da bamu da tabbacin da wane addini ma suka tashi ba a yanzu."
"Yes sir. In sha ALLAHU."
Dada ya juyo yana kallon Imran. "Imran matsayinka na NSA ya kamata ka bada umarnin tantance kaf jami'an hukumomin tsaro a aikinka na farko. Akwai waɗan da dole sai an sauke su a aiki zamu samu filin namu aikin. Musamman manya-manyan saman nan. Akwai abubuwa da yawa da suka sani.
Received at 5:37 PM
2 people reacted with  "Hummm".
Dada ya faɗa. Imran yasan iya amsar kenan. Dan haka ya cigaba da tsokanarsa. Sai da ya tabbatar ya kaisa bango sannan ya barsa suka koma maganar Office. Sun iso UNIT ZERO ana kiran magriba. Sai suka tsaya sukai salla a farkon anguwar sannan suka ƙarasa gidan. Da su Dabo suka fara cin karo ata ɗayan sashen da aka gyara dama dan ajiye mutane. Cike da girmamawa suka fara gaishesu. Imran kawai ya amsa. Gogan hannu kawai ya ɗaga musu.
Sun ƙaraso wajen da aka shirya cells da yawa da ƙarfuna. Na can ƙarshe da ihu ke fitowa suka dosa. Faro na tsaye daga ƙofa hannuwa a aljihu fuskar nan babu ɗigon fara'a. Sai wasu jami'ai biyu cikin baƙaƙen kaya fuskar su a rufe idanun su da yankan baki kawai kake iya gani. Suna sakama mutane uku dake a kujera shocking a jiki, shine suke ihu.
Isowar su Dadan ya saka Faro fitowa. Kauda kai Dada yay daga kallon matasan yaran ya maida kan faro. Dai-dai Imran na faɗin. "Wai sunƙi magana ne?".
Faro ya jinjina kansa yana furzar da huci. "Sunƙi. Sun dage akan aiki kawai aka basu basu san masu kayan ba. Sannan basu san minene a motocin ba. Sannan sunƙi faɗa mana inda sauran suke. Sai nake ga kamar da gaske basu sani ɗin ba....."
"Ƙarya suke yi. Koda basu san su waye ogannin ba sun san mi suka ɗakko. Sannan su dukkansu yara mutum ɗaya ne. Da ace ba mutum ɗaya ya basu horo ba, dole su samu saɓanin magana."

Dada ne mai maganar. Batare da ya jira amsawarsu ba ya tura ƙofar ya shige. Binsa da kallo Imran da Faro sukayi. Sai kuma suka bi bayansa suma cikin wajen....... ✍

Received at 5:36 PM
reacted with 
[4/5, 9:35 PM] +234 708 144 4204: KIƊA A RUWA 3

35

.......Yanzu saura Ruƙayya da Ammar. Duk da tasan Ammar na matuƙar son Ruƙayya, amma ita bama ta fahimci ina aka dosa ba, Ammar ɗin kuma da alama ya kasa faɗa mata. Tana fatan ALLAH ya daidaita su suma kamar yanda Bilal da Asma'u suke. Dan a yanzu itama babban fatanta su gama jarabawar nan kawai kowa ya tare ɗakin mijinsa ta samu nutsuwa. Hatta Nabeeha duk iskancin nan nata Mammah addu'a take mata ta shiriya kodan samun zaman lafiya a gidan, jinin Yaya Nasiru bazai taɓa zama abin ƙi a gareta ba har abada. Dan Nasiru ya wuce abin da zasu yarda.

Wannan nasiha ta Mammah ta kawo masalaha su Ruky suka nutsu a ɗaukar lassing ɗinsu. Dama dai Alhamdullah a ɓangaren karatu basu da wasa. Ga Mammah ta musu register a online class ɗin Chef Yakudima. Dan ta aikoma Mammah alƙawarin data ɗauka na kayan snacks masu daɗin tsiya daya saka Mammah sake gamsuwa da aikinta. Ba'a nan Mammah ta tsaya ba, takan zaunar da su cikin hikima tana musu nasihohi da suka shafi aure. Wani lokacin Ruky kan dinga yi ma Nimrah dariya wai da ita Mammah take da Small Mom. Su dai ba yanzu ba. Ita dai Mammah takan yi dariya kawai.

{×××}{×××}{×××}

Duk yanda su Hanoon suke taka tsantsan da su Ruky yau da alama muguntar tasu zata motsa. Dan tunda Afeef ya sakko daga sama suke kallonsa suna ƙus-ƙus. Tun bai kulasu ba har yay tsaki ya tashi ya bar falon.

“Zakaci ubanka. Shegen ƙafa kamar na ƴan tsaki.”

Ruky ta faɗa tana raka shi da harara. Tsakin Nimrah taja itama da faɗin, “Ai garama ƴan tsaki kamar dai wani tsuntsu da ake kira zalɓe. Ya kamata yau yaji a jikinsa.”

Ruƙayya tace, “Ni kaina ina son ya fara ji a jikin san. Kina da wani plan ne?”.

“Akwai kuwa. Zo ki ji.......”

Ta gwargawaɗama Ruky komai a kunne. Dariya suka sanya. Tare da tafawa. A lokacin Biebah ke fitowa a kitchen. Sai suka gimtse. Dan basa son ta gane komai balle ta hana su. Bako ta gane ɗin ba. Sai ma aiki data sakasu na gyara mata ɗakin baƙi dan yau Faro zai zo. Shima take yima abu a kitchen. Yanda suka tashi ba musu yin aikin nan ya bama Biebah mamaki. Amma sai batace komai ba ta juya ta koma.

Sun fito sai karaf a kunensu Hanoon na cema Afeef, “Bro bakayi wankan bane?”.

Ƙaramin tsaki yaja yana bata amsa da, “Banyi ba, wannan Mumun yaron ashe ya birke makunar water higher kafin ya fita. Shine na ɗan kunna ruwan yayi zafi a ɗakin su Dayyan na ɗibo acan Dad ya kirani na kawo miki waya”.

Kallon juna Ruky da Nimrah sukai. A take kansu ya kawo haske. Komawa sukai da baya. Wuff suka shige ɗaki Nimrah na faɗin, “Ga dama ta samu ma ai basai anje da nisa ba”.

“Kamar ya?”.

Cewar Ruky yana waro idanu. Nimrah bata bata amsa ba. Sai ɗan goran dake ɓoye ta ɗakko tare da leda. “Da wanne za'a fara?”.

“Kai jama'a. Hot pepper kin fini bala'i fa. Yanzu dan ALLAH wa kika saka ya samo miki abin nan?”.

“Hahhh kina wasa dani. Kulu na saka shekaran jiya da zata gida. Wannan kalkashine kwanansa biyu kenan a jiƙe. Wannan karara ne”.
“Miye karara?”.
“Banza kefa haihuwar birni ce baki san komai ba. Wani abu ne mai shegen ƙaiƙayi. Idan aka sakama mutum sai ya koma kamar ya haukace”.
Dariya Ruky ta sanya babu alamar tausayi. Ta ce, “Yayi yanzu ya za'ayi?”.
“Muje ki gani”.
Da sanɗa suka fito a ɗakinsu suka haura sama. Sun san Mammah barci take yanzu. Dan in tai sallar Azhar takan ɗan kwanta. Small Mom da su Kulu hankalinsu nakan aiki a kitchen. Uncles duk sun fice. Mu'azz ma na school. Dayyan kuwa basu san ina yake ba. Ɗakin Mu'azz da Afeef yake zaune suka nufa. Ɗakin kaca-kaca. Shiyyasa kullum Mu'azz cikin ƙorafi yake yanzu. Sai da suka rufe kofar sannan suka shiga Bathroom. Shi da ɗan sauƙi a gyare yake, sun san kuma Mu'azz ya gyara kafin ya fita.
Sun san shower gel ɗin da Mu'azz ke amfani da shi. Dan haka suka ɗauki ɗayan da suka tabbatar na Afeef ne. Tsabar mugunta yana da yawa fa a ciki amma suka tatse rabi a wata robar sabulu da babu komai ciki suka haɗa da kaf kayan wankan bayin suka ɓoye sannan suka zuba karara a sauran suka ajiye. Sosansa ma suka ɗauka suka barbaɗa.
Received at 6:24 AMReactions: Tsakanin Nimrah da Ruky kar ta san kar ne. Tun ba'ayi nisa ba Ruky ta gane ƙarya Nimrah take. Da ƙyar ta iya gimtse dariya ta lallaɓa ta ɗauki wayar Biebah ta kunna recording ɗin video. Abu ya kai yanzu Afeef susa harda cokali. Da wuƙa ma ya rarumo aka ƙwace. Ya koma bango, ganin bazai masa ba ya koma ya ɗakko cokula. Riga dai tuni ya saluɓe ya watsar. Hijjabin Mammah kam sai da aka tsawatar masa. Amma ya gwada son cirewa yafi sau babu adadi.
Ita Hanoon da farko iya wuyanta ne da hannaye. Sai da ya kacame ta gudu ɗaki wai zatai wanka. Aiko tana zuboma kanta ruwan nan tun a bayin ta ƙara haukacewa. Da ƙyar ta iya ɗauro towel. Ganin haka Mammah ta hana Nimrah zuwa yin wanka, sai kaya da tace Biebah ta kaita ta cire. Caraf Ruky tace bari ta kaita. Suna shiga ɗaki Nimrah ta fashe da dariya.........✍
Received at 6:24 AM
[4/5, 9:35 PM] +234 708 144 4204: KIƊA A RUWA 3

36

.........“Muguwa, wlhy dama na zargi ƙarya kike. Kai Trouble Queen kin iya munahinci”.
“Bazaki gane ba Trouble Buddy, dole fa sai da haka. Idan ba hakaba kin san halin Mammah tsaff zata ramfomu. I sauri bani kaya na canja mu koma kada a cigaba babu mu kallo ya wuce”.
Kwantar da hankalinki ai ina mana video. Tafawa sukai Nimrah na rungume Ruky. “Sai dake abokiyar ɓuruntu. Dole mai bakin uwa yasha bulalarmu”.
Haka suka cigaba da shaƙiyancin su kafin a canja riga a fito. Sai dai yanzu Nimrah ta rage nata soshe-soshen wai taji dama-dama data cire rigar. A wannan halin su Ja'afar suka iso gidan. Sai kuma ga doctor da suka kira shima ya iso. Nan fa doctor ya fara duba Afeef da yafi jin jiki. Abinka da fata fara jikinsa yay burɗin-burɗin kuma jazur kamar borin jini. A haka ma na Hanoon yafi nunawa saboda bayan farin ta tana ƙarawa da mai ita. Shi dai doctor bai gane komai ba sai hasashen Allergy ne kawai. Maybe ruwan da sukai wanka da shi ne. Nan fa kowa yace badai ruwa ba. Sai dai ko wani abu suka ci.
Koda ya tambaye su shi Afeef Banda kukan a taimakeshi babu abinda yake yi. Itama Hanoon ta kasa bada amsa. Sai da aka zo kan Nimrah ne tace ita bataci komai ba. Kuma batai wanka ba. Sai ta sake rikita tunanin doctor. Gashi ita bai maga komai a jikinta ba. Ƙarshe sai ya ɓige da wai jininta ne mai ƙarfi shiyyasa nata bai ƙarfi kamar nasu ba. Zai mata allura kamar su ta wayance ita dai a bata magani kawai tunda bai kai nasu ba. Nata ƙaiƙayin ma ya fara sauka. Maganin kuwa ya bata, akace

a kaisu ɗaki su kwanta dan zasu iya yin barci. Nimrah bata sha magani ba. Cike da dabara ta juyema Ruky data kawo mata ruwa shi a hannu. Dan haka koda suka je ɗaki ƙofa ma suka rufo suka hau rawa....

ALLAH ya shirya. Yau dai Afeef ya gane ALLAH ɗaya ne shi da Hanoon😂♀.

\••••\••••\••••\••••\

Biyar saura wasu mintuna Dada ya dawo gida. Dan hankalinsa duk yana nan. Babu arziƙi daga sallar Asr ya baro office ɗin. Bai samu kowa a falon ba. Sai su Kulu dake kai-kawon shirya abincin Faro a falon baƙi. Biebah na ɗaki tana shiri. Mammah ma bata fito ba tai zaman azkar bayan sallar la'asar. Afeef da Hanoon suna can suna barci wahala. Nimrah na ɗaki a zuwan barcinta take, sai dai hirarsu ma suke sha da Ruky hankali kwance, sai dai dole ake ƴar ƙasa-ƙasa kar asiri ya tonu.

Mammah ta amsa sallamar Dada tare da bashi izinin shigowa. Cikin kasa ɓoye mamakinta ko zama bata bari ya ƙarasa yi ba ta ce, “Yau dai ka dawo da wuri ALLAH yasa lafiya?”.

“Mammah kece kika tayar min da hankali. Duk da su Ma'aruff sun min bayanin doctor ya duba su”.

“Nima na rikice a ɗazu ɗin ne. Yara duk sun rikice kamar masu aljanun susa”.

“Mi doctor ɗin yace to?”.

“Wai ƙila wani abu suka ci da jikinsu baya so. Amma ita Nimrah ma da sauƙi. Hanoon da Afeef ne suka fi jigatuwa kam. Duk suna can suna barci ya musu allura”.

Karan farko Dada yay ɗin jim cikin nazari. Sai dai baice komai ba ya miƙe yana faɗin, “Bari na gansu”.

Miƙewa itama Mammah tayi suka fita tare. Ɗakin su Nimrah ne kusa da nata. Dan haka nan Mammah ta fara nufa yana biye da ita. Tana taɓa ƙofar da yake kunnen su a wajen yake Nimrah ta baje, Ruky ta yayimo blanket ta rufa mata. Ta koma gefenta ta zauna tana ɗaukar littafi batare data duba inama ta buɗe ba. Sai da su Mammah sukai sallama ta gyara fuska alamun tana cikin damuwa ta amsa, ganin harda Dada ƙirjinta ya buga. Yawu ta haɗiya masu nauyi tana ambaton sunan ALLAH da miƙewa. Sai kuma ta rissina tana gaida Dada da tunda ya shigo idonsa akan littafin hannunta ya fara sauka.

Koda ya amsa mata sai karaf ta ce, “Mammah bari na kawo ma Dada ruwa naga yanzu ya shigo”. Bata jira amsar su ba ta fice. Dada kawai ya girgiza kai murmushi na son ƙwace masa, amma sai ya basar yana maida hankalinsa ga Nimrah da Mammah ta yayema bargo sai wani nishi-nishi take. Kallonsa da Mammah ta ɗago tayi ya sashi ƙarasa takawa gaban gadon sosai, ya wani zubama mutuniyar ido. Tsaff kuwa suka shige cikin nata.

Received at 6:24Yanda take fiki-fiki da su tana narke fuska tamkar zata saki kuka sai taso bashi dariya itama. Bai dai dara ɗin ba ya kauda nashi. Dan fuskar tasa ma a tsuke take tam.

Nimrah aka sake narke murya ita a dole mai ciwo ana gaishe shi. A taƙaice ya ce, “Ya kike ji?”.

“Dada na samu sauƙi. Sai dai bakina ɗaci. Jikin kuma har yanzu yana zafi. Ga barci ina ji yaƙi zuwa”.

Yanda ta jero zantukan yasa Mammah ƙara rikicewa. Ta fara salati da faɗin, “Sai ya sake kira mata likita ya dawo a kuma dubata ko ya kaisu asibitin tunda su Ja'afar sun koma kasuwa. Ga su Bilal babu wanda ya dawo.”

“Mammah relax, normal ne zata daina ji. Badai ya basu magani ba?”.

“Muhammad bazaka gane ba yaran nan sun sha wahala wlhy”.

“Tunda an basu magani wahalan ya ƙare ai. Ta kwanta ta rufe ido barcin zai zo.”

Ita dai Mammah badan ta gamsu ba suka baro ɗakin. Na su Biebah suka shiga. Anan kam kallo ɗaya yayma Hanoon dake barcin wahala ya san ga asalin mai jiyyar nan dai. Da yake barci take Biebah ce kawai data gaida Dadan tai masa bayani akan

Hanoon ɗin nanma suka fito. Daga nan yace Mammah basai ta haura sama ta wahala ba ta bari zai duba Afeef ɗin shima. Dan haka shi kaɗai ya shiga ɗakin Mu'azz ya duba Afeef dake barcin wahala a tuɓe an ware masa ac kamar Hanoon yayi ɗai-ɗai a gado.

Dada dake ayyana (JIKI MAGAYI AI) A zuciyarsa ya fita zuwa nashi ɗakin. Sai a lokacin murmushin da yake ta riƙewa ke fita a fuskarsa, dan tun a kallon farko da yayma Ruky ya gane basu da gaskiya, saboda book data riƙe ma ƙasa ne a sama, itama uwar dabar langyaran nata ya san na bogi ne. Yaran nan sai a barsu kawai. Wanka ya shiga. Bayan ya fito yana shiryawa ya kasa shanye tambayoyinsa. Waya ya ɗauka yay kiran Mammah yace ta saka Ruƙayya ta kawo Nimrah ga wani magani zai bata saboda ɗacin bakin itama ta samu tai barci. Mammah bata kawo komai a ranta ba ta aiki Hinde dake zuba mata shayi ɗakinsu Nimrah.

Hinde na isar da saƙon Mammah aka shiga yar kallan kallo tsakanin Nimrah da Ruky, sai dai ba damar ƙin zuwa. Ga Hinde taƙi tafiya dole suka shanye maganar bakunansu, Ruky ta kama Nimrah tana sake jangwaɓewa kamar gaske suka nufi upstairs ɗin. Dariya taso kama Kulu dake hangensu ta ƙofar kitchen. Anya ta taɓa ganin yara masu rashin ji irin waɗan nan biyun? Maza sukafi irin wannan iya shegen, amma su sun ma fi wasu mazan...

Ruƙayya tai knocking, Dada dake zaune a cikin kujera ya basu izinin shigowa. Har suka ƙaraso inda yake bai ɗaga kai ya kallesu ba, yanata rubuce-rubucen sa kamar ma bai san da su ba.

"Zaunar da ita kije ki haɗa min abinci". Yay maganar tasa cikin ishara ga Ruƙayya. Kamar dama abinda Ruky take fata kenan tsilim ta nufi ƙofa. Nimrah kamar zatai kuka ta bita da kallo. Sai dai babu damar magana. Mintuna kusan biyu da fitar Ruky Dada yayi kamar ya manta da Nimrah, sai ta hau gyangyaɗin ƙarya. Abinda bata sani ba duk motsinta akan idanunsa ne, dan ta gefe yake kallonta yana aikinsa. A bazata ya furta.

"Sai yanzu barcin yazo kenan?".

Fiskewa tai kamar bataji ba. Ta cigaba da gyangyaɗin har kamar zata tuntsura. Ɗagowa yay a karo na farko ya zuba mata idanu, tasirinsu ya sata jin rikicewa. Tai wani laɓai-laɓai da fuska tana kawo numfashi mai nauyi irin ta farka ɗin nan. Suna haɗa ido ya ɗage maga gira sama. Kame-kame ta fara da faɗin, "Dada barcin ya fara zuwa, naje na kwanta dan ALLAH?".

Bai amsata ba saboda dawowar Ruky datai knocking da sallama. Izinin shigowa ya bata. Ruky na ajiye tray ɗin abincin a table ɗin gabansa, cikin shagwaɓa ta ce, "Dada Mammah tace na koma yanzu zan kaima Uncle Haydar da yazo ruwa shima".

Nuni yay mata taje, dan baya son ma yayi magana koya kalleta ya sake rikitata. Dan ya fahimci a halin da take ciki. Tun bayan gama tantance halayensu ya gane uwar dabar tafi na'ibar tata dakewa idan suka aikata abu. Tuni Ruky ta fice abinta tanama Nimrah Addu'ar fitowa lafiya itama....

★★★

Received at 6:24 AM   A dai-dai wannan lokacin kamar yanda Ruky ta faɗa Faro ne ya iso gidan. Dan tunda aka ɗaura auren nan bai zoba aiki ya musu yawa a UNIT ZERO. Weekend yaso zuwa hakan bai samu ba. Shekaran jiya waccan kuma Biebah ta marairaice masa wai suna sunan baby. Yau ma ɗan lokacin da yaga yana da shi yace bari yay amfani da shi, saboda in har suka kama yaran nan bakwai da suke fako da Ojo baya jin za'a sake gane kansu kuma.

Sai da ya fara shigowa ya gaida Mammah cike da jin kunya. Ita ko kowa nata ne. Bata nuna tama gane ƙunshe-ƙunshen da yake ba ta ce, "Idonka kenan Haydar?".

"Mammah ayi haƙuri, ayyuka ne sukai yawa a office. Ranar naso shigowa na gaida su Gwaggo Habibah tace kun fita gidan Baffa".

"Shike nan na haƙura. Ya wajen tsoffin? Duk da Hajiya muna waya dan taso shigowa sunan nan tace ƙafa ta sata gaba".

“Wlhy ƙafa ke damunta. Amma ina shirin suje Egypt a dubata tunda nan ɗin sai cin kuɗi ake ba wani canji”.

“Ai asibitocin ƙasar nan sai addu'a. Na kuɗin ma dai gasu nan ne. Gara kuje can ɗin, ni bagashi na samu sauƙi ba sosai.”

“Haka Haysam ke gaya min, shiyyasa ma yace a kaita can itama”...

Sun ɗan taɓa hira kafin ya miƙe yana tsokanar Ruky data sakko daga sama tana gaishe sa. Dariya take da ɓoye fuska. Ya tambayeta Nimrah da Mu'azz.

“Yaya Mu'azz na school. Ninah kuma na sama ɗakin Dada”.

Faro yay dariya a zuciyarsa saboda maganar ƙarshe. A zahiri kam yace, “To ki gaida min su”.

Kanta ta ɗaga masa. Daga haka ya fice domin komawa falon baƙi yaga ta inda ginbiyar tasa zata ɓullo ita kuma. Dan tunda ya shigo ko mai kama da ita bai gani ba..........✍

To kuyita haƙuri da ni fa. Na kusa shiga satin hidima sai a hankali. Aurar da ɗa ba wasa ba□. ALLAH ne ke dafa min a typing ɗin nan ma da tuni na gudu muku tsabar yanda nake ba nutsuwa wlhy.□□
Received at 6:24 AM
3 people reacted
[4/5, 9:35 PM] +234 708 144 4204: KIƊA A RUWA 3

37

........“Zo nan”.

Dada yay maganar a dake yana tsare Nimrah da idanunsa dake rikita lissafinta. Kamar zatai kuka ta miƙe daga inda take zuwa gabansa. Hankalinsa ya maida kan abincin da Ruky ta kawo masa, tare da jeho mata tambaya kai tsaye.

“Mi kuka zuba musu a jiki?”.

Zabura ta ɗanyi tana ƙwalalo idanu waje ta ce, “Dada munga idi! Su waye kuma?”.

Yasan dama sai ta masa drama ɗin, dan haka ya sake haɗe fuska.

“Na duba cctv footage kenan?”.

“A'a dan ALLAH kayi haƙuri. Dada matsala aka samu, aljanun mu ne kawai suka hukunta shi?”.

Harga ALLAH baima san yayi kasare yana kallonta ba. Yanda ya tsareta da idanu itama kawai sai dariya ta kamata. Ta ce, “Dada da gaske fa nake”.

“Ni nace wani abu ne Kiddo?. Kawai dai dole na nemo malamai ai muku rukiyya ashe, yaushe kuke da aljanu ban sani ba?”.

“Dada basa cutarwa, a barsu kawai ba sai anyi rukiyyan ba.”

“ALLAH ya shirya min ku. Mi kuka saka musu?”.

“Dada dan ALLAH bazaka dake mu ba idan na faɗa?”.

“Ƙila”.

Sai kuma tsoro ya kamata, tab ɗin Dada ya dake su ai sun mutu. Ta tabbatar yanzu haka Ruky na can a tsure fiye da itama. Sake matsowa tai kusa da shi kamar wata mage, sai dai bata taɓa jikinsa ba amma ta lafe kusa da shi sosai. Cikin sake kwantar da murya da shagwaɓar data gama rikita lissafinsa sai dai ya dake ta ce,

“Dada kayi haƙuri bazamu ƙara ba. Kaga shi wannan mai kama da talo-talon shi ya jama macen mai kama da taɓaryar gwari. Dan shi muka hukunta. Ba yanda za'ai ya ɗauke ka a video mu barshi. Ai ko Yaya Mu'azz yay ma haka sai yaji a jikinsa balle ku iyayenmu, iyayen namu ma kai fa Dada. Ashe ma kun mana baki da zamu barshi.” yanda tai maganar ƙarshe tana tura bakin sosai ya kauda kai daga kallonta yana danne murmushin dake son bayyana a kan fuskarsa. A ransa yana ayyana (Indai Fitina ce a bar muku kayanku) shi sunayen ma data kira yaran sun fi bashi dariya. Amma dai baiyi ba. Itama bata jira ya sake tambaya ba ta ce,

“Karara muka saka masa”.

(Innalillahi wa-inna ilaihiraji'un ya faɗa a zuciyarsa. Shi soja ne yasan mi ake kira Karara. Dan su kansu wani lokacin suna amfani da shi musamman wajen ɗana tarko, idan kuma aiki yay aiki yakan taɓa jikinsu. Dan ko shi ya taɓa taɓashi tsabar azabar da yasha sai da ya kwanta asibiti. Yanzu dan ALLAH inama suka samu kararan?)

A zuciya duk yake maganar yana kallonta kawai. Ita kam sai cuɗa yatsun nata take na fama yanda ta saba. Ganin yanda take yi ya sashi basar da zancen, dan in ya tashi su biyun zai haɗa yay musu faɗa. Nimrah na jiran ya fara faɗa sai taji shiru. Sai ma gefensa ya nuna mata yana faɗin,

"Dawo nan".

Yay maganar yana nuna mata kusa da shi a saman kujerar. Sosai ta waro idanun waje. Alamar taya zata iya zama a kusa da shi ita kam. Sai dai kallon daya sake wullo mata ya sata ɗan laɓe baki irin na mai shirin kukan taɓara.

A karo na biyu yay mata gargaɗi da idanu. Dole ta shanye hawayen data fara ƙaƙalowa na ƙarya. Inda ya nuna matan ta zauna, sai dai a ɗofane. Amma sai ya kamata ya zaunar da ita da ƙyau har jikinta na gogar nasa. Zata fara mutsu-mutsu ya miƙo mata laptop ɗinsa jikin screen ɗin da wani hoto yana faɗin, "Kalla hoton nan da ƙyau ko zaki iya gane su waye?".

Computer ɗin ta amsa, ta ɗora a jikinta tana kallon mutanen jikin hoton daki-daki. "Lah Dada wannan kamar ni fa".

Dariya taso bashi, amma ya dake yana ɗan matsota jikinsa sosai yanda shima zaiga hoton da ƙyau, tsabar hankalinta ba wajen yake ba ta ƙara gyara zama sosai kusan jikin nata Duk a nashin. kallon yarinyar da take nuna masa yayi. Tabbas ita ɗin ce, tana sanye da boyal zani da riga, an masa ɗinkin buba da aikin wuta. Taci ɗammara da gyale tana hararar yaron kusa da ita. Yanda take farin ciki sosai ta saka shi murmushi yana kallon fuskarta. Hoton ta cigaba da kallo tana faɗin, "Dada dan ALLAH ina ka samo?".

Received at 6:24 AM

reacted Maimakon bata amsa sai ya ce, "Gama duba sauran ko zaki gane su".

Bata musa ba ta cigaba da kallo. Ga shi dai tabbas tasan fuskokin amma sunayen sun mata nisa. Sai da ƙyar ta dinga tsinto wasu tana faɗa masa. Tana faɗar yana rubutawa. Wanda bata gane ba kuma yana alamar jikin ainahin hoton dake cikin wani file. Ya sake nuna mata wani, nan kam harda iyayensu mata da maza. Dan harda Babanta. Fuskar Ummanta ta zubama ido. Hawaye suka shiga rige-rigen sakko mata. Shima ya jima yana kallon Umman tata, abubuwa da yawa na dawo masa. Kafin ya maida dubansa kanta.

"Ba kuka ake ba, addu'arki tafi buƙata a yanzu sama da komai. Zaki iya gaya min waɗan nan duk su waye?".

Kanta ta jinjina masa. Ya ciri tissue ya bata. Hawayen ta goge sannan ya fara nuna masa kowa da sunansa. Hakan ya sashi fahimtar tafi riƙe ƴan gidansu, dan waccan hoton yaran gidan kakanninta ne, inda aka haifa Ummanta. Koda tazo kan Kawu Tanimu sai ta sake fashe masa da kuka da faɗin, "Dada dan ALLAH wacece ni? Ina duk waɗan nan suke? Nasan duk na san su. Musamman Kawu Tanimu na".

( Alhamdullahi) Ya faɗa a zuciya. A zahiri kam cike da lallashi ya furta, "Karki damu zamuje inda suke idan lokaci yayi in sha ALLAHU. Wannan fa waye shi?". Ya nuna mata Babanta data tsallake batace komai a kansa ba. Idanu sosai ta zuba masa, sai kawai kanta ya shiga sarawar ciwo. Da sauri ta dafe shi tana faɗin, "Wayyo Dada kai na". Har tana neman sakar masa laptop ɗin ƙasa. Da sauri ya tareta ta kwanto jikinsa gaba ɗaya. Itama laptop ɗin ya riƙe. Saman table ɗin gabansu ya ajiye, ita kuma ya rungumeta sosai dan jikinta rawa yake. Abun kamar wasa sai ga Nimrah na neman rikice masa, sai da ya riƙe mata kai yana mata addu'a. A hankali ta fara sauke numfashi da ajiyar zuciya a jajjere, sai barci. Yanda take barci kanannaɗe a jikinsa ya sashi zuba mata idanu. Abubuwa zuciyarsa keta tuna masa a kanta, ciki harda tuna ranar farko da suka haɗu da Mamanta ɗauke da tsohon cikinta. UBANGIJI mai rahama da jinƙai. Mai tsara al'amura a yanda yaso. A lokacin inda za'ace masa abinda ke a wannan cikin abinda zai mallaka ne matsayin matar aure sai yace mai faɗar baida

hankali ma. Amma shi UBANGIJI ikonsa mai girma ne. Ya ja numfashi ya fesar, tare da lumshe idanunsa a hankali.

Kiran sallar magrib ya sashi miƙewa ɗauke da ita ya shinfiɗar a saman gadonsa. Fuskarsa da guntun murmurshi ya kai hannu ya shafa fuskar ta, kafin ya gyara mata hulan kanta ya wuce bayi yin alwala......

//★//★//★//★//★//

Tun kafin ta iso falon ƙamshinta ya iso hancinsa. Turaren nan nata na rikita masa lissafi tun ba yanzu ba. Yana dakewa ne kawai kada ai abin kunya. Amma yau sai yake jin kamar ma bazai iya hakan ba. Biebah da bata san yanayi ba tai sallama a ƙofar falon. Koda ya amsa da bata iznin shiga kanta a ƙasa ta shigo.

In dai haƙuri ne da rashin son hayaniya shi shaida ne akan Biebah ɗinsa. Ta ɗakko halayya da yawa na Mammah. Rashin kamaninta da su Haysam baisa ya taɓa kawoma ransa ba mahaifinsu ɗaya ba. Sai a jiya da Haysam ɗin yay masa bayani da kansa. Ya kuma tabbatar masa mahaifin Biebah ɗin na nan a raye. Hasalima ya ƙara bunƙasa da dukiya, kuma bai ƙara samun haihuwa ba har yanzu. Wannan abu ya ɗaure kan sa sosai, dan shima ana faɗar sunan ya sanshi. Dan mutum ne daba ɓoyayye ba. Lallai akwai baban al'amari a tsakanin wannan ɗiya da mahaifinta, ga shi kuma wani ikon ALLAH tana bala'in kama da shi, ya tabbatar koshi yaga Biebah a yanzu ba asiri ba komi ke kansa sai zuciyarsa ta girgiza. Dan kamanin bana wasa bane ba fa....

“Yaya sannu da zuwa. Kayi haƙuri na saka jira”.

Furucin Biebah ya katse masa tunani. Ajiyar zuciya ya ɗan sauke da sakin murmurshi. “Ba komai, ai amarya bata laifi”.

Bata wani kawo komai a ranta ba tunda tasan dai bai wuce akan saka rana ba. Sai tai ɗan murmurshi kawai tana sunkuyar da kai. “Ina Baby na?”. Ta faɗa cikin son ture wancan zancen. Ɗiyarsa take kira Babynta. Wannan kuma yana cikin abinda ya saye zuciyarsa da shi sosai. Ya nisa kaɗan yana gyara zama. “Babyn ki na lafiya. Duk da yau kwana biyu banje na gansu ba nima.
Received at 6:24 AM
Aiki yamin yawa sosai. Amma koda nake fitowa ɗin nan munyi waya”.

Tai murmurshi tana jinjina masa kai. “Masha ALLAH. Ya jikin Hajiya?”.

“Alhamdulillah da sauƙi itama.”

Ruwan data zuba ta miƙa masa. Ya haɗa da hannun nata ya riƙe. Hakan ya sata daburcewa dan bai taɓa mata hakan ba koda da kwatance. Kallonsa ta ɗan yi ta janye idanunta dan haka yay murmurshi da faɗin, “Kowa kin tambayi ya yike amma ni banda ni. Anya akwai amana a wannan sabgar Biebalo.”

Kanta a sunkuye tana murmurshi ta ce, “Ai kai na ganka kana lafiya”.

“Tab sama-sama dai. Bakiga duk ma na rame ba”.

Ɗagowa tai ta kallesa fuskarta na nuna damuwa. Ta ce, “Miya same ka?”.

“Ƙaunar Biebalo da tsananin buƙatar ta a kusa dani mana”.

Ya faɗa kansa tsaye yana ja mata hanci. Wata muguwar kunya data rufeta bata ma san ta furta, “Kai Yaya na banu”.

Dariya yayi sosai. Dan yanda tai ɗin dole ta baka dariya. Sai da yasha ruwan ya ajiye kofin sannan ya gyara zamansa da faɗin. “Da gaske nake fa. Shiyyasa ma kikaga inata dojema zuwa gidan nan. Dan nasan bazan iya kauda idanu na ba.”

Ita dai yau gaba ɗaya yana neman rikitata da kalamansa. Abinci ta buƙaci zuba masa. Yace ta barshi sai yaje salla ya dawo magriba ta kusa. Ta jinjina kai tana miƙewa ta koma kujerar nesa da shi kaɗan kamar yanda ta saba. Bai hanata ba ya cigaba da janta da hira har aka kira sallar magriba sannan ya miƙe ya shiga bayin cikin falon ɗaura alwala...........✍
Received at 6:24 AM
3 people reacted
[4/5, 9:35 PM] +234 708 144 4204: KIƊA A RUWA 3

........Dada ya fito Faro ya fito suka haɗu a compound. Cike da shaƙiyanci Faro ya furta, “Alhajin ALLAH ai nazata ma sallar a ciki zakayi yau?”.

Cikin rashin fahimta Dada ya harareshi. Faro yay dariya da faɗin, “Miye na hararata daga faɗar gaskiya. Na shiga ciki akace zuciyarka na ɗakinka tare da kai. Amma bawan ALLAH ko kunyar Mammah baka ji ne?”.

Yanzu kam Dada ya gane sarai. Dan haka ya girgiza kansa da faɗin, “Bani da lokacin ka. Ka cigaba ina da maganinka a hannu Haydar”.

“A'a tsaya mi kake nufi?”.

Gaba Dada yay abinsa batare daya sake tanka masa ba...

Bayan an idar da salla sun fito Faro kema Dada bayanin yaran nan duk sun zo hannu fa. Sannan ya fara aiki akan Garba.

Dada ya jinjina kansa yana ɗan furzar da iska. “In dai Garba ya faɗa tarkonmu Ojo ya gama zuwa hannu Haydar. Yanzu damuwata musan ta yanda zasu rarraba kayan nan da yaran suka ce”.

“Nima hakan na damuna sosai. Amma akwai wani jami'in farin kaya na yarda da aikinsa gaskiya. Ko zamu shigo da shi tawagar nan ne?”.

“Hakan ba laifi bane in dai ka yarda da shi.”

“A, na yarda da shi gaskiya sosai. Amma in kana da lokaci yau da sai yazo ku haɗu”.

“In dai ka yarda da shi basai na ganshi ba. Dan satin nan zan yi busy da yawa. Bana jin ma zan shigo UNIT ZERO gaskiya.”

“Yaran nan fa? Ya kamata dai ka shigo”.

“Ku cigaba da kula da su. Amma kar ku haɗasu da waɗan can tunda su an fara treating ɗin su. Driver nan ma Bilal nake so ya dawo dan yayi tafiya”.

“Ba Ammar na nan ba?”.

“No, Ammar baya ji, zai iya ƙwaɓa aikin. Karka damu Bilal ɗin ya kusa dawowa”.

“Na gane. ALLAH ya dawo da shi lafiya ya bamu sa'a”....

Isowar Nabeeha wajen ya saka Dada yay shiru. Faro da bai san dawan garin ba ya fara tsokanarta da kalmar, “Uwargida sarautar mata”..

“Hummm!”.

Kawai tace masa. A take ya fahimci ya ɗebo da girma. Sai kawai yayma Dada sallama ya wuce masaukinsa. Nabeeha bata gaida shi ba, dan haka bai sake bi takanta ba. Sai da ya wuce Dada da yaƙi kallonta da alamar ɗaci a muryarsa ya ce, “Ke baki iya gaisuwa wa mutane ba ko?”.

Duk da yanda take son dinga danne yanayinta sai da ta ɓata fuska, muryarta na fita da takaici ta ce, “Miyasa zai kirani da wani Uwargida”.

Idanu ya zuba mata a karo na farko. Abu biyu ya saukar mata a lokaci ɗaya. Tsigar jikinta ta tashi, sannan wani shakkarsa ta tsarga mata. Ta sani shi baya son raini, ba'a kansa kawai ba. Ko ga wani kayi, wanin daya tabbatar ya girmeka sai ya nuna maka ɓacin rai. Sai dai idan wancan ɗin ya zubar da nasa girman ne...

“Kayi haƙuri ina son muyi magana ne”.

Nabeeha ta faɗa muryarta na rawa. Tamkar Dada bai jita ba, yay ƙoƙarin barin wajen. Da sassarfa ta tari gabansa, cikin danne shakkarsa dake son rinjayarta da aro jarumtar dole kawai ta rungumesa ta sakar masa kuka.

Kasa motsawa Dada yayi, sai dai yabi compound ɗin da kallo dan son tabbatar da babu mai ganinsu. Ita ko wani bugawa ƙirjinta yayi, saboda jin ƙamshin turaren da tunda ta dawo take jinsa a jikin Nimrah da Ruƙayya. Tabbas turaren SHUWA INCENSE AND MORE +234 704 229 3387. Duniya ne. Suna da turare wuta da khumra kaloli har uku: black humra, white humra, brown humra. Akwai oil perfume da kullacham da genine da Turare kabasa kaloli uku shima. white, black, and brown. Akwai man kitso, da kayan gyaran jiki masu gyara fata da sanyata laushi da santsi kiyita glowing

abinki hajjaju. Tsagaitawa tai da kukan nata, ta ƙara zuƙar numfashi da ƙyau. Jin tabbacin ƙamshin ne fa ya sata saurin jan jikinta baya. Ya bita da kallo, itama nata idanun ta ɗago tana kallonsa, zuciyarta na tafasa a cikin ƙirjinta. Tana da kishi mai zafi, kuma ko yaya ya taso mata bata iya haɗiyewa.

Tsaf ya karance wutar bala'in da ke ci a cikin idannunta. Sai dai bai san akan miye ba. Bai kuma yi magana ba har sai da ta buɗe nata bakin ita tayi.

Received at 6:24 AM "Saboda kana samun biyan buƙatar ka a wajen tatsitsiyar yarinyar da ka haifi wadda ta fita ma kake wulaƙantani Haysam. Ka kasa sauke nawa hakkin amma ita kana tare da ita ko kunyar ƙannenka baka ji? Kaƙi taka inda nake duk da halaccin da nai maka na jiranka tsahon shekarun da bani da tabbas na dawowarka. Kana zaton bazan iya barinka ba saboda ina sonka ko?......"

Kuka ya sarƙeta ta kasa ci-gaba da magana. Sai jiri da take ji kamar zata faɗi. Kanta ta dafe, da jan ƙafa tabar wajen ganin yaƙi yay magana. Wani irin zafin tsanarsa take ji a ranta. Tana son mijinta, tana masa kishi mai tsananin gaske da ita kanta har tsoron kanta take ji. ALLAH wani lokacin har ji take kamar garama ace ya mutu idan ta tuna yarinyar nan matarsa ce...

Koda ta wuce Dada ya kai mintuna biyu a wajen kafin ya wuce ciki dan kalamanta sun masa zafi. Bai samu kowa a falon ba sai su Afrah. Hankalinsu kuma na kallon cartoon har ya wuce basu ganshi ba.

Da sauri Nimrah dake daga balcony ɗin upstairs tana kallonsu tabar wajen, hawaye share-share a fuskarta. Wani ɗan lungu ta samu ta maƙale, har sai da ta ga shigarsa ɗakinsa ta fito ta sauka downstairs. Itama bata kula su Abees ba ta shige ɗakinsu. Ruƙayya dake zaune a tsorace ta tashi zaram tayo kanta tana tambayarta dukanta Dadan yayi? Maimakon amsa sai kawai ta rungumeta ta fashe da kukan.

Ruky tai matuƙar daburcewa, itama tata muryar na rawa alamar zatai kukan ta ce, "Dan ALLAH ki daina kuka Ninah, ki faɗa min miya miki?".

Yanzu ma bata iya bama Ruky amsa ba, sai da ta tabbatar kukan ya saka zuciyarta rage nauyi sannan ta sanar mata abinda ta gani tsakanin Dada da Nabeeha. Ruƙayya ta dalla mata harara. "Shine kuma abin kuka kamar wata sakarai. Ninah wai miyasa akan matar nan kike son zama wata lusara ne?".

"To ni ya kike so nayi? Kawai fa kaina ya kama ciwo ya barni a ɗaki barci ya ɗauke ni sai yanzu na farka. Na leƙa ta window ɗin ɗakinsa na hangota ta fito a sashen ta, shine na fita balcony ashe shine tsaye tare da Uncle Haydar......"

"Kema gashi kin faɗa ita ta kawo kanta. Ninah itafa matarsa ce. Banda ma sun sami matsala daba wannan maganar ake ba. Ni ba wannan kishin irin nata nake so kiyi ba, kishi irin na kwatar ƴanci zamuyi. Dan haka al'amarinsa da matarsa yama daina damunki. Mu zauna mu tsara abinda ya dace kin fahimta".

Kai ta jinjina mata, itama sai ta rungumeta tana faɗin, "Uhmmm my Trouble Queen na tsoron kishiya. Wlhy kin fara son Dada".

Karamin dundu Nimrah tai mata a baya. Ruky ta sanya dariya.....

(+++)+(++++)+(+++)

Anan kam Biebah na zubama Faro abinci shi ko ya zuba mata idanu. Komai tayi ƙyau take masa. Ji yake a ransa anya zai iya dannewa kuwa. Shifa sai yanzu ma yake ji kamar Haysam bai kyauta masa da batun a ɓoye auren nan ba. Koba komai inda ta sani ai ya ɗan rage zafi. Amma yanzu komai yayi zata iya kallonsa a baibai ne. Haka dai dole ya shanye maitarsa yaci abincin.

Yana kammalawa kaɗan suka ƙara taɓa hirar ya miƙe akan zai wuce. Tayi mamaki, dan kafin yazo yace mata sai irin tara ɗin nan zai tafi. Dan haka ta kallesa cikin damuwa da ƴar shagwaɓa ta masoya. "Yaya amma cakai bazaka tafi da wuri ba. Miyasa ka canja kuma?".

Gaba ɗaya sai lissafinsa ya nema ƙwacewa da salon nasa. Ya haɗiye busashen yawu, tare da runtse idanunsa da launinsu ya canja. Tsawon sakanni kafin ya buɗe ya

ɗan tako kusa da ita gab har sai da ta motsa zata ja baya saboda kusancin nasu. Yay wuf ya taro ƙugunta. Ta waro idanunta sosai, sai kuma lips ɗinta ya kama rawa tana son yin magana.

Yatsarsa ya saka a lips ɗin nata yana sake kusanta fuskarsu gab da juna. Hakan ya sake daskarar da jinin Biebah data shiga tsilla-tsilla. Shi ko ko'a jikinsa. Saima nasa idanun da suka rine sosai ya riƙe natan da shi. Miryarsa na wani kalar komawa ƙasan maƙoshi ya furta. "Idan kika hanani tafiya zan aikata ba dai-dai ba. Dan wannan sojan naki bai san ya taɓa ya bari ba".

Received at 6:24 AM Yana kai ƙarshen zancen ya wani irin janta ya saka a jikinsa gaba ɗaya yay ma bayanta zobe da hannayensa. Idan Biebah bata suma ba a wannan lokacin to ina tabbatar muku numfashinta ya tafi yawon duniya na wucin gadi. Dan numfashinta bai dawo da ƙarfinsa ba sai da ya sumbaci idanunta, tai wata zaburar da ya saka shi sakin dariya. A rikice ta kwace jikinta kawai ta nufi hanyar fita. Yana kiranta amma ko waiwaye.

Ya ƙara ƙarfin dariyarsa yana cizar lips. Dan harga ALLAH dariyar ta bashi. Ga wani shauƙi dake ɗawainiya da shi. Ai dolensa yay nisa da Biebah har tarewar nan. In ba hakaba ya rantse sai ya aikata ba daidai ba. Dama a yanayin mai son yin kuka an jefe shi da kashin awaki yake a halin yanzu.........✍

[4/5, 9:36 PM] +234 708 144 4204: KIƊA A RUWA 3

39

.........Tun daga wannan ranar tsakanin Nimrah da Dada aka koma ƴar wasan ɓuya. Dan tun randa ta baro ɗakin nan nasa aka koma ƴar nesa-nesa, ba komai yasa haka ba sai haushin wannan runguma da Nabeeha tai masa. Sanda yake fita basu tashi ba. Yakan dawo daga office late, da taji motsinsa sai tayi yanda tai ta bar falo in har suna zaune anan. Sai kace wadda ta ma haddace lokacin dawowar tasa. Mammah na lure da su. Sai dai bata taɓa nuna ta fahimta ba balle tai magana.

Shi kuma Ammar ya dage yana jan Ruky a jiki, kamar sakata aiki da wasu abubuwan. Amma baya yarda su keɓe dan zuciyarsa na raya masa abubuwa, ya kuma tabbatar idan ba ƴar nesa-nesa ɗin nan ba za'ai abin kunya. Ita kuma a hankali yanayin nasu ke mata tasiri, duk da tana shiga kunya musamman idan yayi wani abin da a can baya baya musu shi, yanzun ma bayama Nimrah sai ita. Shi kam Bilal yayi ƴar tafiya ne tun monday ɗin bayan ɗaurin auren, sai ta waya yake shoshalewarsa da Asma'un sa, har yanzu ba'a gamu fuska da fuska ba tunda aka ɗaura. Faro ma tun zuwan da yay ya rufama kansa asiri. Sai aka koma ƴar waya kawai da bada uzirin aiki-aiki. Duk da itama ta masa yajin kwana biyu saboda kunyar abinda ya faru.

Yayinda angwaye keta dauriya anan iyayen biki ne keta shirinsu. Wato su Aunty Ummi da su Shariffa. Suma su Ja'afar cikin satin nan zasu bar ƙasar kawo kaya, daga nan zasu zo da komai na amare in sha ALLAHU. Mammah nata addu'a a garesu, sai in suna neman shawara suzo ta basu, sai dai ita ta maida hankali sosai akan su Nimrah musamman akan abubuwa masu muhimmanci da ya kamata iyaye da kansu su nunama ƴaƴansu game da rayuwar aure ba ko jira ƙawa ta gayama ƴarki ba ko wata. Abun na basu kunya, amma yanda take haɗe fuska ke sakawa su nutsu. Sun fara class ɗin su na Chef Yakudima 08135358038 kullum da safe, da yamma kuma su wuce islamiyya. Mai lassing ma na zuwa, dan sati mai zuwa zasu fara exams ɗin su.

Su Hanoon dai ba ƙaramin kama kansu sukai a gidan ba yanzu. Dan tunda suka sha jiyyarsu suka tashi kwana biyu sai suka fahimci koma minene su Nimrah ne sukai musu shi. Sun gane hakan kuwa ta dalilin video ɗin da suka ɗauka. Yanzu basu da aiki sai zaman kallonsa suna dariya. Kuma basa yi a gaban Mammah. Kai ko Biebah da su Lailah ma, ita kanta mai wayar bata san ina suka saka video ɗin ba dan sun ɓoye shi. Hakan da sukai ya kawo masalaha sosai, musamman da batun jarabawar su da class ɗin Chef Yakudima 08135358038 ya sake kwashe rabin lokacin su Nimrah ɗin ma.

★★★★

Yau ta kasance juma'a ne. Rana ce da Nimrah take cika shekara sha bakwai. Da yake ba wani biki suke ba ko'a jikinta. Hasali ma tama manta da wani cikar shekararta. Yau mai lassing bata zo ba, dan haka suka sha barcinsu. Monday in sha ALLAHU zasu fara exams ɗinsu kuma.

Birthday cake na bazata mai ƙyau Ruky ta shirya ma Nimrah. Dan haka ta gudu sashen su Lailah acan tayi shi. Sai da zasuyi sallar magriba Nimrah tace zatai wanka tana jin zafi Ruky ta saka su Kulu suka tayata shirya komai a falo. Dama tayi hakan ne saboda dawowar Uncle's ɗinsu. Dan sai Lahadi su Uncle Ja'afar zasu wuce suma. Abin kamar wasa sai gashi ɗan kwalliyar ɗin da sukayi yayi ƙyau sosai. Su Afrah sai murna suke dan basu taɓa gani anyi a gidansu ba. Wannan ma Ruky sai da taita lallaɓa Mammah ta yarda, kuma badan komai tayi ba sai neman magana. Babu wanda ya sani ta aiki Abees da Aheel sashen Nabeeha wai ya faɗa musu 8:30 Mammah na kiransu..

Koda su Abees suka je sashen Nabeeha banda kallon tsana babu abinda yaran suka samu. Haka kawai take jin baƙin cikin yaran. Yanda bata shiga harkar iyayensu suma ba shiga tata suke ba. Dan tunda ta dawo gidan ko barka bataje ta musu ba. Hakan yasa suma suka nuna bama su san da ita ba a gidan. Dada dai uba suke kallonsa, kuma girmansa na musamman ne a garesu. Ita kuma tunda ta kasa riƙe nata girman sai taji da matsalarta can. Dama kuma mazansu sun musu gargaɗi akanta, hakan ma ya ƙara basu lasisin riƙe kansu.

Received at 6:25 AM Ismat ce ta amsa yaran, suko dama ba wajen zuwansu bane, suna gama faɗa suka baro sashen batare da sun damu da abinda akai musu ba abinka da yara. Sai da akai sallar isha'i kowa ya shigo sannan sukaga mi Rukyn tayi. Ma'aruff ya riƙe baki da faɗin, “Yaushe aka fara bikin birthday a gidan nan bamu sani ba?”.

Kunne Ruky ta kama tana shagwaɓe fuska da faɗin, “Uncle Ninah kawai namawa, kuma ALLAH na roƙa Mammah”.

Gefe Ammar yay da kansa yana runtse idanunsa. Dan yanda tayi sai da yaji kamar ya kamata ya rungume bakin shagwaɓar ya... Uncle Ma'aruff ya girgiza kansa kawai da faɗin, “Shike nan sai a yanka mana cake muci to”.

Daɗi ya kama Ruky jin basu yi faɗa ba. Tasan kuma da Uncle Ma'aruff yayi Uncle Ja'afar ma zai yi. Ana haka su Shariffa ma suka shigo. Ruky nata kallon hanya amma babu Dada babu su Nabeeha. Ba haka taso ba, dan haka ta kama leƙe-leƙe. Mu'azz abokin daba tsaf ya harbo jirginta, dan haka ya matso yana mata magana ƙasa-ƙasa.

“Uwar mi kike shiryawa?”.

Harararsa tayi da masa nunin yay shiru. Kafin ta sake rage murya ta sanar masa. Sai yay murmurshi da faɗin, “Shine zaki shirya wannan plan ɗin ba gayyata? Ai dole dani za'ai wannan sabgar. Jeki ki fito da Ninah zan ƙarasa sauran.”

Tasan Yaya Mu'azz zai yi, dan haka cikin farin ciki ta wuce. Ja'afar ya kalla Ma'aruff dake wasa da Naseer daya amsa hannun Shariffa. “Twiny mi yaran nan suke shiryawa ne?”.

Kallonsa Ma'aruff yay da tambayar “Kamar ya?”.

“Bakaga Mu'azz da Ruky na ƙus-ƙus ba. Sannan Ninah bata a falon”.

Fuskarsa da murmurshi ya ce, “Bari mugani dai to. Ni kaina na fara fahimtar wani rashin jin zasuyi......”

Maganar tasa ta tsaya saboda shigowar Dada falon riƙe da hannun Mu'azz. Dai-dai nan kuma Ruky ke fitowa da Nimrah idanu a rufe. Tsayawa Dada yay yana kallonsu. Hakama su Biebah duk sun maida hankalinsu kansu. Sai ga su Ismat sun shigo. Nabeeha sai cika take tana batsewa dan da ƙyar Ismat da Amima suka sakata ta taho. Rayhana kuwa da manufa ta biyosu jin ance Mammah ke kiran, tasan koba komai za taga Dada da ganinsa ke musu wuya yanzu a gidan fiye da kowa.

Suma tsaye sukai cirko-cirko, sai da Ruky ta kawo Nimrah tsakiyar falon kawai Mu'azz ya dawo kusa dasu ya fara mata waƙar birthday. Su Ayyan kuwa suka hau

tayashi suna tsalle. Shi Dada ma abin nasu girmar kansa yayi, dan haka ya gagara magana. Sai ma zaune da ya kai kusa da Mammah dake cema su Nabeeha su ƙaraso mana suka tsaya. Dan ita bata san miya kawosu ba. Tunda bata san Ruky ta zabga mata ƙarya ba.

Ismat dake jin kamar taje ta rungume Ja'afar ta ja hannun Nabeeha dake shirin ja baya. Ganin haka itama Amima ta tare ta, dole badan taso ba suka ƙarasa ɗin. Lokacin Ruky ta buɗe fuskar Nimrah da mamaki ya kamata tana bin komai da kowa na falon da kallo. Sai kuma ta tsaida idannunta dake cika da ƙwalla akan Ruky, tare da rungumeta. Yanda tayi ɗin ya bama kowa dariya banda su Nabeeha. Dan alamu sun nuna itama bata san an shirya abin ba. Dada ma kamar baya falon yama maida hankalinsa kan Khadijah da ya saka Ammar ya kawo masa. Yana son yara sosai, yau kuma su Abees ba tashi suke ba uwarsu na shagali.

Nabeeha tana son tace ma Mammah gata tana tsoron Dada, dole ta dake tana jiran Mammah ɗin ta fara magana da kanta. Amma wani irin tafasa zuciyarta keyi da kallon su Nimrah dan haka ta ɗauke kai, wani sashi na zuciyar tata kuma najin daɗin ganin yanda Dada ko kallonsu bayi yake ba shima...

Oho su masu birthday bama su san tanayi ba. Dan Kulu na kawo cake su Ma'aruff da su Lailah suka biye su Nimrah suma. A take suka je aka zagayeta akace ta yanka. Ita ta riƙe wuƙar Ruky ta ɗora hannunta kan nata da su Afrah gaba ɗayansu. Suka ko yanka cake suna farin cikinsu. Ga video Mu'azz na musu da hotuna. Sai lokacin su Hanoon dake ɗaki suka fito dan hayaniyar ta ishesu. Hanoon na ganin Dada a falo zaune yau Available taji farin ciki ya kamata. Shi ko Afeef tsaki yay ciki-ciki ya koma. Dayyan dama barci yake ko sallar magrib da isha'i bayi yay ba.

Received at 6:25 AMReaction An yanka cake Nimrah ta cira ta nufi Mammah. Sai da ta durƙusa gabanta cike da so da ƙauna tana ruƙunƙumeta ta kai cake ɗin bakinta. Su Ammar suka saka dariya wai ko zata koma ciki ne irin wannan kanainaye Mammah haka. Dariya aka sanya, Mammah taci cake tana taya su. Saura data gutsira ɗin ta amsa itama ta bama Nimrah tare da shafa mata kai. “ALLAH ya ƙaro shekaru masu albarka Auta. Yasa daga yau kun ƙara hankali ke da Ruƙayya.”

Sosai su Biebah ke dariya. Dada kansa sai da yay wani gajeren murmurshi da furucin Mammah ɗin. Amma yanda basu yake kallo ba sai ka rantse hankalinsa baya wajen. Nan ko sarai kallesu yake ta gefen ido. Musamman yanda Nimrah ta rungume Mammah sai da yaji wani sanyi da nutsuwa ta musamman na ratsa jikinsa. Yana son Mammah, yana kuma son wanda ke sonta.

Nimrah ta sake ɗibar cake zata bama sauran Mu'azz da Ruky suka kalla juna. Dan anzo inda suke so ɗin. Aiko sai kawai Ruky ta kama hannun nata ta jata har gaban Dada. Nimrah ta waro idanu waje, Ruky ta harareta. Hakan kuma yayi dai-dai da ɗagowar Dadan ya kallesu jin suna tsaya masa a kai........✍

[4/5, 9:36 PM] +234 708 144 4204: KIƊA A RUWA 3

40

.........“Yaran nan sun iya haɗa bomb”. Ma'aruff ya faɗa ƙasa-ƙasa yana ƙunshe dariya. Ja'afar ya bashi amsa da, “Dama sunan uwar daba ɗin kenan ai. Yau Dada ya shiga one chance. Bari muga zai amshi cake ɗin kuwa.”

“Idan bai amsa ba ɗura zamuyi masa. Dan dole shegiyar matar can ta fita a falon nan da takaici, ta kuma tabbatar Ninah ɗinmu ce a sama”. Da ƙyar Ja'afar ya gimtse dariya...

Anan kam koda Dada ya ɗago sai idanunsa a cikin na Nimrah dake fiki-fiki da nata tana kallonsa. Dai-dai Ruky ta bata mintsini tana ɗan sake turata gaban nashi. Juyowa tai zata harareta idonta ya sauka akan Nabeeha dake kallonsu da wani masifaffen yanayin ɓacin rai fuskarta kamar zata yo aman wuta. ALLAH sarki Mammah tsamm ta miƙe abinta tabar musu falon ma. Dan ta tabbatar idan tana nan Dada bazai amshi cake ɗin nan ba. Kuma koba komai ita kanta sai taji tana son

Nabeeha ta fahimci irin Nimrah suke buƙata a rayuwar Muhammad, idan kuma ta kasa canja kanta tana ji tana gani Nimrah zata ƙwace komai da take ganin ita itace ta isa.

Nimrah dama harda nauyin Mammah take ji, tana ganin ta wuce tai gajeren murmushi. Sai kuma ta kalla su Ja'afar da su Lailah. Amma tsabar shaƙiyancin iyayen nasu a tare sukai mata alamar tayi harda jinjina. To dama ba'ace tayin ba tayi bare ma an bata lasisi. Cike da jin ƙwarin gwiwa kuwa ta ƙarasa takawa gaban Dada daya ɗauke kansa tun ɗazun. Kneeling tayi a gabansa ta ɗan kallesa, suna haɗa ido ta janye nata da sauri tare da wayancewa ta lakatama Khadijah dake a hannunsa cake ɗin kamar dama ita tazo yima hakan.

Dada dake kallonta a ransa yace (Kam yarinyar nan ni zata yarfa?) sai kawai a bazata jitai an kamo hannunta dake riƙe da cake ɗin. Idanunta ta ɗago da sauri. Ganin tabbacin Dada ɗin ne kuwa sai ta waro su waje. Shi ko ya fuske cike da nutsuwarsa da kamewa ya kai hannun nata kusa da bakinsa idanunsa a cikin nata ya riƙesu suna kallon juna cikin ido ya gutsira cake ɗin. Yana dai riƙe da hannun nata ya sake maida shi saitin nata bakin ya wani ɗan ɗage gira alamar itama ta ci. Kamar sokuwa haka Nimrah ta buɗe baki ta gutsira saitin inda ya gutsira ɗin. Sannan ya saka ɗayan hannunsa ya kwashe wanda ta sakama Khadijah a kumatu ya mayar kan hancinta batare da kowa ya ji abinda ya faɗa ba ya motsa lips kaɗan ya furta, “ALLAH yasa nan da wata shekarar kin zama Mummy”.

Da sauri Nimrah ta waro idanu tana wawwaugawa inda kowa yake. Tare da fatan ALLAH yasa babu wanda yaji miya faɗa. Basu ji ɗin ba, amma yanda tayi duk sai suka tsargu.

“Awwwwwww!!”.

Ja'afar da Ma'aruff suka faɗa cike da shaƙiyanci. Kunya ta kama Nimrah sai kawai ta duƙe kanta a cinyarsa batare data farga ma da abinda tayin ba. Shi kuma kawai ya shafa kanta yana sakin wani ƙayataccen murmushin da ya bama kowa mamaki a wajen. Dan Mammah suka fi ganin yanama irin wannan murmushin mai sanyi, da armashi dake bayyana cikakken shauƙin farin cikinsa.

Ja'afar da Ma'aruff suka tafa. Ma'aruff ya ce, “Oh-oh proud of you Daughter kin ciwo mana kofi”.

Harara Dada ya wulla masa, sai kuma ya kauda kai yana ƙoƙarin haɗiye murmurshin dake neman suɓuce masa. Su Lailah da Shariffa kuwa aka duƙar dakai ana ƙunshe dariya. Ammar, Mu'azz Biebah kuwa hannu suka sa suna rufe fuska suma su a dole sunji kunya. Halin da Nabeeha take ciki ba'a magana, gefe ga Rayhana da Hanoon zukata kamar zasu fashe. Ismat da Amima ƴar uwarsu suke tayawa kishi.

Da ƙyar aka samu Ninrah ta ɗago a jikin Dada. Shima sai ya miƙe batare da yace musu komai ba ya saka mata Khadijah a jiki ya wuce sama. Kamar jira suke dama ya bar falon. Su Ammar suka zagayeta suna liƙa mata kuɗi. Ruky kuwa da Biebah suka rungumeta ransu fal farin ciki. Ma'aruff da Ja'afar suka sake kunna al'amarin suka hau mata liƙin suma. Ihun su Afrah da dariyar su Lailah da su Mu'azz ya ƙara kunna wutar baƙin ciki a zuciyar Nabeeha. Kawai taji kamar ta fashe da kuka. Hanoon kuwa da gudu ta bar falon itama nata kukan na tahowa. Rayhana da jikinta ke rawa ji take kamar taje ta shaƙe Nimrah.

Received at 6:25 AMDan yau ko makaho ya san abinda Dadan yayi a bayyane yake yana son yarinyar. Nabeeha ta yinƙura zata miƙe dan ta gama cin alwashin wlhy yau ko ita ko Nimrah sai dai wani ya mutu Amima da Ismat suka rirriƙeta. Duk da itama Ismat ɗin nata kishin akan Shariffa na cimata zuciya. Sai dai bata son suyi wani abinda ɗan sauran mutuncinsu zai ƙarasa ɓarewa. Amma tabbas yau ta sake tabbatar da akwai aiki ja a gaban ƴar uwarta. Dan wlhy babu shakka ƴan uwan Dada da yarinyar nan zasuyi amfani wajen ɗaukar fansar duk abinda Nabeeha tai musu a baya. Ko wanda bai san mike faruwa ba yaga abinda suke mata a yanzu yasan da biyu ne...

Oho suke lissafinsu, su ko su Ruky shagalinsu suke. Dan sun ma koma cin cake batare da sun nuna sun tuna su Nabeehar na a falon ba ma. Dan haka suma suka tashi suka fice zukatansu kamar zasu kama da wuta....

∆×××∆×××∆×××∆

Washe gari a bazata Dada ya gwangwaje Ruky da Nimrah da wayoyin iPhone sabbi dal a kwali ƴan yayi. Sai kuma ga su Ja'afar da laptop guda biyu suma da dama sukai musu alƙawari tun kwanaki. Wayyo zo kaga farin ciki da murna kamar zasu fasa gidan. Da ƙyar suka bar kunnen mutane ya huta.

A ranar da dare su Ja'afar suka wuce. Suda ƙasar su kuma sai satin biki idan ALLAH ya kaimu. Washe gari shima Bilal ya dawo. Sosai su Nimrah ke murnar dawowar sa. Dan kaf kawunan nan nasu babu mai taya su akan shiriritarsu irinsa. Hutun kwana biyu zai yi kafin komawa aiki. Da wannan hutun nasa Dada yay amfani ya turashi ƙauyen su Malam Ari tsohon driver. Batare daya sani ba kuma su Dabo suka bi bayansa suka samu address ɗin.
Washe gari ya shirya zuwa ganin tashi ginbiyar, su Nimrah suka maƙale masa dole yaje da su. Shi dai ya daure ba kamar su Ammar ba. Dan sunyi hirarsu kamar yadda suka saba ko taɓa Asma'u baiyi ba. Su Ruky ma nata musu kai-kawo ina ya samu wannan damar. Da zai dawo ya tarkatosu suka taho harda Lolo zai ƙarasa weekend ɗinsa...

★★

Aiki ya matuƙar yima su Dada yawa. A yanzu ko lokacin shirmen gidan baida shi. Ga office ga aikin bayan fage. Su Dabo sun sami nasarar ƙwamuso masa Malam Ari. Sannan sun kwashe iyalansa dan sun fahimci akwai matsala. Waje na musamman Dada yasa suka ajiyeshi. Acewarsa sai bayan biki zai fuskance shi. Dan abu nata matsowa ga Office ma ya ɗauki zafi sosai.
Ranar wata Laraba kawai a bazata aka kai wasu mugayen hare-jare a gabashin ƙasar data tada hankalin kowa musamman jami'an tsaro. Nan fa aka shiga sukar ministan tsaro da NSA. Shi kansa Dada hankalinsa ya tashi. Amma ya hana Imran yin magana da manema labarai dan ya fahimci harin tsokana ne. Wasa farin girki ai sai abu ya ƙara tsamari. Satar shanu, kidnapping mutane da zuwa a tada ƙauye babu gaira babu dalili. Abu ya kai har bomb ya tashi sau biyu a tasha da kasuwa.
Dole tako wane fanni Imran ya shirya ninka tsaron jami'ai. A bayan fage Dada na aiki da su Faro. Shugaban ƙasa duk da ya fahimci shirin babba ne yanata ƙarfafa kansa da ƙarfafa su Dada. Ga ƴan jam'iyya da masu muƙamai sun masa caaa wai sai a canja Imran akan harkar tsaro dan babu abinda zai iya. Shi kuma ya muna musu ai dama Imran bai ce zai iya komai ba ALLAH shine maiyi. Dan haka suje suyi addu'a. Sannan suma aikin nasu ne bana Imran shi kaɗai ba. Wannan magana ta musu zafi, suka ƙara ƙullatarsa da komawa gefe suna masa zagon ƙasa har wasu na iƙirarin son barin jam'iyyar. Shi ko ya toshe kunensa yayi kamar bai san sunayi ba......

★★

A ɓangaren su Nimrah ma sun fara exams. Dan haka shiriritarsu ta rage a gidan. Yayinda su Aunty Mommy keta shirin hidimar biki dake ta matsowa. Duk da halin da ƙasar ke ciki da yanda su Dada sam basu da lokacin kansu na tayar musu da hankali kamar kowa. To amma ya za'ayi, dama ai ana bikin duniya ake na kiyama. Dan haka hatta gyaran jiki su Lailah da Aunty Mimi sun fara yima amare. Asma'u da Biebah na gidan Aunty Mimi. Nan kuma su Shariffa da Lailah suke kan su Ruƙayya. Aunty Mommy da Aunty Ummi suna nasu shirye-shiryen. Hakama Ummu matar Uncle Nasiru.

Received at Su Nimrah amare kuwa daga exam sai islamiyya da class ɗin Chef Yakudima 08135358038. Duk wani aiki na gidan an sauke musu shi. Ɗakin Dada ne dole Nimrah take gyarawa sai dai ba kullum ba. Dan yanzu ma yakan haɗa sati bai kwana a gida ba yana UNIT ZERO..........✍

Received at 6:25 AM
[4/8, 7:30 PM] null: 41

.........A ɓangaren yꞌan Kungiyar Duhu gadai nasarar kai hare-hare da tada hankalin al'umma sun samu amma sun kasa jin farin ciki da gamsuwa saboda yanda su Dada suka matsa musu. Sai kama musu yara masu musu aiki akeyi. Tun abin baya damunsu har ya fara ɗaga musu hankali. Ranar suka kira Dagger babban yaronsu dake da mafi rinjaye yara suka masa tas. Da nuna masa idan fa ya fara gazawa zasu nema wanda zai iya.

Kalamansu sun masa zafi amma ya danne bai nuna musu ba. Sai da ya koma gida ya samu Mole shima cikin nashi ɓacin ran yace masa lokacin da zasu fara nasu shirin suma yayi fa. Amma sai sun ɗakko Nimrah dan shine first target ɗin su. Ɗakkota lokaci guda kuma bazai yiwu ba dole sai Mole ya nuna mata fuskarsa da sanar mata waye shi a gare ta. Tunda yanzu babu mai basu information ɗin gidan yanda ya kamata. Gaba ɗaya Nimrah ɗin ta daina kiran Dagger, sai ma Sanda da shi Molen ke ɗan taɓawa a waya lokaci-lokaci shi da maigadi. Shi kuma maigadi tsoro na hanashi sanar da Mole wani abun duk da bai san waye shi ba. Gara ma Sanda da yake yana da bakin surutu.

A wajen Sanda Mole yaji su Nimrah na zana jarabawa. Dan haka suka ɗora shirinsu akan binta makarantar. Sai dai abinda shi Dagger bai sani ba shima fa Mole na nashi shirin a bayan fage. Dan tuni ya ƙulla abota da wani mutumi dake da alaƙa dasu, dan suna kawo musu kayan abinci duk ƙarshen wata a jejunan da suke. Wannan mutumi shine yay masa hanyar samun gida a maƙwafciyar ƙasar. Aka kuwa samu mai ƙyau, da kansa yaje bisa ga wani aiki da Dagger ya sashi yaga gidan. Bai taho ba kuma sai da aka zuba komai a kwanaki uku. Aka ɗauki ma'aikata aka zuba sannan ya dawo. Ko yanzu da Dagger ya kawo batun Nimrah baiji ya damu ba tunda yasan ya kammala shirinsa shima.....

>>>>>>%<<<<<<

Anan kuwa Nabeeha ta matuƙar tada hankalinta akan batun bikin nan dake tunkarowa. Dan tunda taji abinda ake shirin yi Nimrah zata tare shike nan. Gashi ganin Dada ya mata wahala a gidan. Suma su Mammah ɗin ba ganinsa suke ba. Sai da mahaifiyarta tai mata tsawa sakamakon itama First Lady ta tsarata sannan. Ta tabbatar mata idan fa ta tada hankalinta Adeel na nan na jira. Dan yanzu ɗin ma akwai aikin da ta saka akai mata a kansa shiyyasa hankalinsa yabar kansu. Dan baya ma ƙasar yanzu haka.

Abinda Hajiya Hasiba bata sani ba kuwa babu wani asirinta da yaci Adeel. Ya tafi harkar kasuwancinsa ne kawai da kuma tsarin da First Lady ta zauna ta masa batare da sanin ita Hajiya Hasiba ba. Amma dai kalamanta sunyi tasiri akan Nabeeha. Musamman data tabbatar mata akwai abinda take shiri akan Nimrah. Amma sai ta tare dan aikin yay musu sauƙi tunda yanzu tana sashen Mammah ba wani abu zasu iya a kanta ba.

Duk maganar da sukai Rayhana na laɓe na jinsu. Hakama Nana, sai dai babu wanda yasan da ɗan uwansa. Wannan shine ya kawo masalaha akan Nabeeha sai dai ta saka kanta a damuwa sai rama take da duhu. Tun Ismat da Amima na lallashinta har suma suka gaji suka watsar da ita. Jiddah dama ta maida kanta gefe. Ko zuwa tai gidan suka kawo mata ƙorafi iyaka tace suyi hakuri kowa ma hakuri yake a nashi gidan. To sai ma sukai tafiya ita da mijinta yanzu haka basa ƙasar suma.....

••}{••}{{••}}{••}{••

A yau su Nimrah sukai final exams ɗinsu. Ba wani sabawa sukai da kowa ba dan haka suna kammalawa suka fito a hall ɗin cikin farin ciki. Kullum Mu'azz ke kawo su. Idan ya tashi school da wuri yazo ɗaukar su. Idan yana da lecture Biebah tazo ta ɗauke su. Dan haka koda suka fito sai suka nema waje suka zauna.

Abokan jarabawar tasu nata farin ciki da shagalinsu saboda su sun san juna. Su Ruky ne kawai baƙi a cikinsu. Su dai kallonsu kawai suke, dan zasu iya rantse wa ma bayan gaisuwa doguwar magana bata taɓa haɗasu da kowa a cikinsu ba tsawon kwanakin jarabawar nan. Nimrah ta fara ƙorafi saboda barci da take ji sai ga kiran Mu'azz ya shigo
[4/8, 7:30 PM] null: Miƙewa tai tana faɗin, "Alhammdullahi Buddy tashi yazo".
Miƙewar itama Rukyn tai tana ambaton Alhmdllh ɗin, daga haka suka fito a gate ɗin makarantar. Kansu tsaye inda motar Mammah take suka nufa, dan da ita Mu'azz ko Small Mom ke kawosu dama su ɗaukesu kullum. Kai tsaye Nimrah ta buɗe baya tana faɗin, "Barci zanyi shiga gaba dan ALLAH Ruky. Bata jira amsarta ba ta buɗe bayan ta shiga. Itama Rukyn ta shiga gaban.

"Subahannallahi waye kai?".

Ruky ta faɗa tana zabura, sai dai bata kai ƙarshen maganar tata ba aka fesa mata abu. Itama kuma Nimrah anan baya ta zabura ne ganin mutum a bayan kusan lokaci ɗaya da Rukyn. Sai dai ita saɓanin Ruky ca tai, "Baba driver".

Malam Buba yay mata murmushi da faɗin, "Na'am Uwa".

Gabanta ya faɗi, sakamakon leƙo kai da Dagger yay yana kallonta shima dan shi ne a gaban. Sai kuma ta kalla Ruky da sauri. "Na shiga uku mika fesa mata?".

"Kar ki damu ƴammata na, barci kawai na sakata zata tashi bada jimawa ba". Daga haka ya tada motar zai bar wajen. Nimrah ta sake jeho ma Malam Buba tambaya, "Baba ka koma aiki ne?".

Kai ya girgiza mata alamar a'a.
"To ina kuka samu motar gidanmu?".
Kai tsaye ya bata amsa da, "Amsa mukai hannun Mu'azz".

"Yaya Mu'azz?! Ta yaya to?".

"Ki kwantar da hankalinki Uwa, yanzu zaki ji komai bari muɗan gangara".

"Ni kana rikitani Baba Driver. Miye wani Uwa? Ni sunana Nimrah ne".

Murmushi kawai yay mata baice komai ba. Shima Dagger dake kallonsu ta mirror ɗin gaba sai yay ƴar dariya. Nimrah dai ta sake rikicewa. Ga shi sunƙi amsa mata tambayoyi ko ɗaya. Hasalima sun canja hanya bata gidansu ba. Sai da Dagger ya tabbatar sun yo nesa da makarantar sannan ya samu waje yay parking. A kuma lokacin ne Malam Buba ya fara kwaye gemun sa na bogi daga fuskarsa. Ashe duk tsawon zaman da yay a gidansu gemun nan ba nashi bane. Nimrah dake kallonsa kamar sokuwa ta saki baki da hanci. Sai da ya kammala tsaf cikin rawar lips ta furta, "Baba driver dama gemun nan naka na ƙarya ne?".

Kai tsaye ya amsa mata da "Kwarai Uwa. Na saka shi ne kawai dan na samu salamar zama a gidan da kike."

"Gidan da nake? To saboda mi?".

"Ba lallai kisan dalilin ba yanzu."
Dagger ya bata amsa yanzu kam. Ta kallesa da ƙyau. Sai kuma ta ce, "Nifa kuna sake rikitani. Kai ince kasan Baba Driver ne ma ta sanadina."

Dariya sosai Dagger yayi, ya sake juyowa da ƙyau yana kallonta. "A tunaninki kenan Nimrah. Amma bari muzo miki a mutane. Da farko dai ana kirana Dagger ne. Malam Buba kuwa da kike ma kallon driver ko wanda na sani ta dalilinki ba haka bane. Malam Buba abokina ne, aminina kuma ɗan uwana. Yaje aikin tuƙi a gidan da kike ne saboda ke. Ki kalla fuskarsa da ƙyau zaki ce baki sanshi bane?".

Nimrah ta kalla Malam Buba a karo na biyu, kallo irin na ƙurulla amma sam babu wani alamar ta sanshi. Sai kanta dake wani irin mata nauyi ma. Ga zuciyarta na

bugawa da masifar ƙarfi. Ba ita kaɗai ba, shi kansa Malam Buba tun buɗe fuskarsa da yayi a farko yaga babu wani reaction daga gareta na alamun ta sanshi hankalinsa ke tashe. Shiyyasa ya kasa ci-gaba da magana, dan tabbas akwai alamar tambaya.....

"Ban sanshi ba! Bamma taɓa ganinsa ba".

Furuci mafi muni daya kusa wantsalo zuciyar Malam Buba ƙasa. Idanunsa sukai wani kalar juyewa. Muryarsa da jikinsa na rawa yay ƙoƙarin kamo hannun Nimrah yana faɗin. "Uwa baki sanni ba? Ni ne fa mahaifinki Maude. Babanki mijin Ummanki Hassatu. Yayan Tanimu ɗan Inna".

Kanta ne ya ƙara Mummanan sarawa. Ta kai hannu tana dafe shi da girgizawa. "Ban sanka ba, wlhy ban sanka ba n......"

Tsabar yanda Malam Buba ya fahimci zai iya haukacewa da furucin Nimrah baima san ya kama kafaɗarta ya fara jijigawa ba yana faɗin, "Uwa! Ni ɗin ne baki sani ba. Naja'atu Babanki mahaifinki ne baki sani ba. Ki kalleni, ni ne mahaifinki......"

Received at 18:13Reactions:

[4/8, 7:31 PM] null: Ina maimakon ma ta fahimcesa sai ta tafi luuuu ta sume masa kawai. Ya ƙwalla kiran sunanta kamar zai fasa motar. A kuma dai-dai lokacin idon Dagger ya gano masa wasu motoci biyu dake tunkaro su...

"Mole! Mole akwai matsala. Ƙyale yarinyar nan muje tabbas ana bin mu".

Ina Mole bama yajin Dagger, har yanzu sai faman jijjiga Nimrah yake da kiran sunanta yana faɗa mata shine mahaifinta. Motar Dagger ya ɓalle da ƙarfi ya fice. Yay saurin duƙewa ƙasa ya buɗe inda Mole yake kawai ya fisgoshi. Amma ina yaƙi sakin Nimrah. Dagger bai san ma ya wanke masa fuska da mari ba ya fisgoshi gaba ɗaya cikin ƙaraji yace, "Kai wawa mahaukaci jami'an tsaro!!!".

Yanda marin nan ya shigesa, da yanda Dagger yay maganar cikin ƙaraji a kunensa ya sashi dawowa a hayyacinsa. Tuni ya saki Nimrah daya jawo gab da ƙofar tai yaraf. Shi kuma suka bar wajen a guje. Sai dai ina jami'an tsaron sun ƙaraso wajen har sun fara harbinsu. Dole suma suka ƙara gudu suna nausawa jejin wajen da maida murtani. Jami'an tsaron kuma suka rufa musu baya.. ƙarar wannan harbi ce ta farkar da Nimrah, dai-dai isowar ogan jami'an inda suke yay saurin kai hannu zai tarota dan yanda ta zabura gata a bakin ƙofa ta tafi ne zata faɗo ƙasa ta kai aka ɗora masa bindiga a kansa...........✍

Received at 18:13Reactions:

[4/8, 7:31 PM] null: 42

.........."Waye kai?".

Jarumar muryar Dada ta daki cikin kunnen sa. Numfashinsa daya riƙe a maƙoshi ya sauke a hankali jin ba waɗanda yake zato bane. Sai ma wani ƙaramin murmushi da ya ɗan saki kaɗan. Dai-dai nan Faro da yanzu motarsu ke isowa suka ƙaraso wajen suma. Dan shi Dada a mashin ɗinsa yazo. Mashin ɗin kuma sam baya ƙara dama, shiyyasa shima baiji zuwansa wajen ba. Faro daya riga ya sanshi sosai yana isowa wajen ya furta, "T. Ɗalha".

"Yes Sir!".

Jami'in ya faɗa dan shima kai tsaye ya gane muryar Faro kamar yanda ya gane ta Dada a maganar farko da yayi. Dada ya ɗan harari Faro dake kallonsa yana wani murmushin neman magana. Sai kuma ya janye bindigarsa daga kansa ya maidata cikin jikinsa ya matsa ya kama Nimrah da kansa.

Nimrah na riƙe da kanta dake sara mata kamar zai fashe ta shige jikinsa lips ɗinta na rawa alamar son yin magana amma ta kasa. Sai ma hankalinta da kamar ya rabu biyu. Dada ya fahimci kallon ƙurullar da take ma mutumin, dan haka shima ya juya yana kallon sa. Amma sai jiri ya kwashe Nimrah ta tafi zata zube. A tare Dada da jam'in suka zabura zasu tareta. Sai dai cikin sa'a Dada ya riga shi riƙeta. A karo na farko kuma ya watsa masa kallo mai nauyi. Tare da jefa masa gargaɗi cikin kausashiyar murya.

"Matar aure ce".

“I'm sorry Sir!”.

Jami'in ya faɗa yana duƙar da kai, sai dai gaba ɗaya alamun murmushi yake son kufce masa ya bayyana a tare da shi. Shi Dada ya riga ya ɗauke kansa dan haka bai lura ba. Sai Faro daya zuba masa ido cike da tuhuma da mamaki. Yasan waye T. Dalha sosai. Mutumin kirki ne balle ya zarge sa akan wata manufa. Bai dai ce komai ba dan yanzu ana kan aiki ne.

Dada da tuni ya ɗauke kansa daga garesu dama ɗagata yay cak ya saka a mota. Karo na farko idanunsa suka sauka kan Ruƙayya da Nimrah ke nuna masa. Ƙarasa kwantar da ita yay ya zagaya inda Raƙayyan take itama. A kallo ɗaya ya fahimci sumar da ita sukai da gangan, dan haka bai taɓa ta ba ya maida murfin ya rufe.

A wannan lokacin tawagar su Yusuf ke ƙarasowa wajen cikin kaki. Dada bai tsaya ba ya miƙama Faro key ɗin mashin ɗinsa. Motar ya koma yay mata key kawai yabar wajen. Daga Faro far T. Dalha da kallo sukabi motar, kafin Faro ya dawo da kallonsa akan T. Dalha ɗin cike da tuhuma.

T. Dalha ya kauda kai yana murmurshi. Cike da basarwa ya ciro waya a jikinsa yana faɗin, “Bari na taɓa yaran nan muji sun kama su”....

_____

Kai tsaye Dada gida ya nufa. Koda ya samu waje yay parking sai ya ɗaga waya yay kiran Ammar dan ya tabbatar yanzu suna gidan basu kai ga fita sallar juma'a ba, dan da ɗan sauran lokaci kaɗan.

“Fito ka sameni a compound”.

Ya faɗa a taƙaice yana yanke kiran. Babu jimawa kuwa sai gashi ya fito sanye cikin jallabiya. Dada shima ya fito yana nuna masa gaban motar. Ajiyar zuciya Ammar ya sauke mai ƙarfi, dan tun ɗazun cikin tsananin tashin hankali suke duk da an kawo Mu'azz gida tuni. Kuma Alhamdullah babu wani mumman rauni a tare da shi, shima sumar da shi kawai sukai suka ajiyesa gefen titi suka ɗauki motar. Ganin Ruƙayya kamar babu rai sai da gabansa ya faɗi. Amma sai Dada ya katse shi da faɗin,

“Kallonta zaka tsaya ko ɗaukarta?”.

Ƙeya yaɗan sosa. Kafin ya ranƙwafa ya ɗauketa yay ciki. Sai lokacin Dada ya kama Nimrah ya fiddota itama. Hannunta na riƙe cikin nashi ɗayan kuma ta riƙe kai suka shiga falon. Mammah dake tattaɓa Ruƙayya da Ammar ya shinfiɗe tayo kansu a rikice ta kama Nimrah ɗin tana jera mata tambayoyi.

Da ƙyar Nimrah ta iya furta, “Mammah basu mana komai ba ki kwantar da hankalinki”.

Ajiyar zuciya kuwa ta sauke. Dada dake kallon su ya ɗan furzar da numfashi. Kusa da Mammah da duk hawaye suka cikama idanu ya zauna yana amsa gaisuwar su Shariffa da duk suka sake nutsuwa waje guda cike da girmamawa a gare sa. Ya maida kallonsa ga Mu'azz dake kwance.

Received at 18:13Reactions:

[4/8, 7:32 PM] null: “Sun maka wani abu ne?”.

Kai Mu'azz ya girgiza masa. Muryarsa da damuwa ya ce, “A'a Dada. Abu kawai suka fesa min daga nan na rasa hankalina.”

“ALLAH ya kiyaye gaba”.

Ya faɗa a taƙaice ce yana miƙewa. Su kuma suka amsa da amin....

Likita aka sake kira ya farfaɗo da Ruƙayya. Nimrah kuwa addu'oin Mammah taita mata a haka barci ya kwashe ta. Dukansu aka maidasu ɗakin Mammah mazan gidan suka fita salla.

Sosai abin nan ya tsaya ma Mammah a zuciya. Ji take anya baza'a matso da tariyar nan ba yaran nan su koma ƙarƙashin mazajensu. Ita fa harga ALLAH wannan ɗauke-ɗauken na ɗaga mata hankali matuƙa. Yau badan ALLAH yasa Muhammad yayi dabarar saka abu a wayarsu da motar ba da basu san kuma mizai faru ba. Dan

ba lallai yanda Nimrah ta tsira a ɗaukar farko a yanzu ace duk sun tsira ba. Waɗan nan wane irin ibilasan mutanene haka?.

Bata da mai bata amsa, dan haka ta haƙura ta zauna tana ta kallon su Ruƙayyan kawai. Addu'a kam yau sun shata kala-kala.....

<<••>><<•>><<••>>>

"Bafa a samu mutanen nan ba Zak.. Ni nama fara tunanin ko aljanu ne?".

Dada dake zaune ƙafa ɗaya kan ɗaya yana sauraren Faro dake maganar ya ɗago idanunsa a karo na farko yana kallonsa. Sai dai yaƙi yace komai akan maganar da Faron yayi tsahon lokaci. Har ma ya fidda rai da samun amsar sai kuma ya amsa masan.

"Suna da maɓoya ne kawai ta wajen. Shiyyasa suka kai motar suka ajiye a wannan gurin saboda kota ƙwaɓe".

"Wow! Tabbas maganarka na kan hanya. Ya akai kammu bai kawo wuta ba ne. Dan yaran T. Dalha dama sun tabbatar sun harbi wani a cikinsu a ƙafa."

"Shine kuma suka baro jejin?".

Dada ya faɗa cikin alamun ɓacin rai.

"Relax Haysam, ka musu uzuri. Dole su dawo da baya tunda basu san shirin mutanen ba. Gashi babu wani makaman kirki a hannunsu, wlhy bindugunsu duk sun saki fa. Kasan fa ƙasar yanda take".

Shiru Dada baice komai ba. Amma alamu sun nuna ya gamsu da zancen Faro ɗin. Dan suna a haka Imran ya shigo. Hannu duk ya basu suka gaisa, kafin ya zauna. Bayanin yanda komai ya faru Faro ya bashi. Mamakin tsagerancin mutanen nan ya tsaya masa a rai. Shima zai fara faɗa akan dawowar Jami'an tsaron da basu zauna a jejin ba har sai sun gano inda suke Faro yay masa irin bayanin da yay ma Dada. Shiru yay dan ya fahimta. Sai kuma zuwa can ya furta,

"Dole ne a sabuntama Jami'an tsaron kasar nan makamai na zamani in har ana son aikin nan ya tafi yanda ake buƙata".

"Tabbas wannan shine abinda ya dace. Dan mutanen nan sunada makaman da suka fi na jami'an tsaron. Ka duba fa kaɗan daga kayan da muka fara samu nasu yanda suke."

"Wannan gaskiya ne Haydar. Amma shi wannan T. Dalha yake ko? ya akai yasan da wannan shirin nasu haka?. Kaga fa yama rigaku zuwa".

"Nima wannan tambayar nata min kai-kawo a rai. Amma nasan T. Dalha jami'i ne mai gaskiya da sanin kan aiki. Dan wannan halayyar tasa ce ta ɗagashi da sauri a aikin jami'an farin kaya. Shine ya jagoranci aikin kwashe iyalan driver ɗin can fa".

"Oh Masha ALLAH dama shine?."

Kafin Imran yaba Faro amsa Dada ya furta. "Ina buƙatar bincike a kansa".

Bai jira amsar su ba ya miƙe abinsa ya nufi ɗakin sirri. Da kallo duk suka bishi, sai da ya shige Faro yay murmushin da yake ta riƙewa. Cike da gulma ya kalla Imran. "Hummm mutuminka fa kishi ke ɗawainiya da shi....." ya kashe abinda ya faru ya sanar masa. Imran yay ƙaramar dariya da faɗin, "ALLAH ma ya taimakesa ba'a karya hannun ba. Amma fa gaskiya nima ina buƙatar ganin T. Dalha ɗin nan. Dan akwai abinda ya kamata mu sani a kansa. Kace fa Nimrah nata kallonsa?".

"Sosai, dan har kamar htna son yin magana ma"...

★Dada kam koda ya shiga ɗakin sirri wasu hotuna ya shiga tattarowa. Tare da wasu tsoffin files yana bincike. Kafin ya koma gaban computer. Tun ma bai nisa ba ya samu abinda yake so. Ya zubama bayanan daya tattara idanu, mamaki sosai na kamashi. Yaya akai tun a wancan lokacin basuyi wannan tunanin ba? Sannan miyasa shi ma ya ɓoye musu?.

Received at 18:13Reactions:

[4/8, 7:32 PM] null: Maimakon samun kansa da neman amsa waya ya ɗauka tare da file ɗin ya fito. Ya samu Imran kawai a zaune sai Dabo. Faro ya fita. Hannu kawai

ya ɗagama Dabo dake gaishe shi. Sai kuma ya miƙa masa file ɗin hannunsa yana faɗin, “Bincika min cikin hukumar ƴan sandan farin kaya yaushe wannan mutumin ya fara aiki”.

“Okay Boss”.

Dabo ya faɗa yana amsar file ɗin. Waya ya sake ɗauka shima yay kira. Bugu biyu aka ɗaga masa. Daga can akai sallama cike da girmamawa. Tare da gaisuwa. A taƙaice ya amsa. Sai kuma ya cigaba da faɗin. “Hassan zan turo maka wani suna yanzu ina son bayanansa gaba ɗaya a cikin jami'an ku yake”.

“In sha ALLAHU Sir. Ka tura kawai”.

Komai Dada bai sake cewa ba ya yanke kiran. Dukkan abinda ya faɗa ya turama Hassan ta email. Yana ajiye wayar Dabo ya ce, “Sir! Ga shi na samu komai”.

Ƙaramin Murmushi yayi, dan yasan Dabo shegen kansa ne indai akan kutsen bayanan sirrine ko shi daya koya masa a yanzu ya dama shi ya shanye. Shi kansa Imran sai da ya murmusa da faɗin, “Anya Dabo ba kune matsalar ƙasar nan ba? Dan wataran brain ɗin mutane zaku dinga shiga ta na'ura”.

Dariya Dabo yayi da faɗin, “Sir mu mun isa. Wannan ma dan aikine kawai”..........
✍

Received at 18:13Reactions:
[4/8, 7:33 PM] null: 43

........Tsaf Dada ya gama duba bayanan da Dabo ya samo. Koda Imran ya amsa ya duba yayi matuƙar girgiza shima. Cikin kasa shanyewa ya furta, “Kenan tun a wancan lokacin Jam'i ne?”.

Dada ya ce, “Hummm! Yayi wasa da hankalinmu.”

“Bana wasa ba kuwa. Amma Nimrah ta gane shi kenan?”.

“Banda tabbas, naga dai tanata kallonsa”.

“Kai ya rabbi. Bana son abubuwa su kwaɓe a yanzu har sai an kammala bikin nan lafiya wlhy. Ni mutanen nan ma da suka ɗauke su ne naketa tunani su kuma mi suke nema? Dan bana jin na farkon ne suka sake dawowa?”.

Dada dake jingine da kujera idanunsa a lumshe ya ɗan furzar da iska. “Suna da alaƙa. Amma ba'akan manufa ɗaya suke ba a kanta. Ina ƙyautata zaton driver ɗin nan ne da yaron nan da aka ɗauke su hoto a tare har ta gani”.

“What! Zak.. na fara shiga ruɗani fa. Anya mutumin nan bashi da alaƙa da Nimrah kuwa?”.

Karo na farko Dada yay murmushi. Sai dai baice komai ba. Hakan yasa Imran fahimtar akwai abinda ya sani game da mutumin yana ɓoyewa ne. Cikin kasa haƙuri ya furta, “Ka sanshi kenan?”.

Miƙewa Dada yay kamar bazai amsa masaba yanzu ma. Sai da yaje bakin ƙofa ya furta. “Manta kawai Imran. Ya kamata mu wuce”.

Imran yasan waye Zakinsa, sai kawai ya saki zancen kamar yanda ya buƙata suka fito.....

•••••••••••••••

“Wlhy tunda suka zubar min da jini a karo na uku sai na ƙarar da su. Kisan gilla zan musu na tashin hankali. Sai sun san sunyi da ɗan halak. Ni Dagger bana barin bashin gaba....”

Mole ya katse Dagger da faɗin, “Oga kayi shiru dan ALLAH. Yanzu bata wannan ake ba mu samu muƙarasa gida a cire maka wannan harsashin shine mai muhimmanci. Jibafa yanda kake zubar da jini duk da an ɗaure”.

A wahale Dagger yaja tsaki yana cigaba da nishi. Ga zufa ta masa sharkaf kamar an masa wanka da ruwa. Mole ke goye da shi a bayansa duk da kuwa ya masa nauyi. Dan Dagger ƙato ne na gaske dan ma yana shaye-shaye. Tun barowarsu inda su Nimrah suke suka nausa cikin jejin nan ƴan sanda suke binsu. Sun san jejin sosai

kamar yanda Dada yay hasashe, amma da yake tsautsayi ya ratsa a bazata Dagger ya samu harbi. Daga nan ne suka samu ɗaya daga maɓoyarsu suka shige shiyyasa yaran T. Dalha basu samesu ba. Sai da suka tabbatar sun haƙura sun koma sannan suka fito, Dagger ya gama galabaita dan yanata zubar da jini, shiyyasa Mole ya goya shi. Sun ɗanyi nisa da tafiyar wasu matasa biyu sukazo a babura suka ɗauke su.....

ΔΔΔΔΔΔΔΔΔΔΔ

Kwana biyu Nimrah na fama da ciwon kai. Dole ne ka tausaya mata dan tasha wahala sosai. Ita ko Ruƙayya tunda ta farfaɗo ta miƙe kamar komai bai faru ba. Tun daga ranar Dada ya saka musu dokar fita. Dama sun kammala jarabawa. Islamiyya ce yace a haƙura bayan biki sa koma.

Hakan kuwa akayi, sai ma su Shariffa suka samu dama da nutsuwar yi musu gyaran jiki. Sai class ɗin Chef Yakudima 08135358038 da shima suka ƙara dagewa. Dan duk rashin son girkin Nimrah sai gashi class ɗin na mata daɗi saboda yanda Chef Yakudima ke treating ɗinsu tamkar ƙannenta. Ga shi dai online ne amma sun shaƙu sosai kamar sun taɓa sanin juna.

A yau ranar juma'ar data rage saura kwanaki takwas biki su Uncle Ja'afar suka iso. Washe gari asabar kayan da suka zo da su suma suka iso. A kuma ranar suma su Gwaggo Khadijah suka sauka. Abinda ya fara bama Mammah mamaki ganin zuri'ar su Yaya Babba. Dan basu taɓa zuwa inda take ba. Itace ma idan ta ɗan je takan leƙasu a gaisa. Su kansu su Dada sunyi mamaki. Amma shi dai bai ce komai ba. Su Bilal da su Aunty Mimi ne ma suka tanka. Dan da farko ma su Ja'afar ƙin kulasu sukayi. Sai da Mammah tai musu magana.

Ba wannan ya sake bama Mammah mamaki ba sai washe garin Lahadi da itama wasu a danginta suka iso tare da zuri'ar Kawu Zubairu yayan Uncle Nasiru Ogan Abdul-rasheed na ɗinki idan baku manta ba. Mammah ta share hawaye, dan wannan na nufin yanzu yan uwa sun fara dawowa garesu kenan. Ta tabbatar kuma darajar tasu ta ƙara fitowa ne saboda wannan appointment da aka bama Muhammad ne.
Received at 18:13Reactions: ❤
[4/8, 7:34 PM] null: Saboda yanda ƙura ta tashi a lokacin babu wanda zaice sunan Haysam Abdul-rasheed Shehu Kobi da hotonsa bai shiga wayarsa ba indai yana saka data. Baiwar ALLAH babu wanda ta nunama wani abu. Kowa ta tarbeshi gwargwadon iyawarta. Tun ma ba'aje ko ina ba har gidan ya fara musu kaɗan musamman sashenta. Dan su Ja'afar sun murje ido sun hana kowa zama musu sashe sai iyalan Gwaggo Alawiyya dana Gwaggo Khadijah da Uncle Jamilu kawai. Sauran kuwa sunce su tsaya wajen Mammah ɗin ita suka sani su basu ma san su ba.

Zuwa Laraba dole wasu baƙin suka sauka gidan Uncle Nasiru. Ita Mammah harma mamakin wanda ya sanar da su bikin take. Dan tasan dai bata gayyaci kowa ba. Su ba sanarwa sukai gidan rediyo ba balle ace. Basu turama kowa invention ba. Sai daga baya ta fahimci aikin Uncle Nasiru da Uncle Jamilu ne. A ranar ne akai shirin yima amare jere. Dan haka su aunty Ummi suka ɗunguma zuwa gidan Biebah. Nan kuma aka fara ƙoƙarin tsaftace sashen Bilal, Ammar, dana Dada bangaren Nimrah da nashi bangaren.

Hankalin Nabeeha ya tashi, dan a ranar sai da Hajiya Hasiba ta yini gidan da Mamawo. Dama kwanakin nan tunda baƙi suka fara sauka duk ta ƙara hargitsa kanta. Da ƙyar ƴan uwan ke tausarta. Da tace ma zata koma gida idan an gama bikin ta dawo Hajiya Hasiba tai mata jan ido. Da yamma kuma sai ga First Lady da kanta. Ita ta zauna ta tsara Nabeeha ɗin da zantukan da suka sa ta janye batun barin gidan. Sai dai fa yanda duk ta birkice dole ta baka tausayi...

★★★

Kuce min ina amare su Nimrah suke? Suna gidan Baffa su duka huɗu. Dan dole a yau aka maida su can. A can Hajjo ta buɗe musu batun an ɗaura musu aure tun randa aka kawo kuɗi. Yanda Ruƙayya ke zaro ido da su Asma'u da ita kanta Small Mom ɗin tasu ba ƙaramar dariya ya bama Nimrah ba. Ta dinga tsokanar Ruƙayya har sai da ta sakata kuka. Dan ita fa duk abin nan da akeyi ta dauka kawai ana mata tare da Nimrah ne saboda tana aminiyar amarya saboda wauta.

Ganin kuma tana kuka sai jikin Nimrah yay sanyi ta koma lallashinta itama tana hawayen. Sai da Hajjo ta ce. “Kai kuji min yara da shashancin. Kuda ma kuke ƴan gata. Mutum yay aure a gidansu gaku ga uwarku, ga sauran iyayenku. Sannan kuna tare. Ai idan ma da me yin kuka uwarku Habiba ce. Ni nama taɓa ganin auren gata irin naku? Idan da haka mata ke samu babu su ai babu kukan aure.”

Wannan magana ta Hajjo ta kawo musu nutsuwa, dan kuwa tabbas sun yarda su ƴan gata ne. Ana haka sai kuma gasu Feedo ma sun iso, tuni suka sake mantawa da komai suka koma shiriritarsu. Balle ma harda baƙin Bauchi ƴammata kamarsu-kamarsu. Gobe idan ALLAH ya kaimu alhamis kamu, dan haka a yau da daddare sai ga Mu'azz da akwatinan kayan da zasuyi amfani da su su duka. Dan ranar aka kawo lefen Biebah. Itama Asma'u an kawo nata nan gidan Hajjo tun jiya. Nimrah da Ruƙayya kuwa nasu na wajen Mammah, dan bama a buɗesu ba ance kowacce za'a kai mata sashenta idan masu jere sun kammala gaba ɗaya dan har zuwa yau suna kan aikinsu.

Gaba ɗaya amaren babu mai ganin angonta sai ta waya. Dan Ammar ma dai ya dage, bare yau yana kira Ruky ta saka masa kuka. Jiyay gaba ɗaya ya rikice, gashi baya kusa suna hotel ɗin da zasu sauke abokansu shi da Bilal. Dan su manyan gayyar Dada da Faro basu san ya suke ciki ba. Kai su bama ganinsu ake ba, suna can sabgar aiki tasha kansu. Dan ko Imran yanda yaga sunyi busy ɗin nan sai da yace Dada ya taimakesu da aka ɗaura auren nan a waccan ranar da yanzu suna nan a birkice. Yanzu kuwa sun barma mata sabgar sukuma suna mai fishesu.

Nimrah daba taɓa waya tai da Dada ba dama ko'a jikinta. Kai ita haka ma ya mata, dan rabon ma data ganshi tun randa ta samu lafiyar ciwon kan nan nata, abin mamaki kuma bata sake tuna wani Malam Buba ba balle abinda ya faɗa mata na cewar shi mahaifinta ne. Sosai ɗinkuna nasu duk sunyi ƙyau, dan su duka huɗu an musu na bikin ne na musamman ba'a cikin kayan lefe aka ɗauka ba. Zuwa yamma mai wanke musu kai tazo gida. Dan komai da za'ai musu home services aka ɗauka saboda tsaro.

Received

[4/8, 7:34 PM] null: Da yake kwararriyar mai aiki ce tasan aikinta sosai gata aminiyar Aunty Mimi ce kuma tana da ma'aikata sosai da suma suka san aikinsu zuwa dare an gama gyara su. Amare sun ƙara fitowa. Dama ga gyaran jikin ya sakasu sun ƙara ƙyau matuka, dan kayan SHUWA INCENSE AND MORE +234 704 229 3387. duniya ne. Turare kam ai ko daga nesa ka doso su sai kaji yanda ƙamshinsa ke tashi Masha ALLAH.........✍

Received at 18:13

[4/8, 7:35 PM] null: 44

..........Washe gari tunda safe kuma aka ɗora da ƙunshi. Duk kuma dai mai saloon ɗin nan ce. Kafin Azhar an kammala tsaf. Sai yaranta da zasu ma ƙawayen amarya gobe in sha ALLAHU. Dan yau kamu gobe ƙunshi. Anan gidan Hajjo za'ai Kamu. Gobe kuma ai Kunshi gidan Uncle Nasiru. Ranar asabar Ammie da Mammah kowanne zai yi yinin biki. Lahadi ai dinnar da su Ma'aruff suka shirya, duk da Dada yaso hanawa Mammah tace ya barsu. Dan cikinsu babu abinda akayi saboda yana prison. Yanzu kam ya bari su nuna farin cikinsu daga nan kuma sai na Mu'azz. Dole yay shiru tunda anfi ƙarfinsa...

Ba ƙaramin ƙyau wajen kamu ɗin yayi ba kuwa. Mamaki ya kama su Nimrah ganin yan ajinsu na islamiyya dana boko nata tururuwar zuwa. Dan babu wanda suka gayyata. Basu san Mu'azz yayi invention ya kai makarantunsu ba. Amma da abinda zai baka dariya Mu'azz ɗin da su Imam, Khalifa ne kamar ƙawayen nasu sai su Bintu. Ita ko Biebah dama ƙawayenta tun a jiya suka fara zuwa. Na Secondary dana University. Hakama Asma'u ƙawayenta sun taru sosai gana danginsu kuma...

Kusan ƙarfe uku su Aunty Momy suka iso daga gidan Mammah. Sauran mutane sai anyi la'asar. Aunty Mimi da su Lailah, Shariffa sune kan amare har mai kwalliya ta gama musu aka shiryasu cikin manyan lafaya masu shegen ƙyau. Abin nasu sai masha ALLAH amare huɗu reras. Biki ne iya na mata, sai su Mu'azz dake nane da su Nimrah har ana musu dariya yayun banza. Ko'a jikinsu sukam. Sune ma masu ɗaukar hotuna. Tsabar neman magana yanda suka turama Ammar da Bilal hotunan Asma'u dana Ruƙayya kowacce da wayarta haka suka ɗauki ta Nimrah suka saka number ɗin Dada da suka san yana WhatsApp. Dan sun duba sunga babu number ɗinsa. Abinda basu sani ba kuma akwai numbers ɗinsa har biyu a ciki sai dai wanda basu sani ba. Hatta ita mai wayar bata san numbers ɗin waye ba kuma bata taɓa damuwa da su ba. Haka suka loda masa hotunan Nimrah....

<<••>><<>><<••>>

Dada na Office aiki ya masa caa dan barowarsa office ɗin shugaban ƙasa kenan ya dawo nashi office ɗin wayarsa data shafi family ɗinsa kawai ya samu tana haske. Sai da ya zauna yana sauke numfashi da zare tie ɗin wuyansa gaba ɗaya ya rage botiran shirt ɗinsa guda uku na sama sannan ya ɗauka wayar. Dan bai sani ba ko Mammah ce ta kira shi. Ilai kuwa yana dubawa yaga miss call ɗinta sai na Uncle Nasiru ma.

Mammah ɗin ya fara kira. Bayan sun gaisa take tambayarsa Uncle Nasiru ya kira shi ne?.

“Yanzu nake ganin miss call ɗinku a tare na fara kiranki Mammah. Wani abu ya faru ne?”.

“Dama iyayenku ne maza na Bauchi suka zo”.

“Mammah iyayе kuma? Bayan Uncle Jamilu muna da wasu iyayene kuma a can?”.

Murmushi Mammah tayi dan dama tasan za'a rina. Shiyyasa ta kira shi da kanta duk da hayaniya ta mata yawa. Yanzu haka tana can sama ɗakinsa dan nan ne kawai babu kowa. “Muhammad shiyyasa dama na kiraka dan nasan halinka. Tunda dai sun kawo kansu a maida komai ba komai ba ayi biki a tashi lafiya ba shike nan ba. Bana son ace wata matsala ta taso daga gareku akan dangin nan nawa dana mahaifinku. Kai ne uba, duk abinda sukaga kayi suma sauran ƴan uwanka shi zasu yi”.

“To amma Mammah tunda an riga an ɗaura aure miye na wani gayya? Shiyyasa na saka aka ɗaura auren dan bana son wani damuwa”.

“Koma dai miye nidai nace ayi abinda ya dace”.

“Hummm shike nan. Duk yanda kike so haka za'ayi”.

“To na gode idan kuka min hakan. Nasan ba gidan nan zaka shigo ba yau ma. Su Bilal ma sun tarkata yau sun koma inda baƙinsu suke har su Ma'aruff. Sai ka tarkata su ko zuwa da safe ko anjima kuje ku gaida su dan duk suna can gidan Yaya Nasiru. Yaya Zubairu ma yazo”.

Jin Kawu Zubairu yazo ya saka Dada yin murmushi. Dan haka yay sallama da Mammah akan anjima zasu je. Yana yankewa ya kira Uncle Nasiru shima. Shima dai irin batun Mammah ɗin ne. Dan haka yace masa anjima zasu zo yanzu yana office. Daga haka ya yanke kiran. Zai ajiye wayar yaga notifications an tura masa hoto da number ɗin Kiddo.

Received
[4/8, 7:35 PM] null: Yayi mamaki, dan tunda ya basu wayoyin nan daga ita har Ruƙayya bai taɓa kiran kowa ba, suma bama su san da number ɗinsa a wayoyin ba.

Kamar zai share sai kuma ya ɗauka ya buɗe ta notifications ɗin. Ƙirjinsa yay wani irin motsawa sakamakon cin karo da hoton Nimrah. Tayi masifar ƙyau a cikin

lafaya ɗin. Sannan ta ƙara masa girma a ido. Gashi yanda tai murmurshi da kamar tana hararar wani ya fito da hasken haƙoranta dana idannunta. Ai sai ga Dada da lumshe idanu da cije lips. Baima san ya cigaba da kallon sauran hotunan ba har wanda suke da Rukkayan sa. Duk da basa kama idan ka gansu sai ka ɗauka tagwaye ne. Sannan a kallo guda zaka fahimci akwai ƙaunar juna mai ƙarfi a tsakanin su. Hoton ƙarshe su huɗun ne duka. Su suna tsakiya gefe da gefe Asma'u ne da Biebah. Suma sunyi ƙyau sosai. Ya ɗan murmusa yana ajiye wayar. Sai kuma ya gyara fuskarsa da yanayinsa sakamakon knocking da akayi. Yasan AS ɗinsa ne ya kawo masa lunch daya buƙata. Yunwa yake ji yau ko breakfast baiyi ba, dan rabonsa da kwana gidan su kusan 5days kenan. Ya koma UNIT ZERO ya tare shi da Imran da Faro suma duk gidajen nasu dangi ƴan biki sun cike su.....

★★★★

Gidan Baffa ya cika tam da mata. Dan kuwa ga dangin su Daddy Imran, ga dangin Faro da suma suka iso. Ga tawagar Mammah. Aunty Ummi, Aunty Mommy, Aunty Mimi. Shariffa, Lailah kowa da ƙawayenta. Ita kanta Ammie ƙawayenta duk sun iso. Ga kuma dangi ƴan Bauchi da ƴan Kano. Ga abokan huɗɗa nan cikin gari. Taro fa sai ace sambarka. Karo na farko da wani abu yaso zuwama Nimrah a zuciya kan dangi. Sai dai zuciyarta tai saurin fargar da ita suma waɗan nan ƴan uwanta ne. Dan kowa na mata komai babu ko banbanci akan fuska. Kai ita bama tajin su ba jininta bane. Kawai dai zuciya da saƙe-saƙe balle kuma mutanen nan sun riga sun nuna mata abinda da bata damu da saninsa ba wato dangin nata.

Sosai kamu ya ƙayatar. Ansha kiɗan kwarya. Yayinda Ruƙayya da Nimrah suka sha rawarsu da ƙawayensu. Yo mi yafi ransu ALLAH na tuba. Mutane nata dariya da faɗin waɗan nan amare biyu dai akwai rawar kai. Asma'u da Biebah kam da yake sun fisu hankali su duk sun nutsu kowace da abinda ya isheta. Sukam ƙawayen juna babu abinda suke tunawa. Su Mu'azz sun shige cikinsu ana cashewa. Dan duk ustazancin Imam yau sai da Khalifa da Mu'azz suka saka shi yay rawa.

Sun ko sha liƙi wajen iyayensu yanda ya kamata. Dan Hajjo kanta sai da tazo ta liƙesu ita da tsofaffin ƙawayenta irinta. Gab da magriba aka tashi. Su Nimrah sunyi tuɓis. Suka dai samu sukai wanka sannan suka zauna ana shan hira cikin ƙawayensu. Dan kowacce amarya ɗakinta daban da ƙawayenta. Sune dai dama kowa yasan ba'a raba hanta da jini....

WASHE GARI.

Yau data kasance juma'a kuma ƙunshi. Dan haka amaren ne da ƙawayensu kawai sukai shagalinsu a gidan Uncle Nasiru. Dan tun 12 aka gama kwashesu zuwa can. Sun samu baƙi maza sosai a gidan kuwa. Sai dai da yake suna a sashen baƙi babu ruwansu da su. Hasalima basu san su wanene da wanene ba. Anan ma komai ya tafi musu yanda suke so. Akasha hotuna aka cashe. Dan yau ma su Ruƙayya basu rage komai ba. Balle ma isu-isu ne kawai. Ƙawayen Small Mom kawai suke ragawa. Na Asma'u kam ai kallon sako akema juna itace dama abokiyar faɗan tasu. Anan ma sai yamma taro ya tashi. Anan suka kwana. Washe gari asabar aka maida Asma'u gidan Daddy Imran. Biebah, Nimrah, Ruƙayya gidan Mammah. Dan yau iyaye zasuyi nasu yinin biki. Idan da da mutunci Ruƙayya wajen Nabeeha ya kamata akaita kasancewar Dada ne uba. Amma kowa yama san wata fitina ce daban. Dan tunda aka fara hidimar bikin nan babu wanda zaice yaga idon Nabeeha da ƴan uwanta a gidan. Ƙarshe ma Rayhana da baƙin ciki ke neman zubarwa a ƙasa gida ta koma, wai idan biki ya tashi ta dawo. Anan ma Hanoon ciwo kashirɓan ta kwanta dan ko taro ɗaya bata halarta ba. Mammah tayi busy da yawa bata san abinda ke faruwa ba. A tunaninta ma Hanoon ɗin na tare da Biebah ne. Shima dai Dayyan yana cikin hali, dan yanzu ba zaman gidan yake ba ne kawai saboda ya samu abokai a anguwar. Dada kuma na sane da shi kawai ya share shine dan baida lokacinsa a yanzu.

[4/10, 11:13 PM] null: 45

..........Wajen biyar suka bar gidan zuwa gidan Daddy Imran. Shima acan an bama Asma'u key ɗin mota da tata sarƙar. Duk da biki ne da bana yan siyasa ba sai da aka samu munafukin daya kai batun wannan ƙyautuka a media. Oho suma suka san sunayi. Su dai masu bikin shagalinsu kawai suke yi Alhamdullah.

(((((★)))))

A jiya Dada bai samu damar zuwa gidan Uncle Nasiru ba saboda abubuwa da suka taso musu. Dan suma Ammar da Bilal a ranar sukai bachelorette party ɗinsu su da abokansu. Jiya kuma juma'a sukai walima. Yau asabar ɗin ma akwai party da zasuyi da daddare da ƙyar Dadan ya samo su da yammar nan. Dan Ma'aruff da Ja'afar sun biye musu su kansu ba ganinsu yake ba. Shi ko ko event ɗaya bai halarta ba dan babu ma hakan a tsarinsa. Yo shi baima san mi da mi suke yi ba. Dan ko dinnar daga shi har Faro babu mai maganar zuwanta. Akwai dai walima da zasuyi shima dan shugaban ƙasa ya dage ne kawai a gobe lahadi daga 2 na rana zuwa 6 na yamma in sha ALLAHU, acewarsa tunda babu daurin aure ya dace ayi ɗin, shi kuma yana son ayi ɗin ma dan Dada ya sake sanin mutanen ma da ƙyau. An gayyaci kuma manyan ƙasa sosai harda wanda ma su huɗɗa bata taɓa haɗasu ba.

Bayan sallar la'asar lokacin da can su Mammah keta shagalinsu anan su kuma gidan Uncle Nasiru sukaima tsinke. Sai dai da yake Ja'afar, Ma'aruff, Bilal, Ammar suna tare sun riga Dada zuwa. Amma sai suka ƙi shiga suka tsaya jiransa a compound. Basu wuce mintuna sha biyar ba sai gashi ya iso. Yusuf ne ya tuƙoshi. Dan daga wani waje ma suke yace su zarto nan ɗin.

Yusuf na gama tsayawa suka ƙaraso wajen. Bilal ya buɗe inda Dada yake zaune. Waya yake dan haka ya samu jinkirin fitowa. Dan sai da ya ɓata kusan mintina biyar kafin ya fito. Su huɗun duk suka haɗashi suka rungume har suna bama Yusuf sha'awa. Su ko kewarsa ce ta ishe su kwana nawa basu ganshi ba ya musu wahalar gani. Shima kewar tasu yake ji sosai. Dan har sai da ya tsokani Ammar da Bilal wai yaga har sun fara ƙyallin angwaye. Aiko mi Jafar da Ma'aruff zasuyi in ba dariya ba. Da wannan nishaɗin akan fuskokinsu suka doshi falon baƙin Uncle Nasiru da takalma suke birjit. Dada ne a gaba su huɗun suna take masa baya kamar wani boss da securitys ɗinsa.

Tunda sukai sallama falon yay tsitt. Sai masu ƙarfin hali ne suka amsa a cikinsu. Dattijan tsoffi ne kusan goma sha uku. Uncle Nasiru, Zubairu, Jamilu. Sai Uncle Tijjani (Yaya Babba kenan daya ce zai auri Mammah bayan rasuwar Babansu) sai ƙaninsa mai bi masa Uncle Yusha'u, sai autansu Uncle Mudan daya je saudia ya tare tsahon shekaru, baifi watanni biyu kenan da aka dawo da shi ba. Uncle Ayuba cikon na huɗunsu shine ya rasu tare da Abdul-rasheed in baku manta ba. Sai Uncle Tasi'u da basu san ma da zuwansa ba, ashe shima jiya yaso. Sauran kuwa duk dangin bangaren Mammah ne na wajen mahaifi da kuma na bangaren Inna.

Sosai zaratan mazajen na Mammah biyar ras suka girgiza zukatan su Yaya Babba. Dan babu wanda bai daburce da ganinsu ba. Balle ma Dada ya haɗe fuskar nan tashi babu wasa a cikinta. Abinda ya ƙara firgitasu cike da girmamawa ya gaishe da Uncle Zubairu da Uncle Nasiru da Uncle Jamilu. Amma su sai ya haɗasu a kuɗin goro yace. “Barkan ku”.

Yanda yayi kuma haka ƙannen nasa suma sukayi. Daga haka ya samu kujera ya harɗe hankalinsa akan Uncle Zubairu dake masa magana. Suma su Ja'afar suka samu wajen zama kusa da shi hankali kwance duk suka harɗe. Ko kura tasan gidan mai babbar sanda. Ba boss ɗin kawai ba, hatta su Bilal ɗin kwarjininsu ya cika musu ido. Dan ko makaho ya laluba waɗan nan lafiyayyun zaratan samarin yasan nera ta zauna musu. Sannan hankalinsu a kwance yake duniya nayi da su.

Kunya, nadama, dana sani suka shiga rige-rigen sauka musu a zuciya. Da ace sun riƙesu a lokacin da suke buƙatar taimakonsu matsayinsu na yara marayu da yanzu dasu ake cin wannan duniyar da tsinke. Amma son zuciya da sheɗan ya rinjayesu suka runtse idanunsu. (Mutane da yawa suna kallon yau ne a rayuwar bayin ALLAH musamman yara marayu a lokacin da aka tafi aka barsu da ƙarancin shekaru.
Received at 14:59
reacted with
[4/10, 11:14 PM] null: Sai kaga an kasa ƙyautatawa da kulawa da su ana kallonsu a nauyi matsala mai girma. Shi kuma UBANGIJI shi yasan gobe. Shi yasan su waye bayinsa kuma a goben. Shiyyasa sai kaga ALLAH ya ɗaukaka yaran a shekarun girmansu kuma ƴan uwansu suzo suna nadama da koke-koken banza da wofi da nadama. Su kuma yaran zukatansu sun riga sun bushe da abinda akai musu, masu sauran imani ne ma ke iya musu irin wannan kallon naba wulakanci babu kuma girmamawa irin na su Dadan. Mutane sai mu kula, mu kuma gyara, sannan mu dinga tunawa muma ba ƙarfinmu ko wayonmu ko iyawarmu ce tasa muke rayuwa da namu yaran ba. Idan ka kula da maraya, kaima watarana sai su kula da kai da taka zuri'ar).

An bar su Yaya Babba dai da murmushin yaƙe da kalar zance. Uncle Tasi'u kam da abin duniya ya ishe shi sai dai kaga yayi zugum abinda dariya abin tausayi.

Daga sallar magriba suka baro gidan. Kai tsaye gidansu suka nufa duba Mammah. Sai dai sun samu gidan har a lokacin cike yake da mutane. Bama su san inda zasu gano Mammah ɗin ba. Amma fa securitys ba'a magana. Dan harda na farin kaya da su kansu su Mammah basu ma san dasu ba a kwai su a gidan nan har gidan Daddy Imran. Hatta su Bilal a masaukinsu akwai jami'an tsaro basu sani bane. Dan su Dada basu bari anyi taron bikin nan ba sai da suka shirya. Dole suka haƙura da batun ganin Mammah dan bata ganuwa. Dada ya koma UNIT ZERO dama su Faro jiransa suke. Su kuma suka nufi masaukinsu inda suma abokansu ke jiransu harda su Ja'afar ɗin. Sai dai har cikin rai Bilal da Ammar suna son ganin amaren su ko yaya. Amma lamari yaƙi saita waya. Har mamakin Dada suke da jinjina ƙoƙarin sa shi da Yaya Haydar, har gulmarsu sun sha yi ma....

Abinda basu sani ba su sun fisu iya kamewa ne saboda girma. Musamman ma Dada da baka iya gane ainahinsa ba. Dan ko Imran yana matuƙar jinjinama dauriya irin ta Zak-Shadow ɗin nasa. Babu yanda za'ace Dadan baya cikin buƙata. Shekaru kusan tara ba wasa ba ne. Balle ma su maza ba komai ke iya dakushe wannan yanayin a garesu ba cikin sauƙi. Garama mata wata ko cikin damuwa take zakaga komai ya fita kanta. Duk wanda ya kalla Dada yasan mutum ne mai cikakkaiyar lafiya kodan yanda yake gudanar da komai nashi cikin zafin nama da jarumta. Sai dai nutsuwarsa da kamewa ke ɓoye ainahinsa har takai bai san yabi hanyar saɓama UBANGIJI domin kwaranye ƙishinsa ba. Ya san dai komai lokaci ne, sannan jarabawa ce. Ko Nabeeha na bashi tausayi, amma yana buƙatar ganin ta dawo hankalinta kafin shi da ita su fuskanci juna. Zai iya barinta da ƴan uwansa suyitayi matsalarsu ce. Amma dole ta koya girmama masa mahaifiyarsa. Dan duk duniya baida kwatankwacin ta koda a misali ne. Duk yanda yasan halayen mahaifiyarta marasa ƙyau koda wasa bai taɓa mata kallon banza ba balle yin maganarta da wani, ita miyasa bazata gane tashi uwar ba abar wasanta bace. Koma dai miye ai yanzu ya shirya mata kuwa. Jira yake kawai a kammala bikin nan su koma muhalli guda ɗaya...

°•••°•••°•••°•••°

Yau data kama Lahadi shagali biyu ne zai gudana. Walima da rana, dinnar da daddare. Dan haka tunda fa gari ya waye duk da gajiyar da aka yini a ciki haka aka sake dasa wata hidimar. Amare dama an yanke sai gobe idan ALLAH ya kaimu kowacce za'a miƙata ɗakinta. Dan haka su Biebah suka samu damar yin barci sosai. Basu tashi ba sai kusan sha biyu. A taron walima ba wata kwalliya za'ai musu ba, dan

haka da kansu sukai kwalliya da shirinsu cikin atamfofi. Sannan aka kawo musu alƙyabbu masu shegen ƙyau da tsada suka saka.

Ba ƙaramin ƙyau sukai ba kuwa. Dan zaka iya cewa ma sun shafi gidan sarauta ne. Lailah tazo tai musu turaren SHUWA INCENSE AND MORE +234 704 229 3387. A lokacin itama Shariffa ke shigowa da wani abu a babban kofi sai ƙananun kofuna uku. Zubawa tai ta bama kowannensu. Magananannu biyu suka tsaya kallo batare da sun sha ba.

Received at 14:59

[4/10, 11:15 PM] null: Lailah dake kallonsu ta ce, "Ninah da Ruƙayya wai mi kuke jira ne?."

Kamar Nimrah zatai kuka ta ce. "Mamy wlhy abun nan fa akwai matsala. Jiya ciwon ciki ya sakani da daddare. Hakama Ruky yau da asuba taita ciwon ciki ko?". Tai maganar ƙarshe tana kallon Ruƙayya. Kai ta jinjina itama. Sai kuma ta ce, "Mamy wai minene?".

Shariffa ta hararesu da faɗin, "Ƙaniyarku ce. Dalla kusha ku bani. Ba ciwon ciki ba ciwon ƙashi yake saka ku ƙarewa".

Lailah dai dariya take ƙunshewa. Hakama Aunty Mimi dake bakin ƙofa tsaye. Dan ta fahimci shiririritar yaran nan baisa sun gane mike damunsu ba. Amma tunda sun ce ciwon ciki kawai a barshi a hakan. Ganin suna ƙus-ƙus Shariffa ta fahimci zasu iya zubarwa. Dan haka tazo gabansu ta tsaya tace su sha a gabanta. Aiko a gaban nata suka sha kamar zasuyi kuka. Sai suka bama Biebah tausayi. Dan ita kanta da take babban abubuwan nan da ake basu sun dameta bare su....

Ana idar da sallar azhar aka fara kwasar mutane zuwa wajen walimar. Amare kam sai wajen biyu saura ma. Dan tare aka zo ɗaukar su tare da Mammah. Bilal zai jasu, dan haka Ammar ya maƙale a kusa da shi. Aiko tunda suka fito ƙamshin su ya buɗaɗe compound ɗin. Ji Ammar yay kamar yaje ya rungume Ruƙayya, ya dai daure ya cije da ƙyar. Mammah na lure da shi, ta girgiza kai kawai. Shima Bilal sai ya zungureshi yana nuna masa Mammah ɗin. Ammar ya ɗan waro idanu yana shafa ƙeya. Bilal ya kauda kai yana dariya ciki-ciki. Tun daga nan Ammar ya kama kanshi. Amma harga ALLAH daga shi har Bilal ɗin kamshin turaren su Ruƙayyan ɗaga musu hankali yake.

Sai da suka fara tafiya su Nimrah suka gaishe su. Bilal dake kallonsu ta mirrorn gaba ya ce, "Wai ya naga duk kunyi laushi ne? Mammah yaranki ko basu da lafiya ne?".

Ƙaramar dariya Mammah tayi, yayinda Nimrah da Ruky suka ƙara lafewa jikinta. Sai Biebah ce ta ce, "Yaya bazaka gane ba".

"Ganar da ni Auta. Dan ke gani nai ma kin rame min a ido fiye da su".

Hawaye suka zubo mata. Sai kawai Ammar ya hau dariya da faɗin, "Wai kuka kike?".

Kanta ta sake duƙarwa, da lafiya-lafiya ne sai ta rama. Dan shi da Aunty Mimi sam bata raga musu kasancewar su sakonta. Bilal bai ƙara magana ba, sai idanunsa da suka kaɗe. Shi kansa Ammar ɗin dauriya ce kawai amma har ya fara jin kewarta tunma da aka fara bikin nan. Motar tai shiru dan suma su Nimrah sun koma jikin Biebah suna hawayen ne. A haka suka iso wajen.........✍

Kuyi hakuri da jina shiru jiya. Rasuwa akai mana😭

[4/10, 11:15 PM] null: 46

........Sosai wajen yayi ƙyau, komai kuma a nutse a tsare. Ɓangaren mata daban na maza daban. Kasancewar itama Asma'u sun iso aka dawo da ita wajen su Biebah. A motar aka barsu Mammah ta shige. Sun kai kusan mintina goma sannan Aunty Mommy tazo tafiya da su. Wajen yayi tsitt kamar yanda aka buƙaci shirun domin fara

addu'a. Dan haka hankalin kowa ya dawo kan amare da suka shigo. Sai dai fuskokinsu rufe da hular alƙyabba su duka huɗun, Dada yaji daɗin yanda akai musu shigar mutunci kuwa. Har wajen da aka tanada domin su akai kaisu. Kujeru huɗu daga gefe ta ɓangaren mata.

Dai-dai lokacin kuma ake isar da batun zuwan shugaban ƙasa da kansa ba saƙo ba. Tare da iyalansa gaba ɗaya. Mutane sun ƙara tabbatar da lallai akwai alaƙa mai ƙarfi tsakanin su Dada da Shugaban ƙasa a yau, dan haka ƙus-ƙus ya fara tashi a wajen har sai da aka buƙaci shiru. Sosai tsaro ya ƙaru a wajen, bayan sun zauna akai addu'a sannan Imam ya fito yay karatun Alkur'ani. Sosai zukata suka ƙara nutsuwa, kafin a fara gudanar da wa'azi daga bakin manyan malamai musulinci daya sake sanyaya jikin mutane. Ya kuma saka amare ƙara shiga hankalinsu dan kai tsaye akan rayuwar aure a musulinci taken lectures ɗin suka gudana. Lokacin sallar la'asar yay aka dakata. Sai da aka yo salla aka ɗora wata sabuwar lecture ɗin kuma dai, zuwa 5 akai addu'a aka fara liyafar cin abinci kuma.

Alhamdullahi komai ya gudana cikin nutsuwa da dattako. Dan sosai manyan mutane sun halarci wannan walima. Gashi an nuna a gidajen tv live. Banda masu posting a wayoyi kuma. Sai dai a karo na farko hotunan su Nimrah sun fita. In da mutane suketa ka-ce-na-ce akan wai Zak-Shadow ya auri yarinya ƙarama. Mata suka fara faɗin matarsa tai masa halaccin jiransa shekara takwas ya dawo ya saka mata da kishiya. Mutane basu san gaskiyar magana ba amma sun iya tsara zance da girmamashi. Ga batun zuwan shugaban ƙasa wajen shima sunata yan-yan, akai. Oho shi wanda suke yi dan shi ɗin ma babu alamar yana da lokacin su.....

Ana dawowa gida sallar magriba akayi aka kuma fara shirin dinner. Ana idar da isha'i aka fara wucewa da mutane nan ma. Yayinda amare ke can ana tsara musu ado da kwalliya na amaren girma. Kai daga gani kasan fitar ta musamman ce. Babu wanda ya saka ran zuwan Dada wajen nan da Faro. Dan haka ma akace ayi angunan bogi. Wai Ma'aruff ya zauna tare da Biebah. Nimrah kuma Ja'afar.

Mammah naji ta ce, “Babu ruwanta su da Muhammad, gara su fara kiransa su sanar masa idan ya amince to. Aiko sunata darurar kiran nasa suka dai daure. Sai da wayar ta kusa tsinkewa ya ɗaga. A lokacin fitowarsa a wanka kenan ma. Cikin kame-kame da in inar rashin dalili Ma'aruff ya sanar masa. Yay shiru kamar bazai amsa ba. Hakan yasa Ma'aruff fahimtar sun taro match. Amma ya daure dai bai kashe wayar ba.

Dada yay gyaran murya, sannan ya furta, “Ku kun zama manyan banza kenan ko Ma'aruff? Kunsa Mammah ta takura na barku kuyi shine kuma zaku sake kawo wani abun..”

“Dada kayi haƙuri mun tuba. Kawai mun san ko munce kazo bazaka zo bane. Kuma Yaya Haydar ma idan baka zo ba shima nasan bazai zo ba......”

“Shi ke nan su Bilal ɗin basai suyi ba ya wadatar”. Dada ya faɗa cikin katse shi, yana gama faɗa kuma ya yanke wayarsa.

Ja'afar ya ce, “Hummm dama bana faɗa maka ba Twiny, Dada fa wlhy kishin tsiya ne da shi. Da zakuji ta tawa suma su Bilal su haƙura. Amaren kawai su zauna ba dole sai da anguna ba. Idan ba hakaba kaɗan daga aikinsa yace kada ma aje da Ninah wajen”.

“Wlhy Dada daya gama damu”.

Cewar Bilal kamar zai kuka. Dariya su Ja'afar ɗin suka sanya kuwa. Ma'aruff ya ce, “To inaga kawai abi shawarar Twiny ALLAH. Dama da yaya ya amince ayi dinnar ɗin nan. Kada mu ƙureshi kuma kun san dai Dada ƙaniyarmu zamu ci a ƙarshe”.

Hakan yafi basu masalaha, dan haka duk suka amince. Suka kira su Aunty Ummi suka sanar mata. Itama ta gamsu, dan wlhy tasan badan Mammah ta saka baki ba ma bazai bari ba. Daga haka aka kwashi amare zuwa wajen dinner daya gama cika ya tumbatsa. Ga uban tsaro har ba'a magana.

Received at 14:59Reactions:

[4/10, 11:16 PM] null: Yanda aka tsara amaren ma kawai babu angwaye sai ya kawo wani sabon salo daya burge mutane. Gashi sun sha ƙyau har sun gaji. Gaba ɗayansu material ne a jikinsu dogayen riguna, sai dai kowacce da kalar nata da kuma irin ɗinkin da take so.

Kasancewar an tsara wajen da iya adadin mutanen da ake buƙata komai a nutse. Bayan addu'a ƙawayen su Nimrah da suka shirya kalolin rawa suka fara gudanar data farko tare da su Mu'azz. Ba ƙaramin ƙayatarwa abin yayi ba. Sai kuma mawaƙan da sukai waƙoƙin biki suma suka fara baje kolinsu. Sannan ƙawayen Asma'u suka gudanar da tasu rawar. Su dai na Biebah sun ɗauki girma. Su Feddo sun sake yin rawa ta biyu, kafin ai taƙarshe harda amare. Sosai abin ya ƙayatar da jama'a. Su Uncle Ja'afar sai liƙe yaransu suke da kuɗi. Bilal yana fakar ido ya rungume Ma'u, Ammar na ƙyalla ido ya gani yace, “Wlhy nima bazaka barni a baya ba. Haba ai nayi haƙuri jama'a”. Shima ya kama Rukyn sa ya kanainaye. Mi su Lailah zasuyi ba dariya ba. Sai da Ma'aruff yay musu ƙulli a baya kowa ɗai-ɗai suka sake su. Nimrah nama Ruky dariya da shaƙiyanci ita ko ba baki. Dan gaba ɗaya jikinta yayi sanyi tun lectures ɗin ɗazun. Ita kanta Nimrah ɗin ƙarfin hali ne kawai. Asma'u kam ai bama a magana, kodan ita da Biebah zasu bar gida ne zuwa wasu gidajen. Garama Asma'u gida za'a kaita dan bayan gidan Baffa basu da wani gida abin alfahari sama da gidan Mammah.

Sosai dinner ta ƙayatar itama sai sambarka. Kamar yanda Dada ya saka doka ƙarfe sha biyu a aka tashi. Dan sha biyun ma na cika sai ga kiransa a wayar Aunty Mommy. Cikin rikicewa ta ce, “Dada ALLAH mun tashi, dan yanzu haka ma su Yaya Ma'aruff sun wuce da su Ninah gida. Muma muna ƙarasa sallamar baƙi ne kawai. Ajiyar zuciya ya sauke yana ajiye wayar. Faro da Imran suka kallesa sukai murmushi. Dama tun ɗazun sai ƙananun tsaki yake musu....

___

Sai muce Alhamdullah biki kam ya kammala. Dan washe gari aka karasa zuwa gidan Biebah aka ƙarasa komai. Dada yace duk mai zuwa yaje yaga ɗaki dan shi da Imran zasu kai Biebah ɗakinta. Wannan ba sabon abu bane. Dan tun daga kan Aunty Ummi, Mommy, Mimi shi da kansa ya kaisu ɗakunansu tare da Imran. Sai suma su Ja'afar dake yin mota ɗaya subi bayansu. Kuma anayi la'asar suke tafiya.

Iyaye da yayye sun zagaye Biebah da aka gama shiryawa. Aka fara kaita gaban Uncle Nasiru da Uncle Jamilu, Zubairu, Tasi'u sukai mata nasiha. Sannan aka kaita ga Mammah. Addu'a kawai tai mata dan ita kam duk wani faɗa da nasiha tama yaranta shi. Suma su Gwaggo Khadijah sukai nasu. Sannan aka ƙarasa da ita gaban Dada da Imran, sai su Ja'afar dake tare da su har zuwa Ammar ƙarami.

Sosai idanun Dada sun juye. Duk lokacin da zai kai ƙannen nan nasa gidan aure kobai fito ya faɗa ba kallo ɗaya zaka fahimci damuwa a tare da shi. Yanzu ma koda Biebah ke durƙushe a gabansu ya zuba mata idanu ne kawai. Sai kuma ya kai hannu ya kamo nata. Hakan yasa ta matso jikinsa sosai ta ɗora kanta a ƙafarsa. Kanta ya shafa a hankali yana murmushin ƙarfin hali. “ALLAH yay miki albarka. Yanda kikai mana biyayya kema UBANGIJI ya baki yara masu albarka da zasuyi miki. ALLAH ya zaunar dake gidanki lafiya kamar sauran ƴan uwanki. Habibah na yarda da mijin da kika zaɓa da kanki ɗari bisa ɗari kamar yanda na yarda dana ƴan uwanki a baya. Kema na yarda da tarbiyyar da muka baki, kije kiyi haƙuri. Shi aure ibada ce. Rayuwa ce ta rabi farin ciki rabi jarabawa. Babu wani bawa da zai iyama ɗan uwansa bawa yanda yake so ɗari bisa ɗari na yau da goben rayuwa. UBANGIJI ne kawai mai wannan ni'imomin a gare mu. Dan haka idan kinga kuskure daga Haydar ki yarda shi ɗin mutum ne kamar ke. Dole yay dai-dai kuma dole yayi kuskure. Ku zauna ku gyara a ɗakin ku basai kin kawo mana ba. Ga ƴan uwanki nan su duka ukun tunda na kaisu gidajen aurensu ban taɓa zama shari'a tsakaninsu da mazajensu ba ko sau ɗaya. Kuma ni shaida ne kin fisu haƙuri. Badan mun gaji dake ba zamu kaiki wani gida, idan

so samu ne naita ganinku a kusa dani ina jin daɗi da farin ciki, amma hakan bazai yiwu ba, wannan shine gatan da zamuyi muku muma muyima kammu.
Received at 14:59
[4/10, 11:16 PM] null: Kar ai sakaci da ibada, yanzu ne ma lokacin da za'a ƙara dagewa kinji".

Kanta ta jinjina masa tana sake fashewa da kuka. Ya kauda kansa gefe yana dauke guntun hawayen da suka taru masa ta gefen ido. Daga nan shima Imran ya sake mata tashi nasihar. Kafin su Ma'aruff, Ja'afar, Bilal, Ammar. Daga haka akai addu'a sannan Dada ya miƙe riƙe da hannunta. ALLAH sarki Small Mom, da gudu su Nimrah da Mu'azz sukazo suka rungumeta, dama suna ɗaki sun haɗe kai sunata kuka. Bintu taje ta kirasu yanzu. Idanu kawai Dada ya zuba musu yama kasa magana. Sai Daddy Imran ne ke lallashinsu. Dan su Ja'afar ma sharar ƙwalla suke. Wato kowane ɗan uwa fa a irin wannan ranar yakan ji wannan damuwar ta rabuwa da ƴar uwarsa. Musamman wannan zuri'ar da suka shaƙu suke matuƙar son junansu. Ƙarshe dai da ƙyar Mammah tazo ta janye su Ruƙayya tai ɗakinta da su. Su kuma suka fice Biebah na jikin Dada...

//★//★//★//★//

Ashe wasa farin girki. Sai da suka kai Biebah gidanta daya gama haɗuwa Dada ya kama hannun Faro ya saka na Biebah a ciki. Ya jaddada masa amana ya bashi, idan kuma yaci wlhy bazai taɓa yafe masa ba. Ya tabbatar masa a cikin kaf ƙannensa Biebah itace zuciyarsa. Kar ya bari ya taro faɗan da bazai iya karewa ba.

Faro yay murmurshi da tabbatar masa zai kamanta in sha ALLAHU. Dan shima Biebah ƙanwace a garesa ai. Shima Imran ya sake jaddada tashi amanar. Su dai su Ja'afar sun barma zuciya saboda matsayin Haydar yaya. Amma yasan kosu kaɗai sun ishe shi gayya idan ya taɓa Biebalo. Zasu tafi fa Biebah ta riƙe Dada tanata kuka. Da ƙyar ya ɓanɓareta a jikinsa. Sai suma su Ma'aruff suka rungumeta suna hawaye. Dan Bilal ma kasa tsayawa yayi, kowa yasan yanda Bilal ya shaƙu da Biebah a rayuwa. Kusan shine yay rainonta, shiyyasa komai nata a gidan nan Yaya Bilal ne gaba.

Sosai jikin Haydar ya ƙara sanyi, dan soyayyar waɗan nan ƴan uwa bata wasa bace....

_____

Daga gidan Faro gidan Daddy Imran suka wuce. Zasu ɗakko Asma'u. Sun tadda itama iyaye da yayye zagaye da ita abata nasiha da faɗa. Bayan sun gama aka kawota nan falon Imran gaban Dada matsayin uba. Yanda yay ma Biebah nasiha haka yay ma Asma'u, shima Imran ya ƙara dan daga shi har Ammie sunyi kafin biki ba sau ɗaya ba ba sau biyu ba. Itama dai ta rungume Daddy Imran da ƙyar aka rabasu. Haka Dada ya ɗakkota a mota da su Ja'afar dan Bilal da Ammar sun wuce gida daga gidan Biebah. Lokacin da suka iso ana magriba. Dada na damƙata a hannun Mammah ya wuce massalaci.

Anan ɗakin Mammah tai sallar magrib da isha'i, a lokacin kuma suma Ruƙayya da Nimrah an kammala shiryasu tsaff. Ga turaruka sun sha na SHUWA INCENSE AND MORE +234 704 229 3387. Ana idar da sallar magriba Mammah tama su Gwaggo Alawiyya maganar su rakasu basai sun kawosu wajenta ba. Dan ta tabbatar baza'a rabu lafiya ba. Haka kuwa kayi. Wasu suka raka Asma'u sashenta. Wasu Ruƙayya, wasu Nimrah..........✍
Received
[4/10, 11:17 PM] null: 47

........."Kana nufin lokacin da zaka bayyana kanka ga Zak-Shadow yayi kenan?".

“Tabbas yayi, kuma ya kamata ace nayi hakan saboda wannan shine dai-dai lokacin daya dace. Abinda ya sakani jinkirtawa ya riga yaje hannunsa. Matarsa ita ce babban MAKAMIN da mutanen nan suke riƙe da shi a kasa ta kowanne ɓangare....”

“Hummm kana ganin dan ta koma hannunsa zai iya tsira? Ka sani na sani mutanen nan nada ƙarfi matuƙa. Dan sun binne mutanen kirki da yawa irin Zak-Shadow a ƙasar nan dama wanda suka fishi gwagwarmaya. Shi kansa UBANGIJI ne bai kawo ƙarshensa ba a hannunsu shiyyasa suka kasa kaisa ƙasa badan yafi ƙarfinsu ba”.

“Nasan da haka sosai Sir, kamar yanda kace UBANGIJI kuma ai magana ta ƙare. Abinda nake so ka fahimta bana fatan su sami nasarar kai masa hari ta hannun AMANARSA. Dan ita ɗin amanarsa ce......”

“ƘALUBALENSA kuma a yanzu ba”..

Mutumin ya faɗa cikin katseshi da takaici da damuwa”.

“Bazan yi musu da kai akan ita ɗin ƘALUBALENSA bace Sir, dan inada tabbacin a yanzu babu wani tarko mai haɗari a cikin rayuwar Boss sama da ita. Shiyyasa nima na shirya dawowa cikin duniyarsa, kuma nayi alƙawarin bada rayuwata wajen tayashi wannan yaƙin.”

“Mu ma muna tare da kai a cikin yaƙin, dan Haysam ya cancanci fiye da hakan a garemu. Yanzu miye mataki na gaba?”.

“Zan cire fuskar bogi, sannan zan fito na daina laɓewa a baya.”

“Sai nake ganin kamar ka ƙara jinkirtawa da bayyana masa fuskarka, ka dai cigaba da bashi bayanan sirri kamar yanda ka fara. Dan in mutanen nan suka gane kana raye da wahala rayuwarmu tayi tsaho”.

Murmushi yayi mai ma'anoni da yawa. Kafin ya jinjina kansa da faɗin, “Haka ne Sir. Amma karka manta ai mun jima da mutuwa a duniyar mutane. Har mi kake tsoro a wannan gaɓar? Kai ɗin fa SOJA ne, sojan ma rainon ZAK-SHADOW”.

Ajiyar zuciya ya sauke mai ƙarfi. Ya ce, “Haka ne na fahimta. Yanzu sai muje next kenan? Amma kafin hakan ya kamata mu nema shawarar Baba”.

“Wannan shine dai-dai. Amma kafin hakan zan fara aika masa waɗan nan bayanan. Sai ka turama Baban saƙo ALLAH yasa ya bamu damar ganinsa da wuri..”

Jinjina masa kai yayi. Daga haka suka sallama ya baro wajen. Dama a wani ɓoyayyen waje suka haɗu, yana cikin shiga ne ya ɓoye ainahin kai shiyyasa baka isa gane waye shi ɗin ba kai tsaye.....

••••••••••••

•••••••••••••

Sosai damuwa ke shimfiɗe a fuskar Faro dake kallon Biebah tun bayan ficewar su Dada. Sai da yaji ƙarar rufe gate alamar sun fita gaba ɗaya sannan ya sauke ajiyar zuciya. Karo na farko ya ɗaura hannuwansa duka biyu a saman kafaɗarta. Sai ta sake duƙar da kai sautin kukanta na ƙara fitowa.

“Kukan nan bai isa haka nan ba Biebah? Nima fa yayanki ne. In sha ALLAHU zan yi ƙoƙarin maye miki gurbin su Haysam, koda ba ɗari bisa ɗari ba zan kamanta kinji”.

Kanta kawai ta iya jinjina masa, shima bai matsawa kansa da sai tayi maganar ba ya sakata a jikinsa kawai ya rungume ta. Abinda tafi buƙata kenan a yanzu, dan haka ta lafe tana shashshekar kuka da jan ajiyar zuciya. Bayanta ya cigaba da shafawa a hankali, har sai da ya tabbatar ta rage nauyin zuciyar tata sannan ya kama hannunta suka zauna a cikin kujera. Mayafin jikinta ya yaye, dan haka ta sake sunkuyar da kanta taki yarda ta kallesa. A karo na farko yay murmurshin da har tana jin fitar sautinsa. Sai kuma ya matso sosai yana leƙen fuskarta data sunkuyar. Yanda yay ɗin ya bata kunya, tai ƙoƙarin kauda kanta gefe ya kamo fuskar cikin hannunsa.

“Na zata kunyar ta ƙare ai kuma ko Habibiya. Kin manta yau a gidan Haydar kike? Amarya mai capacity kenan da Babban yaya da kansa ke kawota gidanta”.

Murmurshi ta saki tare da kife kanta cikin hannunsa dake riƙe da fuskar tata. Shima ya sanya dariya yana matsota sosai jikin nasa ya sake rungumeta. Suna a

haka akai kiran sallar magrib. Badan yaso katsewar yanayin ba ya kamata ya miƙar yana faɗin, “Muje na rakaki ɗaki na je massalaci”.
Received at 14:59
[4/10, 11:17 PM] null: Babu musu ta miƙe, haka suka nufi inda bedrooms ɗin suke. Ya tsaya a farkon corridor ɗin yana kallonta. Cikin magana ƙasa-ƙasa ya ce, “Ina zan kai amarya?”.

Kanta a ƙasa ta ce, “Koma ina”.

Fuskar sa da murmurshi har yanzu ya ce, “Shike nan bari na kaiki ɗakina, dan yau baƙuwata ce ke”.

Batace komai ba, shima bai sake magana ba ya kama hannunta suka nufi ƙofar dake can ciki a ƙarshen corridor ɗin. Ɗaki ne babba, an zuba masa kaya masu ƙyau, babu kuma tarkace a cikinsa sam. Ga ƙamshi da tsafta alamar yana samun gyara da kulawa. A kaikaice ta ƙare masa kallo, ya zaunar da ita a bakin gadon ya nufi bayi batare da yayi magana ba. Babu jimawa ya fito jikinsa da ruwa alamar yayi alwala.

“Naje massalaci”.

Ya faɗa yana nufar ƙofa. Ta amsa masa da “A dawo lafiya”.

★Bayan fitarsa itama alwalar ta tashi tayo. Ta gabatar da salla. Koda ta idar bata tashi a wajen ba ta zauna zugum cike da damuwa da kewar gida. Musamman ma su Ruƙayya da a koda yaushe suna nane da ita. Sai Mammah uwa abar alfaharin kowane ɗan halak. Hawaye ne suka cika mata idon, bata bari sun zubo ba ta maida su ta haɗiye. Karatun Alkur'ani ta fara dan ɗebema kanta kewa har aka kira sallar isha'i. Tashi tai ta gabatar, tayi har shafa'i da wutri. Bayan ta idar tana zaune tana addu'a ya shigo. Kyakkyawan basket ɗin hannunsa ya ajiye a gefenta shima ya nema waje ya zauna a ɗaya daga kujerun ɗakin. Tai addu'a ta juyo tana masa sannu.

“Yauwa Baby. Ga abinci nan Hajiya ta aiko”.

Kanta a ƙasa ta ce, “ALLAH ya saka da alkairi”. Sai kuma ta miƙe ta ɗauki Basket ɗin zuwa inda yake. Kallon da yake mata ya sakata kasa kallonsa, murya a ƙurya ta ce, “Ina kitchen yake?”.

“Ke da gidanki kike tambayar kitchen? To na hutar dake zauna mi kike buƙata na ɗauka miki? Dan yau ke baƙuwata ce”.

Murmushi tayi, shima ya miƙe yana nasa murmushin ya fita. Babu jimawa ya dawo da plates da cups, sai spoons. Ta zamo daga kujerar da take zaune ta buɗe abincin ta zuba masa komai. Zata miƙe ya riƙota, kusa da shi ya zaunar da ita har jikinta na gogar nasa. Abincin daya ɗiba ya kai bakinta. Zata fara nuƙu-nuƙu ya ce, “Ɗura kike so kenan?”.

Kanta ta girgiza masa, cike da kunya ta fara amsa. Idan yaci sai ya bata a haka suka cinye abincin da gasashen naman. Ta fara gyara wajen yana tayata. Sun fito tare har kitchen ɗin da yay mata matuƙar ƙyau, dan har sai da ta tsaya tana kallo. Sai kawai jitai an ɗauketa gaba ɗayanta. Babu shiri ta kama dariya da roƙon ya sauke ta amma yaƙi sai da ya kaita har bedroom ɗinsa, a bedroom ɗin ma a cikin bathroom. Sabon brush ya buɗe mata ya saka marclen a jiki ya bata. Ita dai a kunyace ta amsa. Koda suka kammala sai yace suyi alwala...

Sun gabatar da sallolon nafila, yay musu addu'a sosai tare da dafa kanta. Sannan ya ɗora da nasiha, tare da sake maimaita mata abinda yake saurin saka shi a fushi da wanda ke saka shi a farin ciki. Itama yace ta sanar masa. Kasa magana tai, sai bai matsa mata ba ya barta. Shi ya fara miƙewa ya sake shiga bayi. Tana nan zaune kusan mintina talatin sai gashi ya fito ɗaure da towel. Da sauri ta duƙar da kanta, shi kuma dan neman magana yazo har inda take ya kamata ya miƙar. Duk yanda yaso ta kalleshi taƙi kallonsa. Sai ma jikinta dake neman fara rawa. Sai yay murmurshi kawai, cikin raɗa ya furta, “Baby sarkin kunya. Yanzu fa miji nake ba Yaya Haydar ba”.

Ita dai batace komai ba, sai ma sake duƙe kanta da tai. Ya sake murmusawa da faɗin, "Tunda bakin ya mutu shike nan. Jeki kiyi wanka to kizo ki kwanta ki huce wannan gajiyar bikin da kuka kwasarma kanku".

Koda ta jinjina masa kai sai ta nufi hanyar fita. Riƙota yay. "Haba Biebalo ina zuwa kuma? Ga bathroom anan. Har kayan barci kina da su anan ɗakin, kin san duk inda Haydar yake kema kina a wajen".

[4/10, 11:17 PM] null: "Yaya zanje can nidai".

"Bazan ce a'a ba. Amma idan muka je can ɗin nine da kaina zan miki wankan kin yarda?".

Karo na farko ta ɗago a rikice tana kallonsa. Sai dai tama kasa furta abinda ke bakinta. Shi kuma ya fuske ya tsareta da idanunsa da ke a juye. Har sai da taji kallon na sake tsumata da ratsa mata jiki sannan tai saurin barin wajen ta nufi bathroom ɗin nashi kamar yanda ya buƙata tun farko. Sai dai babu abinda zuciyarta keyi sai dukan tara-tara, dan tunda take da shi bata taɓa ganin kalar abinda ya gani a cikin idanunsa ba yanzu........✍

Hy Guys. Barkanmu da sake dawowa filin daga. Barkan ku da salla kuma. Fatan anyi ibada lafiya. UBANGIJI ALLAH ya karɓa mana tare da amsa addu'oin mu baki ɗaya. Ya Rabbi kasa muna cikin bayin da aka ƴanta a cikin wannan wata mai alfarma. UBANGIJI ka gafartama iyayenmu da al'ummar Musulmi da suke kwance cikin ƙasa. ALLAH kayi mana maganin dukkan matsalolinmu na zahiri da baɗini.❤❤😘

[4/10, 11:18 PM] null: 48

.........."Yaufa bazaka kwanar mana a gidan nan ba Zak.."

Shiru kamar Dada baiji mi Daddy Imran yace ba. Idanunsa akan screen ɗin laptop yana aiki hankali kwance. Sarai Daddy Imran yasan ya jishi. Zancen ne baya son ayi kuma bazai barshi ba, yau zaiga ƙarshen miskilanci.

"Haysam!".

Ya kira shi da sunan daya kan jima bai kirasa da shi ba. Dan haka Dadan ya ɗago idanunsa a karo na farko ya kallesa. Imran ya harare shi.

"Kana jina kenan?".

Dada yay murmurshi yana kauda idanun nasa daga kallonsa. Cikin sake basarwa ya ce, "Kazo mu ƙarasa aikin nan, kasan fa gobe akwai office bamu da isasshen lokaci. Dan ba lallai ka ganni a gidan nan ba ma".

"Babu wani aiki da zamu cigaba da yi gida zaka wuce. Bamma san miya dawo da kai ba yanzu..."

"Miyasa kake da rigima ne wai?".

Cewar Dada yana sake maida idanunsa akan screen ɗin laptop ɗin.

Imran ya ce, "Hummm har na kai ka rigima ne. Ni yanzu ma duk ba wannan ba. Canai ka tashi muje na rakaka. Ni ban taɓa ganin ango irinka ba wlhy. Kana ganin Haydar yau ko sau ɗaya bamu ga ƙeyarsa a gidan nan ba".

Dada ya ɗan murmusa kawai baice komai ba. Shima Imran sai ya miƙe yazo ya ɗauke laptop ɗin jikinsa gaba ɗaya...

Dada ya ce, "Kana lafiya kuwa?".

"A'a da sauƙi dai. Koka tashi ko na kira Mammah a waya".

"Ni ne zaka kirama Mammah?".

"Da gudu ma kuwa. Kana nufin zan barka ka barmin yarinya ita ɗaya tana amarya a daren ta na farko gidanka? Nima zuwa zan yau na sabunta nawa angwancin dan baza'ayi babu ni ba".

Dariya ta kusa kama Dada akan furucin ƙarshe na Daddy Imran. Amma baiyi ba sai dai fuskarsa ta nuna alamar murmurshi. Bai sake tankawa ba ya miƙe kawai dan yasan nacin Imran bazai taɓa barinsa yasha iska ba. Wayoyinsa kawai ya ɗiba yay

hanyar fita. Imran dake kashe laptop ɗin yay murmurshi shima ya tattare komai waje ɗaya yabi bayansa....

★Sun iso anguwar ana shirin sallar isha'i. Dan haka suka shiga massalaci kawai. Bayan an idar da sallar Imran yace shi bazai shiga ciki ba zai wuce gida kawai. Dada baice komai ba ya bashi hannu sukai musabaha. Ya shiga mota shi kuma ya shiga gida.

Maimakon sashensa sashen Mammah ya nufa. Falon cike yake da baƙin Kano dana Bauchi da Maiduguri. Duk da kuma kasancewar ba yara ne kawai ba harda manya sai da kwarjininsa yasa sukai tsitt, yaran duk suka sake nutsuwa suna masa sannu da zuwa da gaishe shi. A taƙaice ya amsa a jimlace. Sannan ya gaida suma manyan a jimlacen. Sun amsa masa tare da addu'ar zaman lafiya nahar abadan ga duk ɗinsu ma'auratan.

Sun san bamai yawan magana bane, dan haka basu damu da amsawar tasa a taƙaice ba. Daga haka ma ya wuce ɗakin Mammah dan tunda har bai ganta anan ba yasan tana ɗakinta. A can kuwa ya sameta ita da Aunty Mimi tana shafa mata man zafi a ƙafafu. Ya zauna kusa da ita yana amsa sannun da Mimin ke masa idanunsa akan ƙafafun Mammah ɗin.

"Suna ciwo ne ƙafan?".

Murmushi Mammah tayi da amsa masa da, "A'a gajiyar kai-kawo ce kawai Muhammad. Yanzu nake tunanin kiranka ashe kana kusa?".

"Mammah ta samu ke nan?".

Mammah tai dariya da faɗin, "A'a, yadai kamata kazo kama su Bilal nasiha duk da nasan kullum cikin yi kake".

Murmurshi ya ɗanyi bai ce komai ba. Dai-dai nan kuma sai ga sallamar su Ja'afar ma.....

....★★★....

Cikin matsananciyar kunya Biebah ta fito a bayin duk da rigar wanka data saka a jikinta ta rufa da towel ɗinsa kuma babba. Faro dake zaune bakin gado yana waya ya ɗago idanunsa yana kallonta. Shi sai ma ta bashi dariya. Amma dai ya danne baiyi ba. Ya cigaba da wayarsa duk hankalinsa na kanta. Sai dai ganin bata da niyyar baro inda take tsaye ta sashi miƙewar shi yana bama abokin wayar tashi amsar zancen daya gama yi masa.

A gabanta ya tsaya, kai tsaye kuma ya kai hannu ya yaye towel ɗin gaba ɗaya. Sai kawai ta runtse idanunta dan bazata iya hanashi ba ko yin musu. Bai ce da ita komai ba shima ya jefa towel ɗin kan kujerar mirror sannan ya sake juyowa inda take. Fuskarta da idanun ke rufe ya kalla.
Received at 14:59
reacted with ❤
[4/10, 11:18 PM] null: Cike da rashin kunya irin ta soja ya kai hannu saman igiyar rigar wankan data ma ɗaurin zarge kawai ya jashi ya warware. A take rigar ta buɗe jikinta ya bayyana. Dai-dai kuma lokacin yake ƙoƙarin yin magana da wanda suke wayar kawai yawu ya sarƙesa ya fara tari. Yayinda ita kuma ta zabura jikinta na rawa ta juya masa baya wata kalar matsananciyar kunya da bata taɓa ji a rayuwarta ba na mata bargo a illahirin jikinta..

Faro ya yanke wayar ƙirjinsa na bugawa da sauri-sauri. Ai baima san ya je gab da ita ya rungumeta ta baya ba dan ji yay shima jikin nashi na rawa tsabar yanda yaji wani al'amari mai matuƙar girma ya tsarga tun daga saman kansa zuwa yatsar ƙafarsa. Har ji yake ƙafafunsa na neman kasa ɗaukar nauyin gangar jikinsa. Kallon nan ɗaya tak da yayma Biebah a ainahin Biebah ɗinta ya kwance masa dukkan lissafin sa, dan bai taɓa tunanin yarinyar takai har haka ba, koma yace ta zarce inda yake zato da tsammanin ta. Tunda yasan Biebah a shekarunta na hankali da hijjab ya santa. A hotunan bikin nan ne kawai ya fara ganinta ba hijjab..

Biebah kam da gaba ɗaya ke jinta kamar ta fashe da kuka dan tsoro da kunya neman zamewa a jikin nasa take. Amma ya hanata dukkan dama sai ma kamata da yay ya sake juyota suna facing juna. Bazata iya tsayawa ya cigaba da kallonta a haka ba, duk da tuni ta kama rigar ta sake haɗewa waje guda ta rufe jikin nata. Sai dai bata ɗaure igiyar ba a yanzu. Bata da mafitar data wuce neman wajen ɓuya, musamman daya sake ɗora hannunsa akan nata hannun dake runtse da rigar zai buɗe. Jikin nata na tsuma kawai ta shige nashi jikin ta ƙanƙamesa...

Murmurshi ya saki, sai kuma ya maida fuskarsa kan wuyanta shima yana mata zobe da hannunsa ɗaya kawai ya fara bata sumba a wuyan. Rawar da jikinta take yanzu kam ta wuce ta farko. Dan bata ma san ta saki rigar ta koma ƙoƙarin riƙe hannunsa dake yawo a gadon bayanta ba. Da wannan damar Faro ya samu ya saluɓe rigar gaba ɗayanta ta sauka ƙasa. Zatai magana ya haɗe lips ɗinsu waje guda kawai tare da ɗagata cak daga kan ƙasa ya nufi karagar mulkinsa da ita.......

★∆∆∆∆∆∆∆∆∆★

Anan ɓangaren su Mole kuwa basu san wainar da ake toyawa ba, saboda Dagger dake fama da jiyyar ƙafarsa data sha harbi. Sai yau ne kwatsam kiran Sanda ya samu Mole. Lokaci-lokaci Mole kan kira Sanda ya zungureshi labarin gidan, amma kwana biyu sai bai jisa ba, gashi har ansha biki, shine kawai Sanda yace bari ya taɓa shi yaji ko lafiya.

Bayan sun gaisa Sanda ke faɗin, “Malam Buba ka ƙi dawowa dai, ga shi har an sha biki, ko har yanzu jikin matar taka ne dai?”.

Da mamaki Mole ya ce, “Biki kuma? Na waye? Kuma a ina?”.

Dariya Sanda yay yana gyara zama an samu na fesawa, dan dama yanda akasha bikin nan tuni neman abokin labari yake da bai gani ba. Dan haka ya gyara zama ya fara zayyana zance daki-daki. Tun kan yakai maganar farko ƙarshe zufa ya wanke jikin Mole tas, cikin rawar bakin da yasa Sanda yay shiru na mamaki Mole ya furta, “Sanda kana nufin yanzu ita Uwa ɗin ta tare a sashen?”.

“Kaifa Malam Buba shiyyasa ban cika son baka labari ba, wani lokacin sai ka dinga yi kamar baka ganewa. Miye kuma wani Uwa. Hajiya Nimrah fa nake faɗa maka Babban Alhajin gidan nan ya aura, ita kuma usainarta Alhaji Ammar. Dan ALLAH idan ana baka labari ka dinga barin mutum na kaiwa ƙarsh....”

Ƙittt Mole ya yanke wayar jin hajijijiya na neman zubar da shi a wajen. Cikin sassarfa ya bar inda yake zaune zuwa cikin gida da Oga Dagger ne kaɗai sai ƴammatansa suke holewa. Ai bai jira izinin shiga ba kamar yanda dokar take, Dagger na falonsa jikinsa ƴammata biyu na masa tausa yana busa wiy-wiy Mole ya faɗo. Cikin takaici Dagger ya dubesa, ya buɗe baki zai danna masa zagi ya riga shi yin magana...

“Oga muna cikin tashin hankali. Matsiyacin nan fa ya tare da Uwa”.

Received at 14:59

4 people reacted with

[4/10, 11:18 PM] null: “Miye Uwa?”.

Dagger ya faɗa yana harararsa.

“Oga ya kake abu kamar baka gane ba. Nimrah nake magana Zak-Shadu yake ko mi yasa an musu biki...”

Tuni Dagger ya wancakalar da ƴammatan biyu gefe yana miƙewa cikin rawar jiki. A gigice ya furta, “Amma dai hauka kake ko Mole?”.

“Oga idan ma ban haukace ba da yanzu kam na haukace wlhy. Shi ke nan rayuwata ta gama lalacewa maƙiyina ya zama mijin ƴata”.

Ji kake tauuu Dagger ya wanka masa mari. Tare da nuna shi da yatsa. “Idan ka sake cewa mijinta wlhy sai na kashe ka kaima”. Ya hanaɗesa gefe yana ɗaukar bindiga dake saman tebirin gabansa ya nufi hanyar fita.........✍

Received at 14:59

4 people reacted